🙆🙆 *RAYUWATA CE*🙆🙆

*Na*

*Khadeejah sani (journalist)*

🌈 *Kainuwa writers association*📝

(United we stand and succeed; our ambition to entertain and motivated the mind of readers)

*Assalamu alaikum inayiwa Allah subhanahu wata,ala godiya daya bani ikon kammala littafina rayuwar gidan kawuna sannan yakara bani damar fara wani sabon bookdin nawa mai suna RAYUWATA CE Allah yabani ikon fadakarwa da nishadan tarwa*

*Allah ya yafemin dukkan wani kuskure dazanyi sannan Allah yabani ladan abinda zanfada Ameen*

*Wanna littafi k`irk`i rarren labari ne banyi shi doncin zarafin wani ba Kuma banyi shi Don muzan ta wani ba na k`irk`iri labari nane Don fada karwa da nisha dan tarwa Allah yabani ikon kamalawa Ameen*

*Sadaukarwane gareki mahaifiyata Allah yaja da ranki Ameen*

🅿 *1-2*

Suya, nakeyi ta awara" akofar gida ga maza sun kewaye ni, sunata hirar su jinai wani daya daga cikin su yace

"Nafisa tund`a zu nake Miki magana Amma kinyi shiru Kuma kina jina". d`ago kaina nayi cikin sanyin murya nace

"Uhm banji bane tanawa za,a baka. murmushi" yayi san nan yace

"Kibani awara ta naira hamsin"

"Kawo kudin"

"Kefa dadina dake y`ar'rainin wayo ce guduwa akace Miki zanyi ne dallah bani naci yunwa nakeji wallahi" kallon shi na karayi nace

"Kaga Musa kasaba yimin haka kawai ka gudumin da kudina. kasan nidai bazan ta binka ba" dallamin harara" yayi sannan yace

"Hmm shiyasa nafiso naje wajen hinde Mai awara wallahi nasiya kawai dandai takin tafi Tata

dadine Amma ita har dakina take bina kuma kije ki tam bayeta wallahi ina bata indai taje shiyasa kema nake fada miki kijecan kikarb`a amma ke kauyanci yayi miki yawa" ya k`arasa fada Yana dallah min, wata hararar.

Banza nayi dashi inaci gaba da sallamar wadanda suka bani kudi. idnn da sabo nasaba da wadan Nan magan ganun awurin yan'iskan unguwar mu. don haka kullum kafin nafita sai innata tayimin fada a kansu karna yarda nabi mutum akan baiba ni kudi ba nabarshi da Allah.

Haka naketa sallamar mutane suna tafiya wasu kuma suna zuwa,
Ana haka Musa da abokan shi suka zauna dan nesa da wurin dana  ke kadan amma ina iya jiyo magan ganun su, na tabbata basu san inajiba wani abokin sane yafara cew
"Nifa wallahi Musa inason wannan yarinyar ina mugun Sha,awarta tunda nafara ganin ta gashi naji kace bakauyiya ce ita bata iya harka ba yaza,ayi kenan don gaskiya na matsu najita ajikina" dariya suka kwashe da ita gabaki da yansu wani aciki yace
"Shege zaki wallahi kamar kasan abinda ke raina nima don haka gaskiya asan abinyi kawai" zakin ne yace
"Kai kasanfa bana son wulakanci nace inason wata sannan kace kanasonta wallahi zan yanka Maka rigar mutunci tam.
Haka daya fadane yasaka su yin tsit Babu Wanda yakarayin magana,

Tashi yayi yamatso kusa dani yace
"Baby sannu da aiki ya garin"
Dago kaina nayi na kalleshi kawai najuya naci gaba da aikina ina haka naji an dafani dasauri na dago nayi tunanin koshine sainaga kawata ce farida don haka na saki fuska muka fara gaisawa da ita.

*My fans inayimuku fatan alkairi dafatan kuna lafiya*

*Agaskiya wannan sabon book din nawa zanfada muku yawan comment yawan typing don agaskiya banason turomin wadan Nan sticks din kokuma*👍❤️💃 *bawai bamajin dadiba idon aka turo wannanba a,a munaji saidai munfi bukatar comment akan komai, ina godiya sosai my fans Allah yabar kauna*
❤❤

*By*

*Khadeejah(Ummu Fu,ad & Afnan)*

🙆🙆 *RAYUWATA CE*🙆🙆

*Na*

*Khadeejah sani (journalist)*

🌈 *Kainuwa writers Association*📝
*Dashin Allah*

(United we stand and succeed our ambition to entertain and motivated the mind of readers)

*Sadaukarwa gareki sisternah masoyiyata Ayshat m zazzau Allah yabar kauna*❤

🅿 *5 _ 6*

Mahbub ne yafito daga cikin gida dagudunsa yayi wurin da wannan mutumin yake ganin Babu motarshi yasakashi kallo wurina naji yace
"Anty uncle tafiya yayi naga bayanan?" Banza nayi dashi yakara kwadamin wani Kiran nanma banza nayi dashi harya gaji yakaraso wurina wurgamai harara nayi tare da fadin
"Baka da hankali ko kakeyimin irin wannan Kiran Kumar baka San wurin danake zauneba nagode" ina fadar haka najuya naci gaba da aikina,

Komawa yayi gida zuwa can saigashi yakara zuwa ya tsogunna yace
"Anty innarmu tace kije kibani suyar tana kiranki" cikin tsoro da fargaba nace
"Mahbub mekace mata nayi maka?"nafadane kawai bawai Ina tunanin hakanba nasan abinda zata tambayeni,
Cikin sauri ya zaro Ido yace "wallahi anty Babu abinda nace mata kawai tace kijene" bankara maganaba saidai na Mike nayi cikin gida cike nake da fargabar abinda zatacemin,

Tsaye natadda innarmu tana jirana kallonta nayi naga fuskarta ahade don haka nakoma baya baya da ita inadan yake baki irin murmushin Nan da akewa lakani da kafi kuka ciwo nace
"Innarmu gani" wani kallo ta watsamin sannan tace
"Waye wannan mutumin?"
Dafe kirjina nayi nace
"Wanne innarmu banganeshiba" harara tskara yimin tace
"Mai siyan awara nake nufi wayeshi nafisa banason munafurci kifadamin gaskiya wayeshi Kuma meye tsakaninki dashi" ai cikinane yayi wata irin murdawa datasakani dafeshi sannan nafara fadin
"Wallah Allah innarmu bansanshiba kawaidai Yana zuwa siyan awara Amma baya ga wannan Babu wata alaka tsakanina dashi sai sai........" Shiru nayi Inna raba idanu dakamin tsawa tayi tace
"Saime kibude baki kiyimin bayani banason munafurci fah kinsani"

Jikina Banda rawa Babu abinda yakeyi don innarmu tahanani karbar wani abu ahannun wani don haka atsorace nake wata uwar tsawa data dakamin tasakani dawowa daga duniyar tunanin dana lula don haka nadawo hankalina nafa fada mata abinda ya faru dazu danaje wajen registration din jamb har zuwa tahowa danayi da kudin da zummar idon nazo gida yazo karbar awara zan bashi abinsa nafada mata Kuma yadda mukayi dashi Dana kaimasa shiru nayi ina jiran amsar da zata bani,

"Uhmm wato saboda baki maidani bakin komaiba shine baki fadaminba kika Kama bakinki kikayi shiru karkiga kamar Ina takurakine akan Hulda da maza wannan dakikaga inayi miki shine tarbiyya Kuma shine dacewa shine Kuma daidai agareki 'ya mace don haka wallahi kikula duk talaucin damuke ciki banyarda da wannan shashancin ba ki kiyaye Kuma gobe idon yazo kifada Masa inason magana dashi don bazamu karbi kudinba saiyazo zanbashi kudinsa mungode da taimakonsa garemu ko wannan awarar dayake siya tawadatar basai yayi dawainiya damuba kije Allah yayi miki Albarka" cikinsu kuka nadurkushe kan gwaiwowuna nafara Bata hakuri Nan tadagani tace Babu komi inje Allah ya tsare,

Saida na wanke fuskata sannan nadawo naci gaba da Sana,ata,

***********

*Wacece nafisat*

Sunana Nafisa Adam jiggo maifina su biyune agurin iyayyensu suntaso cikin kulawa saidai mahaifinsu Wanda akewa lakani da jiggo talakane ahaka suka taso suna zuwa makaranta Boko da Allo har sukayi sauka yayan babana mai Isa isya shine yafara zuwa wajen want mai hali alayin nasu yake binsa kasuwa ahaka harya Fara samu awurinsa sosai shikuma babana Yana sanar Saida rake da gurji akofar gida suna haka wani bawan Allah yazo wurin Ahj jiggo yace yanaso yabashi yaronsa Wanda ke Saida rake yadunga bisa kasuwa don bashida yaro Kuma ya yaba da hankalinsa ikon Allah Babu want musu ya amince da batun Nan yafara zuwa kasuwa shekararsa biyu da rabi wannan bawan Allah yakara bunkasa akayi lissafi yaga riba sosai don haka yabawa abbana kudi mai yaw yace yayi jarin kanshi,

Alhamdllh wannan kudi daya bashi shine yadunga bankarashi harya zama wani ahaka ya hadu da innarmu itakowa itadayace agidansu mahaifi ta ya rasu sai mahaifiyarta wadda ke ruke da ita haka akafara shirye shiryen biki ba Bata lokaci akayi bikin tare Dana Dan,uwansa yayansa aka hada abbana ya Gina gidanshi shikuwa yayanshi baigina gidaba Amma alonacin yasiyi fili yace bayan biki zaifara gini ahaka suka fara rayuwarsu matar baba isya itace tafara haihuwa tahaifi danta namiji lokacin innarmu batada ciki ahaka akasha shagalin suna,

Saida tayi kusan shekara uku sannan innarmu tasami ciki ta haifi yarta mace Amma tazo Babu Rai alokacinne itama matar baba isya takara haihuwa tahaifi namiji,

Bayan shekara takara haihuwa akasami Yaya yaci sunan babanta Khalil shine muke kiranshi da yaya,
Yaya yabani suekara shidda lokacin da innarmu takeda cikin mahbub lokacinne kuma Allah yayiwa abbanmu rasuwa munji mutuwarshi sosai  don lokacinma bani da wayo sosai  don haka mahbub baisan abbanmu ba sai a hoto,

Nikuwa tsakanina da mahbub shekara gomane don yanzu inada shekara 19 shikuwa shekara 9 bamu Jima da fara awaraba da innarmu tana saida kayan miyane taga abin sai ahankali shine bayan nayi candy nabata wannan shawarar ta awara akofar gida da taki amincewa saikuma daga baya ta amincewa dakyar don ko Yaya baisan munayiba yatafi neman kudi Legos.

***************

*Cigaban labari*

*By*

*Khadeejah (Ummu Fu,ad & Afnan)*

[8/29, 7:24 AM] Hayat: 🙆🙆 *RAYUWATA CE*🙆🙆

*Na*

*Khadeejah Sani (Journalist)*

🌈 *Kainuwa writers Association*📝
*Dashin Allah*

(United we stand and succeed; our ambition to entertain and motivated the mind of readers)

*Sadaukarwa gareki masoyiyata abar alfaharina kisani dukkan addu,o,inki Ina jinsu kuma Ina

godiya Allah yasaka da mafificin Alkairi yabar kauna wannan page din nakina nabaki kyauta kiyi yadda kikeso da abinki Sai Wanda kikayi niyyar bawa nasan kinsan kanki antynah FAREEDAH AUWAL Ina yinki*❤❤

🅿 *9 _ 10*

Shiga nayi nasami nafisat zaune tana duba wani littafi don ita harta fara zuwa makaranta kuma tare mukagama secondary sallama nayi ta tashi da sauri tare da rungumeni Tana fadin
"Wallahi yau din Nan magama tunaninki nace kokinyi registration din jamb kokuwa bakiyiba?" Murmushi nayi nace
"Wallahi nayi dazu da safe naje fce nayi harmace kilama kina makaranta yanzu"

"Aikuwa kamar kinsani inacan din"
"Ayyah bansaniba danaje mungaisa dake kuma aima bansan ajinba ai"
"Eh saidai hakan kuma aikece haryanzu bakida waya da kinada ita dasaiki kirana don Allah kiyi waya ko tanan arunga zumunci haba saikace ba buduruwaba" murmushi kawai nayi nace
"Allah y hore zanyi insha Allah"
"Ameen ammadai banajin dadin rashin wayar Nan naki Allah"

Wucewa nayi cikin dakin Ina fadin "komai lokacine takwarata kibari Allah zai bada yadda yadda yadda,ayi Amma ana takai wayake ta kaya"

"Indai hakane to nikuma bari nabaki dayar wayata dake ajiye bana amfani da ita ammafa karamace"
Hijjab din dake jikina nacire tare da fadin
"Kedai baki rabuwa da surutu lokacin sallah yayi kuma baba Yana dawowa Daga masallaci zai nemeni karyaji ban idar da sallah bah yayimin fada" Ina gama fada nashige toilet din dake dakina,

Bayan mun idar da sallah Ina zaune ta tashi ta bude wata jaka tadakko wayar tadawo kusa Dani tare da zama tace "yawwa gashi saiki siya layi naira darine ko Dari da hamsin don Allah karkice bazaki karbaba nasan halinki yanzu zakice Inna indai kikace mata nice nabaki nasan bazatace komaiba kitaimaka ki karba please my lovely sister karkiyimin haka" takarasa maganar cikin rausayar dakai gefe,
Kallo kawai nabita dashi bankai ga maganaba naji mama na kirana tashi nayi batare Dana karbaba nayi falon don dakinta Dana Mama Dana afalo Daya suke,
Ina shiga bakina dauke da sallama na tadda baba yadawo Yana zaune saikuma Yaya dake gefansa dakuma Mama itama Tana zaune karasawa nayi na zauna akasa tare da kara gaidasu Saida na gaida baba sannan mama sannan Yaya dake wurin dakyar ya it's amsawa nidai nace kaika Sani yaddama yakemin yauyafi na kullum don haka banwani damuba tunda yasaba,
Babane yafara magana hakan yadawo Dani Daga tunani nabada hankalina Nita fara yiwa

tambaa wadda tabani mamaki yace

" Nafisa kinada Wanda kike some yanzu haka Wanda kikayi alkawarin aure dashi?" Dagow nayi cike da Al ajabin tambayar da naji yayimin dorawa yayi da fadin

"Karkiji nayi Miki wannan tambayar inasone nacika alkawarin Dana daukarwa Dan,uwana yabani amanarku baki Daya yafadamin narikeku kamar yarana don haka nakeso na aurar daku dake da nafisa da yayyannaku baki Daya nafisa tun kwanaki nagane sun daidaita da yayanki shikuma wannan" ya nuna Yaya dake zaune yace "Naga haryanzu bai fidda wataba shine nakiraki kema don naji ya abin yake" sunkuyar dakaina nayi zuwa can nace

"Baba Babu kowa damukayi alkawarin dashi"

"To Masha Allah inason don Allah dukkanku kuyimin afuwa dajin abinda zan fada kugafarceni inason had a zumunci tsakaninki da yayanki kuyi hakuri kudaure karku bani kunya" Banda faduwa Babu abinda gabana yakeyi Jin abinda baba yafada mamaki tsoro fargaba dakuma tunanin mehakan yake nufi nidai nasan yadda baba yake bawani damuwa yayi damuba haka kuma tunda abbanmu ya rasu zan,iya cew baifi sau biyu ko uku yazo gidanmuba baya want nuna Mana kulawa Amma yau kawai yazomin da zancen hadani aure da yaronsa bayan bama jituwa tsakaninmu,

Cikin tunanin naji yace "nasan zakuyi mamakin Jin abinda nafada ba abun mamaki bane tunkafin Dan,uwana ya rasu munyiwa kanmu alkawarin hada yaranmu aure to Sai Allah yayi Shibamai tsayin kwana bane, ajiya nakwanta bacci bayan sallahr asubah nayi mafarkin Dan,uwana yakara jaddadamin zancen had a zuri,armu aure hakanne yasakani taraku don nafada muku abinda yake raina kuma burinmu na farko da mukeso muga muncika" shiru wajen ya dauka nawasu lokuta zuwacan Yaya yafara magana

Cikin yanayin da bazaka ita gane abinda yake cikiba yace

"Allah yasaka hakane yafi Alkairi yabamu ikon cika muku burinku" Ameen suka amsa dashi nidai shiru nayi nama rasa baking magana babane yayimin magana yace

"Nafisa bakice komaiba" cikin dauriya da hadiye kuka nace

"Allah yabamu ikon rike Alkawarin da muka dauka" Ameen suka Kara amsawa dashi nan baba yace

"Insha Allah gone zanzo wurin innartaku zamuyi magana da ita" to nace tare da mikewa nace "baba zantafi dare yanayi" mamace wadda tunda aka fara magana batace komaiba tace

"Kibari ayi sallahr Isha,I Sai yayanku yakaiki amotarshi Kinga dare yayi ga garin Nan Sai ahankali" to nace tare da komawa dakin nafisa Ina shiga ta rungumeni tace

"Wayyo Dadi naji dadin amincewarku keda Yaya Masha Allah" kallonta nayi nace

"Wai dama kuna tare da Yaya shine baki taba fadaminba kuma bantaba ganewaba wallahi" dariya tayi tace

"Wallahi cewa yayi karna bari kisani Amma ai innarmu tasani hakama mama da baba"

"Hmm lallaine wato ni akabari abaya kenan" dariya takarayi tace

"Kinga kusa yadda kikayi wani mugun dacewa keda Yaya Allah yabar kauna wayasanima ko kuma anata soyewa bamu saniba" murmushi kawai nayi bance komaiba,

Kiran sallah akayi hakan yasa natashi nayi sallah tunda inada alwallah nazauna Ina tunani Amma Inka ganni zakayi tunanin addu,a nakeyi,

Nafisa Bata dakin Mama tayi kiranta saigata tashigo da faranti dauke da abinci shinkafane da taliya damiya da nama ta ajiye tare da zaunawa tace
"Mama tace kiyi sauri muci kafin yadawo kutafi" kallonta nayi Ina niyyar yin magana tace
"Wallahi idon bakiciba saina fada mata nasan yanzu Zaki wanice kinkoshi" kallonta nakeyi abin mamaki kamar tasan abinda zanfada Sai kawai nafasa maganar,

Mungama cin abincin sannan mama takirani tace infito muwuce yashigo nace to
Dakko wayar tayi ta biyoni da ita tanata magiya har mukakai falo inda Mama ke zaune shikuw gogan naku Yana waje Yana jirana,
Ganin naki karba yasakata fadawa mama Nan mama tasaka baki har Saida nakarba nayi godiya tare da yimata sallama nafisace ta rakani harwaje,
Zaune yake cikin motar mukayi sallama sannan naje nakama niyar bude baya don banason zama kusa dashi yayita yimin kallonta banza jinai arufe nakara budewa naji arufe jin maganarshi nayi yace
"Me kika maidani dazaki shiga baya lallai raini yashiga tsakanina dake" Jin hakan yasakani komawa nabude gaba nazauna hararata yakeyi sannan yatada motar muka tafi,

Tafiya muke Babu Wanda yayi magana Sai zuwacan yace
"Inamai baki shawara kiyiwa kanki adalci ki ceci kanki kije kisami baba kicemasa bakisona kinada Wanda kikeso don wallahi aurena dake Babu abinda zaija Miki Sai wahala da rashin kwanciyar hankali kinsani tunda nake dake kallon kirki baitaba shiga tsakanina dakeba kuma bantaba Jin zan ita rayuwar aure dakeba ke Koda zama irin wanna acikin mota bana fata mukarayi dake balle zaman aure don haka kije kifada Masa bakya Sona inkunne yaji jiki yatsira" Saida nadauki lokaci sannan nadauke kaina gefe nafara magana nace
"Inaso kasani nima bana sonka kuma haka bana kaunar zama dakai matsayin mini da mata haka kuma Ina fatan Allah karya nunamin ranar dazan aureka harna zauna dakai gida Daya wallahi idon yanzu za,azo atambayeni ace nazaba Dana aureka Dana mutu cewa zanyi gwara na mutu dana aureka, kuma naji kayi maganar naje nafadawa baba inaso kasani ni inada hankali haka kuma inada tarbiyya bazan ita zuwa nafada Masa hakaba don haka Kaine yafi cancanta kaje kafada Masa baniba" Ina kaiwa Nana nabude nafita nabar motar don dama munzo kofara gida,

Zaune yayi Yama rasa abinyi wannan yarinyar shizata kalla tafadawa wannan maganar tan lallai batada kunya Amma zaiyi maganinta,

****************

Bangaransu Musa kuwa haka suka Kari zamansu basuga wucewata ba don haka suka tafi harkarsu sukace za,a had agaba don bazasu kyaleba.

**************

Ina shiga gida nasami Innarmu zaune tana jiran dawowata ganina datayi fuska Babu walwala yasakata maido da hankalinta kaina cike da tambayoyi,

Zaunawa nayi nace
"Innarmu yagida?"
"Lafiya klau kinbarosu lafiya?"
"Lafiya Lou duk suna gaidaki"
"Ina amsawa" shiru tayi tana jiran Jin abinda zance mata nikuwa saina kauda kaina Ina kallon mahbub dake bacci nace "ohh ni mahbub haryayi bacci"
"Kinganshi Nan yayi bacci Wai cikinsa ke ciwo"
"Ayyah shiyasa yayi bacci Allah yakara sauki"
"Ameen aiyasha magani me babban naku yace?" Tajefo min tambaya,
Zamana nagyara Nan nafara Bata labarin abinda yafaru harzuwa karshe tare da nuna mata wayar da nafisa tabani, nayi tunanin zatayi fadan waya Amma sainaji tace
"Allah sarki nafisa angode Allah yabiyata, maganar yayanku da nafisa nasani kuma nasan maganar hadin da yafda muku sunyi magana da abbanku Saidai ni daza,abi ta tawa da anhakura da hadaki da maisunan manya don bana ganin zai amince da wannan batun tunda nasan yadda kuke tsakaninku Amma banakiba Allah yabaku zaman lafiya da juriyar zama da juna" shiru nayi nandai mukadanyi fira kadan natashi natafi daki nayiwa mahbub shinfida nazo natasheshi ya koma daki sannan nayiwa mama saida safe nashige daki,

Tunani barkatai ya hanani bacci nidai nayiwa kaina alkawarin bazan taba bari yayimin abuba banrama ba,

Shima nashi bangaran haka yayita tunani haryaje gida haka kuma yazauna yakasa bacci Sai wuraren karfe uku sannan yasamu bacci ya daukeshi.

***************

Washegari da yamma....................

*By*

*Khadeejah (Ummu Fu,ad & Afnan)*
[8/29, 7:24 AM] Hayat: 🙆🙆 *RAYUWATA CE*🙆🙆

*Na*

*Khadeejah sani (journalist)*

🌈 *Kainuwa writers Association*📝
*Dashin Allah*

(United we stand and succeed our ambition to entertain and motivated the mind of readers)

*Sadaukarwa ga masoya wannan book baki dayanku*

🅿 *7 _ 8*

Zaune nake nacigaba da suyar awara saiga Musa da abokansa yazo ina hangosu nakautar dakaina nayi kamar bangansuba,

Karasowa sukayi musane yafara yimin magana banza nayi dashi jinko sallama basuyiba sai dayanne Wanda naji suna Kira da Zaki yace

"Kai jaki bakayi mata sallamaba shine zakawani fara damunta da magana nifa duk Wanda yake kokarina takura mata wallahi zamunyi fada zan iya fafewa mutum ciki Allah kuwa idon yanemi yatakurata"

Musa yanajin haka yafara kame kame da fadin

"uhm.....a,a...ai Babu wani takura tobara nayi sallamar" Nan yayi sallama amsawa nayi ahankali don bana tunanin sunjinima,

Kallon sauran mutum biyun yayi yace

"Ku bazaku iyayin sallamarba kenan yan,iskan yara" cikin rawar baki suka fara rige rigen sallama sumadai amsawa nayi batare dasunjiba,

Zakine ya dunrkusa agabana Yana wani kalar murmushi yace

"Buduruwata wallahi ina masifar sonki idon naganki jinakeyi kamar nadaukeki naguda kinsan kuwa yadda nake Sha,awar kasancewa dake Allah yabani ikon mallakar jikinki babenah"

Kallonshi nayi Raina banda baci Babu abinda yayi nace

"Wai meye haka don Allah kazo wurin Sana,ata kana takuramin gaskiya banason wanna halin dakakeyimin nidai gaskiya kadaina banaso" nakarasa magana cikin bacin rai sauke kaskon nayi don Daman nagama soyawa don haka nakira mahbub dake kusadani zaune Yana was nace yazauna yajire zantafi gida,

Don Daman haka nakeyi indai nagama soyawa Bata kareba shinake barea nikuma nakwashe kayan nakoma gida,

Saida nagama dauke kayan saura iccen dayayi ragowa kawai sannan nazo nadauke iccen

zantafi gida nayi hanyar shiga gida kawai naji mutum nabina abaya Kiran sunana yafarayi nayi banza dashi kawai saiji nayi yakamo hanuna cikin sauri najuya afusace nace

"Dan Allah menene haka banason irin hakafa nafada maka" ina kaiwa Nan nakara juyawa nayi hanyar shiga gida hanuna dake rike da icce naji yariko tare da fizgoni jikinsa,

Iccen dake hanuna ya zube kasa nikuwa nayi taga taga zanfadi naji ya kamoni yahadani da jikinsa cikin sauri na tunkudeshi tare da wanka mishi mari guda biyu sannan na nunashi da yatsa nafara magana cikin kuka

"Wallahi banyafe makaba Allah ya,isa tsakanina dakai kuma........"maganarce ta katse iya nan don kukan dayaci karfina,

Cikin gida nayi da gudu in kuka maicin Rai Ina shiga naci sa,a nasamu innarmu tana Dakin abbanmu nada tunkafin ya rasu don haka nashige daki nafara kuka maicin rai kwantawa nayi abakin gado Ina kuka narasa me wadan Nan mutanen suke nema agurina bawani Abu bane face sunaso kawai suketamin haddina amatsayi a na yamace inba hakaba meyayi ruwana dasu inajin kalar abinda sukeyi acikin unguwa har yara kanana sukewa fyde batakaran manyaba nashiga uku ni nafisat Yaya zanyi da wanna musiba Allah kayimin katangar karfe da wadanan mugayen mutanen don Alfarmar annabi muhammad(s.a.w)...Kiran da innarmu take kwadamin ne yasakani saurin goge fuskata natashi nadan gayara sannan nafita in amsawa

"Kingama soyawar ne naga kinshigo da kayan?"

"Eh nagama nabarwa mahbub Yana can da ita"

"Masha Allah tunda kingama kizo kije gidan babanku isya yakirani Wai kije yanason ganinki". Fuska nabata don banason zuwa gidan nashi yaronshi mai sunan babanmu bashi da kirki Shima gashi hakan take gwarama mama itace mai kirkin don innaje harda kudin mota take bani Wai karnayi tafiyar kasa dukda Babu nisa tsakaninmu katsemin tunanin tayi wurin cewa

"Kiyi sauri kije kidawo kar magriba tayi miki" kallonta nayi nace

"Waima innarmu mezanyi Masa dayake want kirana?" Dakuwa tayi min tace

"Ungo naki ja,irar yarinya Kai baban nakuma bazakije kiji Kiran da yake yiminkiba to inkinyi niyya kitafi kidauki naira hamsin kiyi kudin mota don kardare yayi inkuma kinso kibar zuwan Babu ruwana" tana kaiwa Nan tashige daki hakan yasakani komawa daki na dakko hamsin cikin kudin Dana shigo dasu nafito nayi mata sallama natafi,

Tafe nake Inna tunanin meyasa baba zaiyimin wannan Kiran na gaggawa haka kodai wani laifin akace Masa nayi nidai nasan baitaba kiranaba rana tsaka saidai idon yaso bamu abincine zai Kira innarmu yace ta aikoni ta karbar Mana abinci Shima kuma sai azumi azumi yake bayarwa don haka natafi like da tunani,

Lokacin Dana wuce abinda bansaniba shine ashesu Musa suna zaune suna tattaunawa akan Marin danayiwa Zaki kowa Yana kawo kalar shawarar data dace shidai zaune yake yama kasa magana Yana tunanin irin cinmutuncin dazai yimin don yahuce cikin hakan ya ganoni aikuwa yayi saurin mikewa Suma cikin sauri suka tashi suna tambayarshi meya faru nuna musuni yafarayi Yana fadin

"Wallahi saina Rama wulakancin da waccen yarinyar tayimin yau dinan bazan tana yaddaba

narantse da Allah saina keta mata mutunci yau din Nan zan huce takaicin watannin danayi in Sha,awarta don haka Kai Musa maza kabita kaga inda tanufa munan biyoka abaya don karta ganmu da yawa" cikin sauri Musa yacika umarnin Zaki yabi bayana nikuwa bansaniba inata sauri don naga yamma tayi sosai,

Ganinki naje titi yasakashi tsayawa kusa kusa dani don haka yajiyo inda zanje lokacin danake fadawa mai adaidaita Hawa nayi natafi batare danasan Yana bayanaba,

Komawa yayi yafadawa Zaki Nan yasaki dariya yace
"Nasan Nanda zuwa magriba zata dawo don haka cikin lungun can wurin wannan kangon zanje nazauna kuma kowa yasami wurin boya tana dawowa zancika mata aiki yau dinan" dukkansu dariya suka saka lokaci Daya kowanne kuma Yakima inda ya nuna musu don zama,

Lonacin Dana sauka nayi cikin layin dondaima bawani nisa Daya titi har yamma tayi sosai don akallah shidda da rabi zatayi don haka nace "ainasanma sainakai bayan magriba don yanzu zaice saiya dawo Daga masallaci,
Shiga nayi gidan tare da sallama nasameshi Yana alwallah don haka na tsugunna na gaidashi amsawa yayi sannan yace
"Saikiyi sallah kafin nadawo don lokaci yayi" to nace tashi nakarasa daki. Mama karo nakusanci da Yaya Adam mai sunan abbanmu kenan don haka nayi saurin yin gefe guda in fadin
"Ina yini" wani kallo yabin dashi na rainin wayo sannan ya wuce abinsa tabe baki nayi nashige cikin dakin Mama nasmu zaune don haka nagaidata ta amsa cike da Fara,a tace
"A,a ga antynah ga antynah sannu da zuwa Daman yanzu nagama maganarki da yayanku nace babanku yace kizo Amma najiki shiru Ashe kina hanya Amma da yammar Nan taturoki sannu da hanya" zama nayi Daga kasa Ina gaidata ta amsa tace
"Ya innar taku"

"Tana lafiya tace agaidaku"
"Muna amsawa Ina mahbub yake bakuzo tareba"
"Eh Yana gida nabaroshi".
"Allah sarki bari nayi sallah idon zakiyi ga dakin takwurarki can kishiga itama Tana ciki saikiyi alwallar aciki kawai" to nace tare da mikewa nayi dakin.

*Inakara fada muku fans yawan comment yawan typing banajin comment mai yawafa Wanda zaisakani kwarin gwaiwar yimuku kullum sau biyu saidaima yakashemin jiki naji bazan iyayiba kullum inkuna yimin zanfu yimuku typing Mai yawafa fans saina jiku*

*By*

*Khadeejah (Ummu Fu,ad & Afnan)*

🙆🙆 *RAYUWATA CE*🙆🙆

*Na*

*Khadeejah Sani (Journalist)*

*_🌈KAINUWA WRITERS✍🏼 ASSOCIATION_*🤝🏻
```{United we stand and succeed;Our ambition is to entertain & motivate the mind of readers}```

https://www.Facebook.com/kainuwawritersassociation

*My lovely Mom godiya nake da addu,arki gareni Allah yasaka miki da mafificin Alkairi Allah yaraya kanena Allah yabarki da dadynmu nagode momynah Samira Haroun Allah yabar kauna my mom*❤❤❤❤

🅿 *11 _ 12*

Zaune nake Ina soyar awara kamar yadda nasaba mutane nata siyan awara don harta kusan karewa,

Motar wannan mutumin Daya jajamin masifa nagani yazo yatsaya Yana kallon wurin danake zaune kauda kaina nakarayi kamar bansan yanayiba mahbub dake zaune kusa danine yadago da niyyar yimin magana ai ganinshi dayayi yasakashi tashi aguje atunanina wurinshi zaije saikawai naga yayi gida da gudu yaje yafadawa mama don nasan ita yatafi fadawa,

Saigashi yafito da gudun yaje Yana fadin
"Uncle sannu da zuwa Ina yini ya aiki Wai Innarmu tace kashigo zakuyi magana" duk yajera maganar ahade
Murmushi yayi yace "to buy Dina muje"
```

Hannunsa yakama suka shiga gidan,

Tsugunnawa yayi har kasa itama Inna ta tsugunna suka gaisa cikin mutunta juna sannan Inna tafara tambayar shi Akan maganar kudi,
Nan yafara magana yace
"Inna kiyi hakuri banayi hakan bane dawata manufa a,a nayine saboda Allah dakuma yadda mahbub yashiga Raina wallahi Inna tunda nake bantaba ganin yaron Daya shiga rainaba kamar mahbub da nayi tunanin kodon banida kannene yasa nakejin kaunarshi Sai Daga baya nagane bahaka bane kawaidai soyayyarki ce Allah yadoramin, Inna don Allah kiyi hakuri da kudin Dana biyawa Nafisat na jarabawa nayine saboda Allah nasan dole saikin nemi ba,asin biyan danayi mata kiyi hakuri Inna idon hakan danayi yabata Miki rai" Yana kaiwa Nan yayi shiru tare da sunkuyar dakai Yana jiran Jin abinda zatace,

Saida ta sauke ajiyar zuciya don tayarda da maganar wannan yaron dari bisa dari magana tafara tace
"Nayarda da dukkan jawabinka kuma na amince dasu Amma abinda banaso shine, yiwa yarinya mace kyauta bakamar kyautar kudi banasonta saboda Babu Dadi cikin tarbiyyar yarinya mace adunga Bata kudi kasan saboda tasani na hanata kuma Koda kabaya tafito zata baka kudinka Bata gankaba wallahi bata fadaminba saita ajiyeshi har Saida kazo kabawa mahbub" Nan Innarmu tabashi labarin yadda mukayi da ita sannan tadora da fadin
"Mungode mungode Allah yasaka da Alkairi Allah yabar zumunci dama wannan shine Kiran danayi maka don naji yadda akayi"
Shafa kanshi yakarayi yace
"Nagode Inna Allah yasaka da Alkairi Nagode da fahimtata da kikayi" Nan sukayi sallama harzai fita tace "namanta banji sunan yaron nawaba" murmushi yayi sanan yace
"Sunana Muslim Muhammad yaro"
"Allah sarki aikuwa kamar inajin irin sunan Nan a radio da tv da muke kallo da nadai manta Yaya sunan yake" murmushi yakarayi yace
"Eh mahaifina ne kill kukeji"
"Allah sarki Allah ya taimaka" Ameen yace sannan yayi waje,

Mahbub tabawa awarar tace yakaimasa,
Dauka yayi yafito da ita,

Zaune nake Ina sallamar mutane Amma hankalina Yana gida ganin wannan mutumin yashiga yasa naketa kallon kofar gidan Ina haka maga yafito Yana murmushi kallonshi nakarayi har muka had a Ido saiga mahbub yafito da bokitin awarar Yana fadin
"Uncle gashi dama tundazu Innarmu tagama jiranka kawai takeyi" karba yayi yabode yadauki Daya yasaka abakinsa yace
"Kaima dauki kaci"  girgiza Kai yayi yace "umm umm nakoshi"
Kallonshi yayi yace
"Dama Ana koshine da awara Maza jeka wurin anty kakarbo Mana leda guda biyu don inaso

nakaiwa abbana yaci Shima" da gudunshi yakarasa wurina yace
"Antynah uncle yace kibashi leda guda biyu zai kaiwa abbanshi awara kingashi abbanshi Yana Nan baiyi tafiyaba mukuwa namu yayi tafiya" hawayene ya wankemin fuska naguge tare da Mika Mai ledar kallona yakeyi na tsayin lokacin sannan yajuya Shima Yana goge hawaye duk da baisan abbanmu ba amma indai zaiga muna maganarshi Ina kuka Shima saiyayi don haka yanzuma yatafi Yana kuka,

Kamoshi yayi jikinshi yace
"Meya faru kuma buy Dina ko antynmuce  tayima want abun"
Goge hawayene yayi yace "Babu abinda tayimin waidannace Kai abbanka Yana Nan baije ko inaba mukuwa namu abban yatafi kuma Inna tace bazai dawoba shine take kuka nima tasakani" tausayi suka bashi Ashe mahaifinsu yarasu Nan yashiga lallashinsa har yayi shiru,
Dibar awarar yayi da danyawa yasaka amota sannan ya dibarwa mahbub Shima yabashi duk da yaki karba Saida ya had rai sannan yakarba,
Bawan yaran dake tsaye yayi sannan yabashi kudin awarar Yakima bashi dari biyardin dayake bashi ya dakko wasu kudin dabaisan yawansuba yace
"Wannan kacewa Innarmu ta siyi want abun" Yana gama bashi yatada motarshi yawuce,

Kaiwa Innarmu yayi kallon yawan kudin tayi tace
"Wato kara zugashima nayi danace yadena bara kudi ai shikenan angode Allah yasaka Mai da mafificin Alkairi"

Saida nagama suyar awara sannan nakoma gida labarin abinda yafaru innarmu tabani yadda sukayi da mutumin data cemin sunanshi Muslim acikin zuciyata nace suna Mai Dadi,

Sai bayan sallahr magriba sannan nafita siyan wake nikadai natafi don anayin magriba zazzabin mahbub yadawo sabo kwance nabarshi nafito,

Take nake Ina sauri don unguwarmu Babu mutane sosai balle kuma idon dare yayi,

Take nake Ina sauri harnaje kantin dake karshen layinmu nakuwa cisa,a Babu waken don haka natsaya nayi jigum Mai kantin need yace "Nafisa kije shagon ya,u na hanyar titi Yana saidawa" to nace tare da yimasa godiya natafi don nasiyo,

Hanyar tayi duhu da yawa saboda Ana gab da Kiran magriba gashi lokacin damuna dare yafi yin duhu don haka garin yakara duhu sosai harna karasa kantin nakuwayi sa,a akwai don haka nabashi kudin zai aunamin donma Ina tahowa da buhu tunda kwano uku nake siya saboda yiwa Muslim,

Abinda bansaniba Ashe su Musa sunganni lokacin da zantafi don haka suketa Bina abaya har sukaga nashiga kantin don haka suka koma inda suka boye na jiya suna jiran dawowata nikuwa dayaye bansan me suka shiryaba sauri kawai nakeyi Yana gama zubamin takarba nariko abona don naruga nabawa Mai kantin layinmu kudin Mai da Magi zanje na karba agunsa innadawo,

Take nake hankali kwance inata sauri don nabar mahbub kwance yanata rawar sanyi Innarmu kuma tana dakinta Bata saniba don banfada mataba,

Kawai jinayi anjawoni tare d rufemin baki iho nake komarinyi Amma Babu dama har sukayi nasarar shigar Dani cikin kangon kwacewa nakeso nayi Amma Ina karfin namini da mace badayaba don haka sukafi karfina,
Kwacewa nake Ina kokarina yin kara Amma Ina nakasa wazan gani akaina ba zaki saikuma Musa dayake tintsira dariya yace
"Oga gala ga ita saiyadda kayi niyya Inka gama Ina jira nima" Jin abinda yace yasakani kara kokarina kwacewa Ina niyyar yimusu magana kawai naji an daukeni da want gigitaccen mari zafafa guda biyu ihun danakeson yine yayi kokarina fitowa...............

😱😱😱 Ohh nice deejah nafisa Allah yakubutar dake baiwar Allah kubiyoni muje zuwa.

*By*

*Khadeejah (Ummu Fu,ad & Fnan)*

[9/3, 7:19 AM] Hayat: *🦚🇳🇬🦚SOJA NA🦚🇳🇬🦚*

*👨‍✈️👨‍✈️The Sweet Army👨‍✈️👨‍✈️*

*⚠Not Edited*

*✍🏻Story with writing by*

_*Zeeabusafana-Mrs'Salihu Bamalli*_

*HAJOW*✍🏻

_*My Social Media Accounts*_

_Facebook_
*Xynervah*
_Instagram_
*Official_Zeeabusafana*
_Snapchat_
*Zeeabusafana*
_Michatt_
*Official Zeeabusafana*
_YouTube channel_
*Zainab Abubakar*
_imo chatt_
*zeeabusafana with my phone number*
_2go_
*Zeeabusafana*
_Yahoo_
*zeeabusafana@yahoo.com*
_WhatsApp_
*My phone number*
_E-mail Add..._
*Zeeabusafana@gmail.com*

✍🏻3️⃣
"Wani hadadden school yayi parking kafin ya budeta ya kama hanyar upstairs din yahau itama tabi shi da sauri yace da wannan kazamin hijabin naki da kika bata da kwalli zaki bini waike ni tsaran ki ne removed it.....jikin ta ya hau kyarma duk da bata san meh yace ba da karfi yace' ba zaki cire ba sai nazo na kwakule miki wa yannan idanun naki kin min zuru sai kace mayya ki cire shi nace' da sauri ta cire hijabin ta ajiye a saman motar suka shiga har office din shigaban makarantar bayan sun gaisa Mutallaf ya masa bayanin komai daya kamata a kanta!

" gaskiya tayi girma da primary school but zamu duba muga meh ya kama ta ayi tunda kace

bata san komai ba!

"Yes of course am sure ko A bata sani ba!

OK no problem but is better ki samu wani yana yi mata lessons a gida before muyi taking dinta sai muga abunda ya kama ta ayi!

Okey thank you ya fada sannan suka fito islamiyan dake kusa da layin su yaje akayi mata interview a fannin islamiya kam babu laifi sai dai bata jin larabci nan sukayi shawarar ajiyeta aji hudu wato ajin su Mimi daga nan suka dawo gida!

'A falo ya sama su mom ya musu bayanin komai gwaggo tace' Keh zonan meh ya miki ne naga idon ki yayi jah ga hijabin ki kamar kunyi kokowa da kato meh ya faru?

'Harara ya bankowa gwaggon yace' kashe ta nayi ta farfado shikenan ko?

Zaka aika mugun kawai daman sojoji imani ne dasu ai ko kadan baku da imani baku da hankali duk munafukai ne yan banza ga Neman matan tsiya babu kamar kai mai warin ya'yan arna ai nikam ban yarda dakai ba wallahi ko daganin ka akwai wata a kasa dan sam ban yarda dakai ba katon banza mala'ikan yaran mutane!............. A fusace ya shige part dinsa gwaggo nabin sa da bakaken magan'ganu da zagi!

" da sauri ya fito da bindiga ya nufi gwaggo! Ta kuwa dora hannu bisa kai wayyo ni indo na boni na shiga casa'in da bakwai jama'a ku taimake ni zai karni!

"Kiyi shiru nace miki!

Da sauri gwaggo ta kama bakin ta tayi shiru

" mom tace' wallahi Mutallaf zan saba maka ja'iri kawai baka jina ne!

Matso da kan bindigar yayi saitin kan gwaggo yace' it was the first with last warning idan kika sake cemin mai warin arna saina harbe ki kowa ya huta da jarabar ki a gida nan ya fada tare da

dana kunamar bindigar jikake tasss! Ya harba gwaggo kam fadi tayi yaraf!

"Ita kam mima aisai ga futsari ta saki a wando mom tayo kansa da gudu! Ya ruga ya rufe dakin sa tayi kan gwaggo data some saboda tsabar firgita dai'dai lokacin duk yaran gidan suka fito saboda sunji karar harba bindigar!

" mama ce ta iso da ruwa ta fara shafawa gwaggo a hankali ta fara bude ido sukace gwaggo sannu!

Gwaggo cikin magagi tace"Rabbi yallahul'lazi kala qani!

Suka kara fadin gwaggo tace' diniyal Islam..............

Mom tace' gwaggo....

Ta kara cewa' a chan suna na indo anan sai yadda kuka bani...........

Aikam dukkan su suka kwashe da dariyar mugunta wasu harda dafe ciki wasu da hawaye wasu kam har kasa!

Nene dake dauka a waya idonta tab da hawayen dariyar mugunta!

Dariyar sune ya fara maido da gwaggo a hayyacin ta tagane ashe ba'a kabari take ba, a falo take Sadiq ya dauko flower din da Mutallaf ya harba ya ajiye suna ta dariya!

Gwaggo tana dawo wa hayyacin ta sai kuma ta daure fuska tare da fafukar su suka bar falon suna dariya.

Da dare Mutallaf yaki fita zuwa cin abinci dan kuwa yana tsoron kar gwaggo ta sanarwa su Abba abunda ya mata!
Lura da bashi a gurin yasa mom ta kirasa bai dauka wayar ba saboda yasan kiran dan haka ya fito white shirt ne mai guntun hannu a jikin sa sai army trouser 3qtr hannun sa daure da army watch kirar Gucci fuskar sa a tamke tamkar bai taba dariya ba ya zauna yana yi yana satar kallon gwaggo wacce itama shi take kallo suna hada ido aikam sai ta kware tana tari sunnar dakai yayi yana murmushin mugun ta dan kam tabbas yasaan yau ya tsorata fitina niyar tsohuwar nan yama yi mamakin da bata fada ba dan haka ya maze!

Sauran duk sun fahimci dalilin kwarewar amma banda Daddy da Abba ruwa aka bata kowa na kokarin danne dariyar sa,
Abba ya dubi Muhsin yace' kai zaka ringa yiwa mima lessons na boko ke kuma Nana ki ringa mata na islamiya ina fatan kun gane?

"Eh Abba

Kai Mutallaf ina so ka shirya gobe in Allah ya kaimu ka dauke mima da Mimi da ma'ida suje su taya mima zaben kayan sakawa kana jina?

A hankali badan ran sa yaso ba yace' to Abba
(Shifa zuwan wannan kuchakar yarinyar zai saka a takura mishi harma ana cewa ya kwasa yara ya fita dasu mtseeww)

Washe gari kasancewar week end tun da around 9su Mimi ke shirin fita dogayen riguna suka saka tare dayin rolling gyale akan su takalma masu tsini suka saka da side Bag!

Mima ma irin shigar su Mimi tasaka tayi sai dai ita flat shoe tasaka tayi matukar kyau dan yau kam bata saka kwalli ta bata fuskar taba!

Sai kamshi suke suka fito lokacin harya fita da motar da mugunta ya dauka 406 ash! Sabuwa dal da ita a bakin get suka ganshi fuskar sa a hade ya fito ya bude booth din motar yace ku shiga!

Da sauri suka dubesa ita kam mima batayi mamakin jin hakan ba duk da tasan yau su ukku ne boot din ya musu kadan gashi Mimi da ma'ida suna da jiki ma'ida zatai magana yace' duk wacce tayi magana saina balla ta anan ku shiga nace dan uban ku! Ai kam da sauri suka shige a matse ya danne boot din da karfin sai da ya rufu ya tada sunyi mugun matsi danko akan junan su suke mimi da ma'ida kuka suke yi rurus kwalliya duk ta baci mima kam ko kyam batai kwalla

ba!

*Share $Comments*

_Mrs'Salihu Bamalli zeeabusafana_
_Momyn Sheikh Albany_
[9/3, 7:48 AM] Hayat: *🦚🇳🇬🦚SOJA NA🦚🇳🇬🦚*

*👨‍✈️👨‍✈️The Sweet Army👨‍✈️👨‍✈️*

*⚠Not Edited*

*✍🏻Story with writing by*

_*Zeeabusafana-Mrs'Salihu Bamalli*_

*HAJOW*✍🏻

_*My Social Media Accounts*_

_Facebook_
*Xynervah*
_Instagram_
*Official_Zeeabusafana*
_Snapchat_
*Zeeabusafana*
_Michatt_
*Official Zeeabusafana*
_YouTube channel_
*Zainab Abubakar*
_imo chatt_
*zeeabusafana with my phone number*
_2go_
*Zeeabusafana*
_Yahoo_
*zeeabusafana@yahoo.com*
_WhatsApp_
*My phone number*
_E-mail Add..._
*Zeeabusafana@gmail.com*

✍🏻2️⃣
" kwalli mima ta dauka tayi kwalliyar ta irin wacce tasa bayi a ruga tare da lafta janbaki kasan cewar bata iya daura dankwalin ba saita ci namara dashi a kugu irin yadda sukeyi inzasu wasa a dandali kai tsaye ta nufi falo!

"Gwaggo ce kadai sai mama dake latse'latse a laptop dinta tana sanye da farin gilashi irin nasu na likitoci yayin da gefen ta karamin table ne mai dauke da kwalin exotic da cup!

(Ajiyan zuciya mama tayi she already know dama sai sunyi faman ganin sun samu mima ta waye tunda rayuwar karkara ta iya matsalar ma shine yanzu idan za'a saka ta school ita ko A bata sani ba dafe kanta ta dan yi tare da fadin ohh! My God).........

'Surutun gwaggo ne ya katse mama daga dogon tunanin da takeyi ohni! Indo Allah mai zamani kuzo ku gane min wannan hauka! Saddiquuuuuuu!

Innalillahi wa'inna ilaihi raji'un haba gwaggo meh ne neh kuma wallahi danaji wannan kiran nasan ba abun arziki bane yasa aka kira ni gani!

'To sauna kama godewa Allah daya sa na kiraka'
Kidai godewa Allah ke daya sa nazo gani!

Kaga wannan kasan ta?

Duban mima yayi tare da girgiza kai yana dariyar kwalliyar ta tah!

Dariya gwaggo tai dauko wayar nan taka mai kama da talabijin kaita kashe min wannan kuchakar da hotuna manya a wanke a lika a falon nan saboda a duk sadda ta waye tagani taji haushi!

"Dariyar mugunta yakeyi dama shine abokin yin aikin ketar gwaggo a gida nan' mima na tsaye sokoko yai mata photo biyu sannan yace gwaggo ki bata style tadan chanja mana!
" harara gwaggo ta watsowa mima tace' ke gadan garki kidan kama kugun mana kinyi tsaye kamar bindiga dan dole mima ta kama kugu aka sakeyi matsawa yayi yana nunwa gwaggo pictures din suna dariya!

A hankali yayi sallama wanda yaja hankalin duk mutanen falon harda mima!
White shirt ne a jikin sa sai army trousers kafadar sa rataye da wata bag irin nasu na sojoji fuskar sa tamke sam babu annuri! Dogo ne faffada his a gentle man yana zubin jarumai kyakyawa ne iya haduwa fari Sol! Mai dauke da dogon hanci with pinck lips idanun sa masu kyawu suna dauke da eyelashes masu kyau girar sa gwanin sha'awa sumar kansa kwance take luff! Tamkar balarabe gefen fuskar sa saje ne a kwance yayin da yake da dimples wanda suka kara mishi kyau!

'Da sauri Sadiq ya karasa yana fadin army your welcome....dafa kafadar Sadiq yayi ba tare da yayi magana ba ya karasa cikin falon dadda'dan kanshin turaraen sa ya gauraye falon a nutse yake tafiya sai da yakai saitin gwaggo sannan ya banko mata harara!

'A kufule ta saki baki dan ubanka Ali ka harara da uwar ka rabi bani ba marar kunyan banza mai warin ya'yan arna!

"Takaici ya kamasa dan ya tsana warin ya'yan arnan da take cewa yanayi dan haka yakara kuluwa yace' ni indo na harara basu ba!
Wallahi zanyi maganin ka dani kake zancen ne yaro zaka sani ne!

Bai tanka taba ya karasa gurin mama ya zauna tare da dora kansa akan kafadar mama yana murmushi' shafa kansa tayi tace' dan albarka yau an leko mu kenan?

" rolling idanu yayi yes'mama

Good but ai is better ace ka sanar dana hada maka abunda kake so ko?

Nop daman ina so inyi surprising dinku ne.....

Kara shafa kansa tayi tace'masha Allah now kaje ka watsa ruwa ka huta ni kuma bari naje ni kitchen na Samar maka abunda zakaci ta fada tare da tashi!
Shima tashi yayi tare da bin bayan sadiq daya shigar mishi da jaka zuwa side dinsa!

Gwaggo tace'katon banza kawai dashi ni wannan iskancin da amina take koya maka nagaji da ganin shi to ta mayar dakai ciki mana shegan takar wofi kawai!

Dan matsawa yayi gefen ta a hankali yadda babu wanda zaiji yace' ai ba mayarwa ciki ba har Nono zata bani ma nasha!

Innalillahi wa'inna ilaihi raji'un! Na boni ni indo mai Jan kallabi wallahi wannan kam anyi dan iskan yaro ni kake fadawa irin wannan maganar bari iyayen naka su dawo zanyi maganin Kane!

Shikam baiko juyo ba yayi gaba abun sa yabarta tana kumfar baki ita kadai duban mima dake gefe tsaye tayi tace' ke kuma zankan'kam kimin tsaye zaki wuce kosai na barar dake anan da kai'kamar gonar masara!

"Gunguni mima tayi ta wuce'

Keh zonan zo zoo!

Juyowa mima tayi a kule gwaggo tace'meh kike cewa?

Yatsina fuska mima tayi tace' ni bance komai ba kawai tukka nakeyi!

" tukka uwaki ne tukka tunda ke akuya ce bari nazo saiki gayan tukka kike yi ja'ira........

A guje mima tabar falon ta koma daki tana dariya gaskiya wannan gwaggon muguwar yar jaraba ce wallahi!

"Wasu yammata ne suma sa'an mima ne bazasu wuce tsaran taba sai dai sun fita jiki ita kuma tafi su tsawo suka shigo dakin da gudu suka rungume ta suna oyoyo your welcome sister!
Ita dai tabi su da idanu dayar tace'nice to meet you sister!

Ganin bata jin meh suke cewa yasa kowacce shiga bathroom sukai alwala kowacce ta saki labulen saitin gadon ta tah tayar da sallah hakan yasa mima ta fahimta sune sauran masu dakin itama sallar tayi dukan su babu wanda ya tashi sai da yayi isha'i sannan suka saka Riga da wando wandon yadan wuce gwiwa sai rigar mai dan dogon hannu hula suka dora da alama kayan bacci ne suka saka!

Wata doguwar Riga suka bama mima ta saka da hula sannan suka kama hannun ta zuwa falo!

Kowa na gidan ya hallara sun hau dinning gaishe da mutanen tayi kamar yadda taga sauran sunyi wani mutum ne yai gyaran murya Alhamdulillah mima yau Allah ya maidoki cikin yan uwan ki kuma zaki cigaba da zamane anan tunda ita inna Allah yai mata rasuwa ni da kike gani suna na alh.Aliyu ni wan mahaifin kine uwar mu daya uban mu daya! Ni ana kira na Abba!

'Wannan ya nuna mom itace'mata tah ana kiran ta da mom wannan shine babban danmu sunan hassan ga husainin sa nan wa yannan matan sune, wannan shine Mutallaf! Shi Soja ne sai Sadiq sannan sai Samera tana gidan mijin ta sai wa'yannan Nana da Nina sune zasuyi aure nan da wata daya! Sai Mimi gata nan itace aka haife ku rana daya da ita! Yaran mu takwas.

"Sai wannan shine mahaifin ki wanda ya haife sa mejor Ahmad kenan Shi ana ce masa Daddy wannan kuma ya nuna mama itace mahaifiyar ki Dr.amina kwararriyar likita ce itace ta haife ke Jidda itace babbar yarsu tayi aure sai Muhsin gashi nan sai Nene wacce lokaci daya za'ai bikin su da Nina da Nana sai ke mima(sunan ki Aisha) sai Ma'ida gata nan wacce kika gani a tare da Mimi kanwar kice kinbata shekara guda! Sai auta Suhaib!

Wannan itace gwaggo itace mahaifiyar mu wato kakar ku kenan!
Dan haka ki saki jikin ki nan gidan kune!
To ta fada cikin sanyin murya!

Kai Mutallaf tunda Hutu kazo gobe in Allah yakaimu saika kaita school amata register da islamiyan su Mimi!
Cikin daurewa yace' to Abba amma shikam Sam baiso ace shi zai wannan kuchakar yarinyar ba jita wata banza da ita bakauyi ya kawai!

'A haka suka ci abinci aka tashi

Washe gari Mutallaf yana dakin mama yana breakfast mom ta shigo tare fa duban watch din hannun ta tace waikai wannan wanne irin wulaqanci ne haka kasan ance zaka kai mima school amma now getting to 11 baka fito ba!

Dan hade fuska yayi mom zanyi breakfast nefa please!

Wallahi bazaka yi shiba saika dawo wannan ai wulaqanci ne tashi ka fita kona saba maka get

out gata chan a balcony tana jiran ka!

Takaici ya cika sa dole ya fito fuskar nan tamkar ta namijin zaki! Sanye take cikin doguwar rigar material tasaka farar hijab fuskar nan ta tah duk ta zaneta da kwalliyar kwalli ji yayi kamar ya shakota a kule ya shiga mota ta shiga baya suka fice!

Ke saka hijab dinki ki goge wannan kwallin stupid kawai dake!
Ita kam tsoron sa take yi jikin ta na bari tasaka farin hijab dinta goge parking yayi yace' fito dan ubanki! Da sauri ta fito ya bude booth yace shiga nan dan bazaki zauna min a sit din mota ba ai sai kijamin abun kunya akaga ina yawo da gaja irin ki!

Karamin booth ne tashige dan haka ta takura ya rufe tare komawa yaja motar suka tafi a hankali yake tukin ya kunna wakar Soldier yana bi!!!!!

*Share$Comments*

_Mrs'Salihu Bamalli zeeabusafana_
_Momyn Sheikh Albany_

[9/4, 8:41 AM] Hayat: 🙆🙆 *RAYUWATA CE*🙆🙆

*Na*

*Khadeejah Sani (Journalist)*

*_🌈KAINUWA WRITERS✍🏼 ASSOCIATION_*🤝🏻
```{United we stand and succeed;Our ambition is to entertain & motivate the mind of readers}```

https://www.Facebook.com/kainuwawritersassociation

*Alhamdllh*
*Alhamdllh*
*Alhamdllh*
*Ina Taya dukkan yan,uwana musulimi murnar shigowar sabowar shekara, ya rabbi yadda muka shigota lafiya Allah yasa mufita daga cikinta lafiya ya Allah yabamu ikon aikata aikin Alkairi Allah kajikan magabatanmu Allah ka karemu da lafiya*
*Wannan shekara ta 1441 damukayi shigo Allah ya hadamu da dukkan Alkairi dake cikinta ka karemu daga sharrikan ciki kacikaman burikanmu Ameen*👏👏👏

🅿 *13 _ 14*

Daidai lokacin Dana zunduma ihu alokacinne yafara kokarin rabani da hijjabin dake jikina kuka nake Ina niyyar kwace jikina Amma Ina nakasa Saida yayi nasarar rabani da hijjab din tare da wulli dashi gefe ha kwanto kaina kuka nake iya karfina Ina kukarin kwacewa Amma nakasa don haka na barwa Allah komai,

Rigar dake jikina yafara kokarin yadda zai rabani da ita Amma yakasa don haka kawai ya yagata ganin akwai vest yasakashi Dona uban tsaki tare da fadin
"Kinbi kinsaka wasu riguna da yawa shegiya kawai" Yana fadar hakan Yana kokarin yagata Amma Ina taki yaguwa don ba,iri dayaneba yadin,

Kuka nake Ina kokarin kwatar kaina don ganin ya dakata Yana neman yadda zaiyi ya rabani da vest yasakani tashi cikin sauri zanyi waje kawai naji yajawoni nadawo kansa,
Ihu nakara saki daidai lokacin shikuma yazo wucewa Jin kukan mace cikin kango yasakashi kunna fitilar wayarshi Yana hasko cikin wajen ganin hasken da nayi yasakani kara dagewa nasaka wani sabon kukan Ina fadin
"Don girman Allah kuyi hakuri karku yimin komai Allah kakawomin dauki innata kizo ki ceceni nashiga uku" ainin wannan kukan yasakashi shigowa cikin wajen da gudu tare dayin kan Zaki dake Haye asamana aikuwa ganin yashigo da gudu yasakasu Musa barin wurin sukayi waje da gudu don dama suna wani daki acikin dakunan dake kangon zakima takanshi yafara niyyaryi aikuwa wannan mutumin Daya shigo Saida yaci nasarar kaimasa naushi afuska Nan yakubuce yayi waje,
```

Nikuwa kwance nake nakasa tashi don kuguna jinake kamar baya jikina dukda Babu abinda yayimin Amma zaman da yayi akaina yabani wuya sosai,
Juyowa yayi kaina tare da kallon gefe Daya yace
"Tashi kisaka hijjab dinki"
Kuka nakeyi nace
"Wallahi bazan iya tashiba bayana ciwo yakeyi kamar zai balle" Jin muryar datayi magana yasakashi karasowa cikin sauri Yana fadin

"Nafeesat Nafeesat kece meya kawoki nan mesukayi Miki please Nafeesat kibani amsa mesukayi Miki kuma suwaye wadan nandin?" Tambayar yakeyi cikin tashin hankali da firgici hijjab din ya dakkomin yazo yasakamin tare da daukata gabaki Daya fitowa yayi wurin Babu kowa don mutane Basu fiya wucewa tananba don haka yayi motarshi Dani da gudu Yana kara maimaitamin tambayoyin suwaye mesukayimin,

Banda kuka Babu abinda nakeyi harya sakani cikin motar shiga yayi sannan Yakima yashiga tare da tada mota,

Tuki yakeyi cike da rashin kwanciyar hankali tare kuma da tunanin abinda yakawoshi unguwar tasu Yama kasa tantancewa yasandai Babu abinda zaiyi dazu yazo kuma yadan juma awurinsu don haka yaketa tunanin abinda yasakashi zuwa unguwar tasu kuma ya ajiye motarshi yataho akafa,
Cikin tunanin barkatai harmuka karasa asibitin dake kusa da unguwar mu shiga yayi Nan naga anata karasowa wurinsa anamasa sannu da zuwa baiko amsaba yakaraso inda nake zaune don naji dama dama yabude tare da kallona yace" Zaki iyayin tafiyar?"

Daya kaina nayi alamar eh sannan nafito ahankali nake tafiya harmuka karasa ciki wani office yabude yace
"Shiga ciki inazuwa" shiga nayi Ina tunanin Daman wannan mutumin yadakkoni Allah yataimakeni dazo ya kwaceni ahannun wadan Nan mugayen datuni yanzu sungama ketamin haddina sun zubarmin da mutuncina na 'yamace hamdaoa nayi sannan nadora da fadin "shikuma yatashi yawani dakkoni kamar wata baby Sai wani rawarkai yakeyi....." Bude kofar da akayine yasakani nayi shiru shigowa yayi tare da sallama wata mata abayanshi Tana rike da kayan aikinsu na likita karasowa yayi ciki Yana fadin
"Baki zaunaba kenan Kika tsaya haka?" Shiru nayi Ina sunkuyar da kaina kasa juyawa yayi Yakima baking kofa yace
"Sister gatanan kifubamin ita sosai please kitanbayeta komai" Yana kaiwa Nan yayi waje,

Kallona tayi tare da murmushi tafara tambayata Ina Bata amsa Nan nafada mata Babu abinda sukayimin kawaidai bayana ke ciwo Amma yasaki Nan tace shikenan tafita zaune nake har yakara shigo namike nace
"Zantafi gida kar Innarmu taking shiru" magana nakeyi Amma kaina nakasa nakasa had a idanu dashi,

Kallona yakeyi cike da tausayi sannan yace "muje to" fita yayi nabi bayanshi,

Take muke Babu maiyiwa want magana harmukaje kofar gidanmu Sai lokacinma natuna da buhun wakena dakuma Mai dazan karba wurin maikantin layinmu Nan nafara hawaye naki fita Daga motar shirune yarats motar nawani lonaci sannan yace
"Yada kuka kuma meyafaru?"
"Waken da Innarmu ta aikeni siyowa yanacan nabarshi". Sai lokacinma yatuna yaga buhu awurin don haka yace
"Jeki gida nakawo Miki" to nace tare dayimasa godiya nasauka shiga fitowa yayi yace
"Kishiga gida in nadawo zanyi magana"to nace tare dayimasa godiya nashiga gida,

Ina shiga nasami Inna tsaye baking kofar soro tanata tunanin ina natsaya kukan dataga inayine yasakata fara jefomin tambayar,

Kasancewar bansaba boye mata komai nawaba yasaka nafara Bata labarin komai Daya faru har Muslim Daya taimakeni dakuma kaini asibitin da kawoni gida dayayi yanzu harma da dakkomin buhun waken Dana bari acan,
Salati kawai takeyi tare da fidda hawaye tace "nagodewa Allah Daya kawo wannan bawan Allah Daya taimakeni ya taimakeki yauda bansan yadda zanyiba aikuwa wannan awarar anbar yinta insha Allah baza,a karayi a Allah yabamu yadda yadda yadda,ayi gaskiya bazamu karayiba ahakura kawai munemi wata Sana,ar" tana kaiwa Nan tayi shiru donjin Ana kwada sallama Jin muryarshi yasa innarmu cew
"Jekice Masa yashigo" wucewa nayi na fada Masa don haka muka shigo tare,
Shimfida tabarma Innarmu tayi yazauna itakuma ta tsugunna agefe buhun waken nakai kitchen nashige daki,

Mahbub nasamu kwance don haka nakarasa tare d tabashi jinai jikin yakara zafi don haka natadashi don nabarshi magani,

Bangaransu Innarmu kuwa gaisawa sukayi tare da jajanta abinda yararu Nan Innarmu tayimasa godiya akan abinda yayimin tadora d cewa
"Ai tunda abin yazo da haka Sai ahakura da awarar dama tafadamin yadda sukayi d wadannan yaran tun kwanaki" Nan Innarmu tashiga bashi labarin yadda mukayi dakuma abinda najisu suna Fadi,

Bakaramin mamaki yayiba donjin nasanma wadanda sukayi yunkuri ketamin haddina don haka yace insha Allah bazai barsuba saiya bimin hikkina kuma arabani dasu don irin wadannan abin tsorone,

Nan suka Dade sunata fira Shima yace d Innarmu abaryin awarar adunga yimasa t dubu uku kullum zaidunga karbar ta dubu daya sauran kuma adunga sadaka da ita,

Sallama sukeyi zantafi daidai lokacin mahbub yafito ya tsugunna Yana kwara amai nikuma Ina rike dashi inamai sannu,

Saida yagama nagyara wurin Yakima gefe yakwanta don haka Muslim yakarasa wurinsa Yana dubashi fita yayi yace yanazuwa yadan juma awake sannan yadawo dauke d Leda kallona yayi Ina zaune ga hawaye afuska ganin yadda mahbub yaketsa wani mikewa Innarmu tana shafa Masa ruwa tacemin Suma yake don haka duk atsorace nake,

Jin muryarsa nayi yace "Inna akaishi inda zai kwanta zandaka mishi ruwa yadda zaifijin dadin jikin" to tace tashi tayi tashiga dakinmu tafara gyara gadon inda za,a dorashi,

Bayan tashinta ya kalleni yace
"Kekuma hawaye baya Miki wuyar zuba Naga alama, yanzu meye na kukan?"
Kallonshi nayi tare da kara matso wasu hawayen nace
"Uhm................

*Kuyi hakurin rashin jina kwana biyu, hakan yafarune dalilin rashin lafiyar danake fama dashi kwana biyu, kuyi hakuri yanzuma kokari nayi nayimuku wannan, please Ina bukatar addu,arku bisa wata Yar matsala data faru Dani please my fans I need your prayers*👏👏👏👏👏

*My lovely mom inamai kara tayaki Al,ajabin abinda yasameki Allah yakiyaye gaba Allah ya tsare my Mom da dukkan yan,uwa musulimi baki daya*😭😭😭😭😭

*By*

*Khadeejah (Ummu Fu,ad & Afnan)*
[9/7, 6:11 AM] Hayat: 🙆🙆 *RAYUWATA CE*🙆🙆

*Na*

*Khadeejah Sani (Journalist)*

*_🌈KAINUWA WRITERS✍🏼 ASSOCIATION_*🤝🏻

```{United we stand and succeed;Our ambition is to entertain & motivate the mind of readers}```

*Dedicated to Ayshat m zazzau*

https://www.Facebook.com/kainuwawritersassociation

🅿 *15 - 16*

"Uhm kana ganin yadda yakeyifa" wani hawayenne yazubo min nakara shareshi da hannuna,
Innarmu ce tafito tace
"Yawwa bari akaishi dakin saika saka mishi"
Mikewa yayi yace
"Bari nadaukeshi Nafeesat shigomin da kayan Nan" tashi nayi tsaye nabishi da kayan Innarmu tabiyo bayana itama,

Gadona danake kwanciya naji Innarmu tace anan za,a dorashi nandin kuwa aka sakashi aka daura Mai Kari ruwan sannan ya nunamin yadda zancire Masa idon ruwan yakare sannan yanuna min maganin nashi da yadda za,a bashi,

Innarmu tayimasa godiya sosai sannan yafita wajen na rakoshi tare dayi Masa godiya Nan yace Saida safe zaizo yaga jikin nashi,
Najuya ina niyyar komawa cikin gida yace
"Nafeesat" juyowa nayi tare da amsawa,
Karasowa yayi kusadani yace
"Kibani phone number naki saboda anjima naji yaya jikin nashi"
"Wallahi wayana babu sim" kallona yayi cike da mamaki Wai wayana Babu sim menake nufi to ahaka nake ruke da wayan Babu sim,
"Kamar yafa banganeba"
Murmushi nayi nace
"Bansaka sim bane da akabani wayar Amma zansaka insha Allah"
"Okay ga wannan wayar kiyi amfani dashi kafin goben nataho Miki da SIM card din" murmushi nayi nace
"A,a kabarshi kawai"
"Saboda me kikace haka?"
"Innarmu zatayimin fada"
"Okay yayi to kibani number din Innaryamu inyaso saina Kira anata naji"
Karba nayi narubuta Masa Sannan mukayi sallama,
```

Kulle gidan nayi nashiga nasami innarmu zaune kusada mahbub Nan nafada mata yakarbi number dinta zuwa anjima zaikira yaji ya jikin nashi Nan tace nadakko wayar narike awurina inya Kira muyi maganar to nace nadakko,

Kwance nake kusada mahbub Wanda ruwan da akasaka Mai harya kare nacire Masa bacci take hankali kwance nikuwa nakasa bacci tunani barkatai yayimin yawa fargabata tayadda zankara fita waje naje wani gurin mainisa don harga Allah tsoran fita nakeyi daga gidan su Musa sungama bani tsoro gaskiya,

Karar wayar Innarmu ce tafarkar Dani daga tunanin danakeyi Nan nafarka firgigit nadauki wayan bakuwar number ne don haka nagane shine ke Kira,

Saida takusan tsinkewa nadauka tare da karawa akunne nayi sallama,
Ajiyar zuciya yasauke sannan ya amsamin sallamata gaidashi nayi dukda dazu mungaisa ya amsa tare da tambayata jikin mahbub nace
"Jiki yayi sauki bacci yaketayi baima tashiba"
"Ayyah Allah yakara sauki"
"Ameen mungode Allah yasaka da Alkairi Allah yabiya"
"Irin wannan addu,a haka nagode sosai Amma banason yawan godiyar Nan kinji tayi yawa ai idon nayimiki Abu kamar nayiwa kainane" shiru nayi don banganeba meyake nufiba dorawa yayi da fadin,

"Tunda Allah yayi nadora idona akanki  Sai naji duk yan mata duniya basa burgni kece tauraruwa guda daya acikin su haskenki yana sa nasu ya dushashe hakika Allah yayi miki baiwar daba kowacce mace gareta ba, sai an laluba gaki da tarbiya, ilimi, ladabi, uwa uba kuma biyayya gana gaba dake, kinada wadatar zuciya, haka kuma tarbiyyar da aka doraki akanta itace kowanne namiji yake burin matarshi takasance da ita, sannan tadora yaranshi bisa kalar tarbiyyar da aka dorata agidansu, tunda nadora idona akanki nagane nayi dace mata tagari, nayi facen abokiyar rayuwa, Alhamdllh, Alhamdllh, Alhamdllh, Ina godiya ga Allah ne Daya bani damar sauke nauyin dake cikin zuciyata na tsayin watanni masu yawa, inaso kiyiwa maganata kyakyawar fahimta kuma kifadamin abinda ke ranki karki boyemin komai please my baby kiduba maganar Dan marayan Nan, kifadamin abinda kikeji game dani"

Shiru nayi Jin kalar kalaman dayake antayomin Yama sakani jikina dukkanshi ya mutu Baki Daya nama kasa Koda motsin kirki kuma narasa menake ciki farin cikine kokuwa akasin hakanne,

Cikin tunanin danakene naji yakara magana yace
"Kiyimin magana please kozanji sanyi cikin raina, kifadamin ko menene duk abinda yake zuciuarki inasonji my baby Fadi wani abun"

Gyara kwanciyata nayi sannan nafara magana cikin sanyin murya kamar banason magana

nace

"Nagode da wannan yabon dakayimin kuma agaskiya naji dadi sosai Allah yabiyaka da mafificin Alkairi, Abu nagaba kuma naso ace kafadamin wannan maganar tunkafin lokaci yakure mana, Amma saidai baka fadaba har lokaci hakure Mana don ayanzu bani da damar amsar soyayyarka saboda......" Katseni yayi cikin sauri yana fadin

"Saboda me kina nufin kice kin mallakawa wani zuciyar Dana Dade Ina tunanin tazama mallakina don Allah karkicemin haka wallahi Ina kaunarki bazan iya rayuwa Mai dadiba inba tare dakeba please karkiyimin haka" yakarasa maganar cikin sanyin murya,

Bakaramin tausayi Yabani ba kuma Nima kaina naji tausayin kaina don ganin nasami maimin so irin Wanda bana tunani gashi lokaci yakuremin ajiyar zuciya nasauke nace

"Yau kwana biyu kenan babana wato yayan babana yakirani da maganar aure kuma yafadamin zai hadani da yaronsa aure nanba da dadewaba kojiya yazo gidanmu sunyi maganar da Innarmu don haka inamai baka hakuri kuma inaso kasani kasaka aranka ni Nafeesat Ina sonka Ina kaunarka saidai banida yadda zanyine da bazantaba aurar waniba inbakaiba, kayi hakuri nagode da kalar soyayyarka gareni" inafadar haka nakashe wayar tare da fashewa da kuka,

Bangarenshi Shima kukan yakeyi kamar wani karamin yaro azuciyar ya kudurce bazai iya rayuwa da kuwaba Sai ita Amma ya akayi akarigashi akayimasa irin wannan shigar Allah yadafamin abinda yake maimaitawa kenan ganin dayayi Babu wata mafita kawai yatashi ya dauro alwallah yafara fadawa Mai kowa Mai komai,

Bangarena Nima hakance tafaru Dana kasa bacci natashi nafara salloli.

*By*

*Khadeejah (Ummu Fu,ad & Afnan)*

[9/8, 12:47 AM] Hayat: 🙆🙆 *RAYUWATA CE* 🙆🙆

*Na*

*Khadeejah Sani (Journalist)*

*🌈KAINUWA WRITERS✍🏼 ASSOCIATION*🤝🏼
```{United we stand and succeed;Our ambition is to entertain & motivate the mind of readers}```

https://www.Facebook.com/kainuwawritersassociation

🅿 *17 - 18*

Washegari da safe muntashi jikin mahbub dasauki sosai,
Hakan bakaramin dadi yayi manaba saidai Babu kwari jikin Yana kwance duk yarame kamar aanda yayi jinyar watanni,

Nagama duk aiyukana dazanyi nayi gyaran gida nahada Mana breakfast dafaman tea nayi saikuma taliya da manja dayaji (🤪 kwakelenki zazzau) dakkosu nayi nakawo Mana dakinmu na ajiye,

Wanka nashiga nafito nasami Innarmu zaune zata hadawa mahbub tea din don harda Madara aka siyamasa tunda bashida lafiya ballalai bane ya iya cin taliyarba,

Saida nagama shiryawa sannan nadawo falon nazauna tare da daukar cup zandibi nawa nasha kwankwasa kofar gidanmu akayi don haka natashi naje don nabude hijjab nasaka tunda bansan ko wayeba,

Ina budewa naci Karo dashi tsaye Yana murmushi fuskarshi ta Kara kyau ajiyar zuciya muka sauke atare sannan nayi saurin dauke kaina Ina fadin
"Inakwana"
Murmushi yakarayi yace
"Lafiya kalau yajikin mahbub?"

"Dasauki bara nafadawa Inna" inafada najuya cikin gidan,

"Innarmu ga wannan mutumin yazo duba mahbub" kallo tabini dashi saikuma tace
"Waye kuma wannan mutumin banason shashancifa?"

Murmushi nayi nace. "okay Muslim zance mantawa nayi" hararata tayi sannan tace yashigo tafada tare da saka hijjab dinta,

Saminsa nayi tsaye jikin motarsa Nan nace Masa yashigo,

Shigowa mukayi nice agaba Yana biye Dani abaya har muka karaso dakin,
```

Zama yayi a kasa tare da tankwashe kafa Yana gaida Innarmu nidai cikin dakin nashige don kunyarsa nakeji,

Bayan sungaisa yake tambayarta yamai jiki tace

"Wallahi jiki Alhamdllh kaganshi yanashan tea saidai rashin karfin jikin danaga baya iyazama sosai saidai kwanciya"

"Alhamdllh to Allah yakara sauki ai yanzuma sakamasa za,a karayi saikiga yasami karfin jikin insha Allah"

"To madallah nagode Allah yasaka da Alkairi yabiya da gidan aljanna nagode Dan nan nagode badan kaiba dabansan Yaya zanyiba jiya kila da saidai ya mutu bamu da yadda zamuyi sannan ga taimakon dakayimana na wadancan yan iskan datuni sungama ketamana haddi don idon sukayiwa Nafisa want abun kamar nisuka yiwa Allah yasaka da Alkairi" takarasa maganar da kuka,

"Inna Babu komi wallahi ai anzama Daya Allah yakiyaye gaba kawaidai Sai akiyaye saboda irin wadan Nan mutanan basuda mutunci kwata kwata kuma insha Allah za,asan abinyi akansu baza,a kyakesu hakaba"

Fira sukeyi inadaga daki inajinsu banyi yunkurin fitowaba Jin muryar Innarmu nayi ta kwadamin Kira tace

"Nafisa Wai Inace kece Kika zuba ruwan shayin Nan Amma kikawani shige daki kamar garar kunya bazakizo kidaukaba Kisha karya huce"

Tashi nayi nafara leken falon zaune yake inda nabarshi bisa darduma fitowa nayi gashi kofin Yana kusadashi don haka nakarasa cikin sanda tare da dauka Ina niyyar komawa daki nayi Innarmu tace

"Kizo kizubawa yarona Shima Mana kinata wani sanda ohh ni narasa meke damunki yau dinan tunda safe kiketa wani lakwai lakwai" komawa nayi nadauki cup nafita waje nawanke nadawo nazubamai tare da mikamai,

Shikuwa zaune yake idonsa nakaina yazubamin ido Sai wani lumshe idanu yakeyi Yana kara kallona,

Mikamai nayi yakarba tare da yimin sannu cikin siririyar murya wadda bana zaton ko innarmu taji maganar da yayimin,

Mikewa nayi zankoma takara cewa

"Waike komai sainace Miki kiyi toki zubamai taliyar yaci saidai bansaniba ko yanacin taliya da manja" takarasa fada Tana kallonshi,

Murmushi nan nashi yayi yace

"Inacinta Inna Amma yanzudai nakoshi wallahi wannan ma ya Isa nagode"

"Ohh Dana Kodai kaima ta yayansu Shima yace bayacin taliya da Mai shiyasa indai Yana Nan bamayi" gyara zama yayi yace

"Wai nikuwa Inna a Ina yake aikene naji mahbub yacemin Wai Yana Abuja hakane kuwa"

Murmushi tayi tace "bawani aiki yakeba yadaiyi karatun yayi degree Amma baisami aikiba shiyasa yake zuwa can irindai yan bige bigen nan nasamari yakeyi acan"
"Amma Inna maizai Hana yadawo yanemi aiki anan garin Ina ganin kamar zaifi zuwa can din"
"Umm banki tatakaba kasan yanzu aiki akasarnan yazama abinda nazama saikana da hanya mukuma wallahi bamu da wata hanya dazamu nema tanan shiyasama danaga yafara nema yanazaune nace yahakura yanemi wani aikin zaifi Masa kawai"

"Hakane gaskiya yanzu abun yazama abinda yazama Amma inason kisakashi yadawo insha Allah za,a Sami aikin yadawo cikin satin Nan idon da dama insha Allah za,asan yadda za,ayi"

"To insha Allah zanfada masa yau dinnan mungode dana Allah yabiyaka"
Ameen yace Yana kurbar ruwan tea din,
Nidai inadaga daki har lokacin Daya tashi tafiya sukayi sallama da Inna kirana tayi tabani wayarshi Daya manta tace nakaimai,

Fitowa nayi nasameshi zaune saman motarshi karasawa nayi nace
"Gashi kamance wayanka" dariya yayi yace
"Wallahi ina sane nabarta nasandai kece Zaki kawomin ai" murmushi nayi kawai yadora da fadin
"Yanzuma zandawo ai zanje nadakko drip nadawo, kuma dama nace zamuhadu shine jiya Kika kashemin way to?" Rufe fuskata nayi da tafin hannuna Ina dariya.

*By*

*Khadeejah (Ummu Fu,ad & Afnan)*
[9/8, 8:57 AM] Hayat: *🙆🙆RAYUWATA CE*🙆🙆

*Na*

*Khadeejah Sani (Journalist)*

*🌈KAINUWA WRITERS✍🏼 ASSOCIATION*🤝🏻
```{United we stand and succeed;Our ambition is to entertain & motivate the mind of readers}```

https://www.Facebook.com/kainuwawritersassociation
```

*Saudaukarwa gareki mamana Allah yajamin da ranki yakara girma*

*🅿19 _ 20*

"Ohh ni Nafeesat kunya har irin haka, bude fuskar muyi magana ta fahimta" budewa nayi tare da sunkuyar da kaina yafara magana yace

"Ajiya kinfadamin wata magana data tadamin hankalina tasakani tsaka Mai wuya nashiga fargaba danaji kincemin Wai anbadaki ga yayanki kinsakani nakasa bacci wallahi Nafeesat yadda naga ranar jiya haka naga darenta please kiyimin bayanin dazan gane"

Shiru nayi zuwa wasu mintuna nace

"Abinda nafada maka gaskiyane yayan abbanmu yahadani da yaronsa Adam" shirune yaratsa wurin zuwa wasu lokuta sannan yace

"Nafeesat inaji ajikina bazan taba rasakiba kuma insha Allah saina aureki inaso kifadamin tsakaninki da Allah kinasona kokuwa bakisona"

Gyara tsayiwata nayi nafara fadin

"Ina sonka haka kuma Ina kaunarka saidai bansan da hakaba sai jiya danaji kace kanasona alokacinne nasan cewar inasonka domin najima Ina tunanin yadda zanyi nasaka afasa aurena da Yaya saidai nasan hakan bamai yiwuwa bane don tunda baba yayi wannan maganar Babu fashi Sai anyi don haka nake Kara bawa kaina dakumakai hakurin rashin juna damukayi Allah yazabaman abinda yafi Alkairi arayuwa"

"Ameen ya Allah Amma inaso kiyimin alfarmar zandunga kiranki muna gaisawa hakan zaikawomin sauki cikin raina"

"Insha Allah nayimaka Alkairi zandunga dagawa muna gaisawa"

Ciro sim yayi daga aljihunshi yamikomin Yana fadin

"Ga alkawarin danayi Miki"karba nayi Ina godiya,

Sallama mukayi yatafi zaije yadakko yadawo,

****************

Agurguje please,

Haka muka Saba kamarme dashi banason abinda zai batamai Rai kuma kusan kullum saimun hadu idon yazo daukar awara Innarmu harta gane datashareni Amma daga baya tayimin magana banboye mata komaiba Saida nafada mata Nan tafara yimin fadan meyasa banfada Masa anbadaniba nace nafada Masa cewa yayi mundinga gaisawa kuma naga Inna gaisawa

bawani abuba ai Babu komi,
Fada tashiga yimin tace karna Kara way dashi kuma Shima zatayi Masa magana,

Yau Yaya yadawo don haka murna kamar me awurinmu nida mahbub, ya iso lafiya Sai firar yaushe gamo mujeyi,

Aranar da yamma suka hadu da Muslim kuma aranar Innarmu tasakashi yayi Muslim magana akan maganarmu Nan yanuna Mai ai komai na Allah ne Ido Allah yayi shine mijina zan aureshi idon kuma Allah yayi bashine shikenan haka Allah yayi,
Sunshigo cikin gida sunata fira Idon kagansu saikace sunsaba sosai,
Nan sukarayin maganar da Innarmu tace yayi hakuri da ace tanada wata yarinyar dasaita bashi Amma yayi hakuri tunda babana yariga yayimin miji Allah yabashi wadda tafini,
Inadaga daki inata kuka Shima dauriya kawai yakeyi Yana yake Wanda hausawa kecewa yafi kuka ciwo,

Haka yatashi suka fita gwaiwa asage suna fita sukafara magana akan aiki tambayarshi yayi meya karanta Nan yafada Masa yakaranci medicin ne aikuwa yaji Dadin hakan don haka yace yafara zuwa asibitinshi ranar Monday,
Cikin murna yazo yake fada Mana natayashi murna sosai Nan yafara Nemo takardunshi don kaimasa,

Duk jikina yamutu kwance nake adaki nikadai inata tunanin tundazu yatafi Amma shiru baikiraniba don haka nadakko wayar nafara neman number dinsa Saida ta katse Ina niyyar Kara Kira yakirani dagawa nayi cikin sauri kawai nafashe Masa da kuka,

Hankalinsa atashe yake tambayata menene kasa magana nayi don nikaina bansan menene yasakani kukaba don haka narasa amsar bayarwa naketa kukana,
Nisawa yayi yace
"Kiyi hakuri wannan Yana Daya daga cikin kaddarar mu don Allah kidaina kukan Nan idon baso kikeyi nayiba Nima, inaso kisani wallahi dauriya kawai nakeyi saboda ayanzu haka zuciyata kamar zata fashe haka nakejinta please my baby kidena kukan Nan haka" yakarasa cikin raunin murya,
Shiru nayi Amma nakasa magana hakan yasa yayita yimin fada akan yadda yaga natada hankalina komai na Allah ne zai iya yiwuwa Sai and daura auren afara da Yaya ayi dashi,
Wannan kalma tayi masifar yimin Dadi don haka nasaki Raina mukasha soyayyarmu,

**************

Alhamdllh yaya yafara aiki asa,a don bakaramin kudi take biyanshiba gashi yanzu abincin gidanmu yadauke Mana Baki Daya,

Yaya da nafisa sunatashan soyayyarsu kamar baza,a mutu ba,
Don sunkara shakuwa sosai duk bayan kwana biyu saiyaje gidan gashi suna mutuncina da yayansu nafisan,
Nikuwa dama tabon Dana ganshi tun kawoni gida dayayi baiko Kara lekowaba ko zuwan dayake bayan wata wata gaida Innarmu yadaina, nace najawa Inna iatama nata kason,

Ana hakane kuma aka saka ranar aurenmu watanni biyu kawai aikuwa ranar nayi kuka mara misali,
hatta Muslim Saida yashiga tashin hankali dajin yadda nake kuka don haka yace bariyazo gida kawai yakashe wayar,
Yana zuwa yakirani yace Yana waje, don haka naboye hijjab Dina aciki nafito inata sanda Innarmu Tana daki aikuwa nayi saurin wucewa asoro nasaka hijjab din nafita nasameshi tsaye jikin mota Ina ganinshi nasaki sabon kuka hankalinsa tashe Yama rasa abinda zai fadamin don haka yace
"Shiga mota muyi magana" tunda nake bantaba shiga motarshi munyi zanceba Sai yau"
Shiga nayi nazauna Shima yashigo,
Kuka kawai nakeyi nama kasa magana,
Yarasa mezaice kawai saijina nayi ajikinsa yajawoni Yana shafa bayana alamar rarrashi dafarko natsorata Amma saina tuna Wanda zan aura don haka kawai nakara kwanciya ajikinasa Ina kuka,
Yadda nakeji akansa banki komaima yashiga tsakanina dashiba da nakarawa wani katon kaina kafiya gwara nasan naje ayadda baya tunani kodan ya sakeni,

Mundauki lokaci haka sannan naji yafara magana yace
"Haba Nafeesat yakike so nayi da Raina da kukan naki zanji kokuma da rabamu da ake kokarin yi kinsan yadda zuciyata take Kuna kuwa dajin yadda kike wannan kukan, please kisassauta min kiyi shiru naji da Abu Daya Mana" Jin yadda muryarshi take rawa yasakani dagowa tare da shafa fuskarshi nace
"Jinake kamar nakashe kaina dama ace idon mutum yakashe kansa Babu laifi gurin Allah wallahi dayau babu abinda zaisa bankashe kainaba, zuciyata Kuna take yimin radadi take yimin narasa yadda zanyi da wannan musibar datake tunkaroni aurena da wancan mutumin wallahi Babu Alkairi acikinsa dama aca Allah yakarbi rayuwata nahuta da wannan abun Koda yake *RAYUWATA CE* haka Babu yadda zanyi, yanzu kana kallo wani yarabani dakai kana gani zaishiga tsakaninmu nashiga uku no Nafeesat anrabani da farin cikina Nina Sani narasa farin ciki har karshen rayuwata shikenan nayi sallama da farin ciki narasaka har abada" nafada tare da komawa jikinsa Ina sakin wani kukan,

Shima kukan yafara cikinmu Babu Mai lallashin wani daga ciki Saida mukayi Mai isarmu sannan muka hakuri fira muka fara sama sama har want lokaci sannan nace
"Bari nakoma gida Innarmu batasan nafitoba" fitowa mukayi daga motar,

Juyowar dazanyi donjin motsin mutum bayana wazan gani ba yayaba Yana wani muzurai,
Kallonshi nayi najuya nakkali Muslim dake niyyar zagayowa kusa Dani Saida yakaraso sannan na nuna Masa Yaya nace
"Shine Wanda aka hadani dashi" kallon kallon akeyi tsakanin Yaya da Muslim,
Don nakabashi haushi kawai saina juya na fuskanci Muslim nace
"My love Sai munyi waya zanje nayi aiki". Shikuwa Jin kalmar Dana kirashi da ita yasakashi sakin wani murmushi yace
"To baby kikulamin da kankifa sosai Allah yayi Miki Albarka"
"Ameen my dear saina jika" nafada Ina dagamasa hannu nashige gida Shima mota yashige yayi gaba abinda,
Yaya dake tsaye kamar andasashi awurin,
Juyawa yayi yafasa shigowa gidan,
Gida yakoma yasami mama zaune afalo binsa tayi da kallo tace
"Wai meke damunkane Adam kana nufin harkaje kadawo?"

Zama yayi tare da had Rai alamar ranshi abace take yace
"Mama don Allah kifadawa baba afasa auren Nan yarinyar Nan bakaramar Yar iska bace yanzufa danaje samunta nayi acikin motar wani mutumi sunata aikata iskancinsu bansan mesukeyiba Ina niyyar shiga gidan Sai gasu sunfito suna fitowa naganta kwance jikinshi Sai kiss yake sakar mata itakuma tanata wani Kara narke Masa ajiki Tana wani fadin my love my dear, haba mama narasa wadda zan aura Sai karuwa nidai gaskiya kuyi hakuri abar hadin Nan nayi alkawarin zansamo wata ahada auren lokaci Daya danasu nafisa" yakarasa fada cikin hawaye,

Nikuwa nace ohhh ni deejah su Yaya harda karya😁🤣

Mama Saida tagama jinsa sannan tace
"Naji abinda kace Amma yadda Bata zama doleba don haka kaikasan wannan baniba yarinyar dako kula samari batayo zakawanizo kashiya mata karya har haka wallahi kabani mamaki Allah yashiryeka, katashi kabani wuri nidai nafada maka duk sati kadunga zuwa inkuwa bakajeba banyafeba wallahi" Tana kaiwa Nan tashige daki,

Mikewa yayi cikin fishi yakoma dakinsa,
Takaici goma da ashirin ya Hadar Masa yazauna yagama tsara magana Amma mama Bata yaddaba gashi kuma ita yarinyar tagama rainashi gabaki Daya don haka kanshima yakulle yarasa mezaiyi tunani yalula kawai yasaki wata dariya tare da mikewa yashiga toilet yayo wanna yafara kwalliya don dama daga office yawuce can Amma yanzu zai koma don yanuna mata Shima bashida mutunci.

*Inayiwa dukkan yan,uwana musulimi barka da juma,a fatan Allah ya hadamu da alkairan

cikinta Ameen*

*By*

*Khadeejah (Ummu Fu,ad & Afnan)*

[9/11, 7:13 AM] Hayat: *🙆🙆 RAYUWATA CE*🙆🙆

*Na*

*Khadeejah Sani (Journalist)*

*🌈KAINUWA WRITERS✍🏼 ASSOCIATION*🤝🏻
```{United we stand and succeed;Our ambition is to entertain & motivate the mind of readers}```

https://www.Facebook.com/kainuwawritersassociation

*Sadaukarwa gareku masoyana*

*Fatima g Abdullahi*

*Rukayyah Abubakar shanono*

*Fareeda Auwal*

*My lovely Mom samira haroun*

*My lovely anty fauxia Mai agogo*

*Anty Fauxia Yar,amana*

*Ayshat Shareef*
```

*Nafeesat feenah*

*Ayshat m zazzau*

*Da dukkan sauran masoyana wadanda banma anbaci sunansuba duk Kuna raina Allah yabar kauna*❤🤝

*🅿23 _ 24*

Shiru yayi zuwa wani lokaci sannan yace
"My love meyasa kikemasa rashin kunya Kinga Babu Dadi abinda kikayi Masa dakinsa I Daya zageni kiyi shiru banason abinda zai dunga batamiki Rai kiyi hakuri da duk kalar rayuwar dazaki tsinci kanki acikinta Ina Kara tunatar dake kiyi hakuri ki rungumeta yadda tazomiki please my love kiyita yimana addu,a nasan duk rintsi addu,armu bazata taba faduwaba, duk abinda yace dake kibarshi kawai nasan bazai yimiki komaiba kawaidai yafadane saboda bacin ran da Kika sakashi" nasiha yashiga yimin Mai ratsa jiki harna daina kukan sannan yace nadaukar masa alkawarin nadaina yimasa rashin kunya ko bayan aurenmu shiru nayi sannan nace
"Sweetheart bazan iya daukar make wannan alkawarin ba zan,iya yin hakuri da duk abinda zaimin Amma wallahi bazan iya hakuriba idon naji yazageka Sai inda maina yakare Kuma saidai ya kasheni Amma bazan barshi yadunga cimaka mutuncina wallahi bazan juraba sweetheart please karka sakani nayi alkawarin abinda bazan cikaba" shiru yayi Yama rasa abinda zaicemin hakan yasa nafara yimasa wani labarin don yamanta da waccen maganar,

******************

Alhamdllh komai ya kammala angama gyaran gidanmu don hardakin Innarmu Saida akayimata pants sannan aka sakamata sabuwar TV bango hakama dakin amarya aka sakamata wannan Kuma duk Muslim ne yasiyo yakawo guda uku tawa Daya data Innarmu dakuma ta Yaya Sai fridge nawa Dana Innarmu nikuma yakaramin da sauran kayayyakin anfani irinsu gass oven dasauran kayan anfani irindai manyan Nan namasu kudi haka aka hadamin kayan kitchen sosai Kuma ankai lefan Yaya akwatina shida Kaya sunyi kyau,
Sai Muslim Daya bawa Yaya kyautar dubu dari uku yace yayi amfani dashi,
Yau saura kwana biyar daurin aure Kuma rabona danaga Yaya Adam tun ranar da mukayi fadan Nan dashi baizo yayimin maganaba akan abinda za,ayi na game da biki nikuwa Daman banyi niyyar yin komaiba don bazan batawa kaina lokaciba,

Yaune Kuma za,a kawo kayan lefena don haka su Innarmu da kawayenta su biyu makotanmu mama da anty larai sunzo tayata aikin abinda za,a bawa yan kawo lefe,

Kwance nake adaki Ina tunanin yau bamuyi waya da sweetheart dinaba kwata kwata Kuma nakirashi bansamuba don haka Raina duk abace yake narasa Yaya zanyi,
Ina haka Yaya yashigo tare da mikomin envelope yace
"Gashi Nan inji Muslim yace nakawo miki" Yana bani yajuya yayi waje,
Tashi nayi cikin sauri tare da budewa nafara dubawa takardace aciki don haka na ajiye nafara dubawa,
Wasikace aciki kamar haka,

*Assalamu Alaikum masoyiyata Ina fatan kina cikin koshin lafiya, Allah yasa haka Amin, inaso kiyi hakuri da sakon dazakiji acikin wannan takardar please banason yawan kuka don Allah karkiyi kuka dayawa nasan koda nace karkiyi kuka saikinyi Amma don Allah karkiyi Wanda zai illataminke, inaso kisani kekadai nakeso Kuma kekadai nake kauna bazan taba son wata maceba kamar yadda nasaki naso ace natsaya na halarci daurin aurenki amma bazan iyaba, tunda naga maganar aurenki da gaskene Kuma naga bikin naki za,ayi nafara neman makaranta a Dubai don nakoma can da zama zanyi karatu na tsayin shekara biyu da rabi Ina rokon Allah yaciremin sonki acikin zuciyata don Babu kyau son matar wani alokacin da Kika zama matar aure zankara kokarin cireki acikin Raina dukda nasan abune Mai wahala yin hakan Amma zan gwada Ina rokonki kema kiyi duk yadda zakiyi kicireni aranki, sannan ga sakonan nabada akawo Miki kudine ki ajiyeshi awurinki kidungayin want amfani sannan account dinki Dana bude Miki kwanaki Dana fada Miki gashinan nasaka Miki ATM card din aciki akwai kudi wanda zaki iyacira kiyi amfani dasu koda bukatar hakan tataso miki, wancan nakin sun kare, sannan maganar pin nasan kinsani date of birth dinkine, Allah yabaku zaman lafiya mai dorewa, nasan alokacin da wannan sakon zai sameki nayi Miki nisa Kuma kema haka kinmin nisa Allah yahadamu da alkairinsa ameen, namanta bankara fada mikiba kidage kidaure kiyiwa mijinki biyayya, uwa uba Kuma hakuri Mai hakuri Yana tare da nasara Allah yabaki juriyar yinsa nikuma yabani hakurin rashinka my love kihuta lafiya*

Kuka nakeyi Wanda har numfashina ke daukewa saboda kukan yaci karfina dajin wannan maganar ta Muslim in Banda innalillahi wa,Inna ilaihirraji,un Babu abinda nake maimaitawa.

Kallon takardar nake nama kasa cigaba da kuka ga kirjina Yana wani irin zafi kwantawa nayi awurin tare da rungume takardar jinake kamar shine ajikina saboda kanshin turarenshi dake tashi ajiki,

Wani sabon kukanne yakara kwacemin kuka nake kamar wacce akayiwa mutuwa,
Ina haka acikin daki har akazo aka kawo kayan bansaniba tunda inacikin dakin da Yaya yakoma cikinsa,
Duk mutanen dasuka kawo kayan suntafi daga Innarmu Sai mahbub da yaya daya dawo alokacin,

Innarmu ce take tambayar Ina nake Yaya yace Ina cikin dakin shigowa tayi tasameni kwance ga zazzafan zazzabi yarufeni Sai rawar sanyi nakeyi ga hawaye nabin fuskata hakan yatada

mata hankali zaunawa tayi kusa dani tare da shafamin fuska zafi taji jikina yayi hakan yasa tafara tambayata
"daman baki lafiya shine kiketa kuka bazakiyi maganaba?".

*Comment*
*&*
*Share*

*By*

*Khadeejah (Ummu Fu,ad & Afnan)*
[9/11, 7:15 AM] Hayat: *🙆🙆RAYUWATA CE*🙆🙆

*Na*

*Khadeejah Sani (Journalist)*

*🌈KAINUWA WRITERS✍🏼 ASSOCIATION*🤝🏼
```{United we stand and succeed;Our ambition is to entertain & motivate the mind of readers}```

https://www.Facebook.com/kainuwawritersassociation

*🅿21 _ 22*

Saida yagama shiryawa sannan yafito cikin shiri masallaci yafara zuwa Saida yayi sallar magrib sannan yawuto gidanmu,

Zaune muke atsakar gida Yaya nayiwa Innarmu bayanin yadda sukayi da baba yace
"Innarmu babane dazu yakirani yace idon natshi daga aiki nabiya zamuyi magana shine naje saiyace Wai yasandai bansiya filiba shine yake tambayata a Ina zamu zauna nace Masa zankama hayane shine yace a,a baiyarda da kama hayaba tunda ga gidan Nan kawai nadanyi gyare gyarena muzauna aciki basaina kama hayaba idon Allah ya horemin saina Gina gidana, nace Masa zanfada Miki sannan naji yadda kikace" shiru yayi Yana jiran amsar dazata bashi Sai tace
"Kaito ya kake gani Khalil nidai Ina tunanin zama gida dayan Nan kamar zan takuraku nake gani"
"Habadai Innarmu wanne irin takura kuma wallahi Babu wani takura kawaidai inata tunanin
```

yadda zanyi tsarin gidan don gaskiya saidai arusheshi agyarashi"
"To kaji irin abun naka yanzu wannan gidan meza,a rush aciki?"
"Innarmu amaidashi ginin zamani"
Shiru tayi tana kallon gidan nikuwa nakara gyara zama nace
"Yaya kasan yadda zakayi kawai" girgiza Kai yayi batare dayayi maganaba naci gaba da fadin
"Kawai abinda zakayi ahade maka dakinmu danaka da wancan karamin dakin yazama falo babba da daki aciki Sai kitchen Sai bandaki acikin can dakin saikuma ayi maka karamin daki aciki kaga shikenan wallahi wannan tsarin yayi ita kuma Innarmu abarmata dakin Abba da wancan karamin dakin na jikinsa saikuma kitchen dincan tunda akwai toiletacikin dakunan kaga anhuta" tafi yayi Yana washer Baki yace
"Wow my lovely sister kinkawo shawara shiyasafa nake sonki saboda basirarki nagode Miki sister nah, Innarmu kinji yadda aka tsara yayi?"

Murmushi tayi tace "yayi sosai Sai asan abinyi kagadai lokaci kurewa yake shiyasafa nakeso kayi kokari kabayar da cikon kudin daza,a karasa had a kayan lefan Nan saboda akaisu da wuri Kota sami dinki da wuri"
"To Innarmu abarsu haka Mana ai sunyi"
"A,a Basu isaba gaskiya"
Langabe Kai yayi yace "atausayawa marayan Allah please Innarmu kudi basa zaunatmin yanzu" saurin saka Baki nayi nace
"Wallahi Yaya kabarsu haka ai sun Isa wayasan su kalar kayan dazasu kawomin ma ai........"
Dokemin bakin da Innarmu tayine yasakani yin shiru batare Dana gama fadar abinda zanceba nafara turo Baki kamar zanyi kuka,
Kallon Yaya tayi tace "nadai fada maka kuma yanzu yaushe za,a fara aikin"
"Gobema Sai afara insha Allah saiku kwashe kayanku Nima zankwashe nakoma wancan dakin"
"To shikenan yanzu munkoma daki Daya da yaran Nan kenan"
"Saidai ayi haka Innarmu zuwa nadan lokacine ai ni ana gamawa zankoma da kayana can"
"A,a bazai yuwuba Sai tatare sannan saikuma kakoma katsare musu dakin insukazo jerefa ayi Yaya da shirginka kenan?"
"Innarmu ai akaramin dakin zansakasu kawai nakulle Kinga shikenan"
"A,a baza,ayi hakaba kill zasu iya zuba wani abun anan"
Yana niyyar yin magana mukaji sallamar Yaya shigowa yayi Nan suka gaisa da Innarmu yazauna kusa da Yaya suka fara fira Innarmu dai tashi tayi tashige dakinta nikuwa zamana nayi saima daukar wayata danayi nafara kiran Muslim Saida takatse bai dagaba saigashi ya biyoni tashi nayi nabar wurin don kar Yaya yajini Amma badan hakaba da agabanshi zanyi wayarma Ina shiga daki muka farashan soyayyarmu inata faman Masa shagwaba shikuwa Sai biyeni yakeyi,

Ina cikin haka akayi Kiran sallah don haka mukayi sallama nashiga bandakin dake cikin dakin don nayi alwallah,
Bayan na idar da sallah nazauna Ina duba Tex message din da Muslim yayimin,
Murmushi nakeyi Ina karantawa Kiran da Yaya yakeminne yasakani ajieye wayar nafito da

hijjab din dake jikina nasameshi tsaye yace
"Kije Adam najiranki awaje" Bata fuska nayi nafita Ina kunkuni don arayuwata wannan mutumin na tsaneshi,
Tsaye nasameshi gaban motarshi nima waje nasamu nesa dashi natsaya don nayi alkawarin bazan karasa canba don gulma shine zaiwani ajiye mota a inda yaga Muslim yana ajiyewa saboda gasa aidai tashi tafi tashi kyau dama tsada ni ko kallon wannan akwalar motar tashi banason nayi mota sai dan,iskan karar tsiya kamar antada injin nika,
Tsaye nake Ina kalle kallen layinmu yadda yayi tsit dashi kamar Babu mutane,
Saida mukayi kimanin mintina sunkai ashirin sannan yamatso kusa Dani tare da fara magana yace
"Ke Yar iska ko mara mutunci shine Zaki fito kiwani tsaya anan bazaki matsoba ko?" Kallonshi nayi sama da kasa nakauda kaina gefe guda kawai cigaba yayi da magana yace
"Wato harni Zaki nunawa kin Isa kuma kinunamin karuwancin danaji ance kinayi yin kikeyi shine harda shiga cikin mota akofar gidan nakuma saikinyi iskanci ko? To inaso kisani bazan dauki wannan raininba tunda za,a likamin ke to dole kibi umarni na kibi abinda nakeso karna Kara ganinki da wannan Dan iskan yaron......."
Cikin sauri na daga Masa hannu tare da fadin
"Karka Kara cemasa dan isaka gaskiya banason Bata suna mutum Mai mutunci da hankali ga ilimi da nutsuwa sannan zaka dunga fadar kowacce kalma akansa inaso kasani zan iya jure kowacce magana Amma Banda zaginsa don wallahi soyayyar danake Masa bazata taba barin awula kantashiba abanza inaji bandauki matakiba don haka kagyara bakinka gaskiya" Ina kaiwa Nan nayi shiru kallona yakeyi Saida ya nisa sannan yake
"Nikike fadawa wadanan maganganun akan wancan jakin mutumin dan iska jahili mara tunani mara ilimi in......."
Katseshi nakarayi nace
"Kasan Allah zanfada maka maganar da bazaka taba mantawa da itaba harka mutu wallahi idon kayi wasa Ana indai har zakaci gaba da fadawa sweetheart dina irin wadannan magan ganun tofa wataran Baki zaiyi jini ato nafada maka idon kunne yaji anhuta" Ina fadar haka najuya da nufin komawa gida kawai jinai yajawoni nafado jikinsa yadaga hannu tare da shararamin marika guda biyu aikuwa rike wajen nayi Ina kallonsa hawaye keson tahomin Amma nadake narukeso don karyaga gazawata nace
" Nika marako wallahi Allah ya Isa banyafeba mugu kawai kuma insha Allah Sai Allah yayimin sakayy......."
Ai bankarasa kaiwaba yakara sakarmin wani Marin Wanda yasakani ganin duhu zuwa nawasu lokuta sannan nadawo daidai hatta jina saida narasashi na wucin gadi,
Magana yafara cikin bacin rai yace
"Inaso kisani bana sonki Kuma natsaneki wallahi da ace za,a bani bindiga ace nakashi wani mutum mace ko namiji aduniya wallahi dake zanfara kashewa saboda banason ko ganin kala kalar fuskarki Kuma indai Kika yadda aka dauramin aure dake kisani kinyi sallama da farin ciki kinshigo kangin rayuwa don wallahi saikin gwammace mutuwarki akan komai ke kisani ni Adam aduniya Babu mutumin Dana tsana sama dake Kuma bazan taba sonkiba har abada banza jaka mara hankali wacce batasan anyimataba nashirya aurenki Kuma nashirya tarbarki cikin gidana Allah yabaki ikon shigowa kiga abinda nafada Miki"

Yana kaiwa Nan yayi wulli Dani gefe guda Wanda Saida kaina ya daki bangon kofar gidanmu tashi nayi cikin sauri nashege gida bansami kowa atsakar gidaba don haka nashige ciki Ina kuka nafada kan gado,

Kuka nakeyi don gaskiya kalamanshi bakaramin batamin Rai yayiba Kuma naji haushinsu kuka nakeyi Babu Mai lallashina nadauki tsahon lokaci ahaka kawai naji karar wayata dubawa nayi naga my love ke kirana saurin dauka nayi tare da sakin kuka nakasa cewa komai kuka kawai nake yimasa hankalinshi yatashi Yama kasa zama shida da yake kwance Amma yanzu yamike tsaye jeromin tambayar kawai yakeyi
"Please kiyi shiru kifadamin menene waye ya mutu kiyi shiru sweetheart don Allah kiyimin bayan" Jin da yayi nakiyin shiru yasakashi cewa
"Tunda bazakiyi maganaba bari nazo gidan kawai Amma kinsan dare yayi ko Kuma indai nazo saina shigo ciki saina fadawa Yaya da Innarmu abinda yafaru tunda ni bazaki fadamin ba" cikin kuka nace
"Kataimaka min karka bari a auramin wancan mugun mutumin wallahi kasheni zaiyi kainake so bazan iya yimasa biyayyaba bazan iya zama dashiba wallahi yadauki alkawarin saiya sauyamin rayuwata tadawo abin tausayi please sweetheart kataimakamin tun Ina gidanmu yafara dukana inakuma Dana shiga gidansa nakai kaina yayi yadda yaga dama kenan" labarin abinda yayimin nabashi dakuma alkawarin Daya dauka akan aurena dashi.

*Comment*
*&*
*Share*

*By*

*Khadeejah (Ummu Fu,ad & Afnan)*

*🙆🙆 RAYUWATA CE*🙆🙆

*Na*

*Khadeejah Sani (Journalist)*

*🌈KAINUWA WRITERS✍🏼 ASSOCIATION*🤝🏼
```{United we stand and succeed;Our ambition is to entertain & motivate the mind of readers}```
```

https://www.Facebook.com/kainuwawritersassociation

*🅿25 _ 26*

Kallonta nayi saina kara fashewa dawani sabon kukan tare da fadin
"Wallahi yatafi yabarni Innarmu yace bazai dawoba sai yamanta dani, Innarmu kataimakamin kar,a auramin wancan mugun kasheni zaiyi wallahi nashiga uku" nakarasa tare da fadawa jikinta,
Batayi yunkurin tambayata ba saboda tasan da tafiyar tashi don haka tayi shiru tare da bubbugamin bayana tana kallona,
Azuciyarta tausayin yarinyar Tata takeji don ko,ita shaidace akan yadda Mai sunan manya don agaskiya baya kaunarta kwata kwata gashinan rabonshi da gidan tun Ana saura wata guda bikin gashi Nan baikara zuwaba ko yazo yakawo mata abinda zata walima baiyiba don hakanema takarbi kudi hanun yayansu don tadan hadamin kayan dazan bawa kawayena tunda ta aika musu da katin da Yaya yabiga don sunanmu yasaka nida nafisa,
Lallashina takeyi tana nunamin wannan shine nawa kaddarar nayi hakuri yacinyeta karna bijirewa abinda Allah yariga yarubutashi, ganin danayi hankalinta yatashi yasakani yin shiru tare dakara lafewa ajikinta dagani tayi tace
"Tashi mujecan Kisha magani" Saida namaida takardar cikin envelope sannan nadauki abuna nabi bayanta adaki nasameta taredasu Yaya sunata ganin kayan ko kallonsu banyiba nanemi wuri nazauna magani tabani nasha sannan namike zanshige daki tace
"Nafisa zonan" dawowa nayi nazo nazauna kusa da ita tace "gakayanki Nan bakiganiba Zaki wuce daki Kuma banason wannan kukan karna Kara ganinki kinayinshi" daga mata Kai nayi tare da kallon kayan kirgawa nayi akwatina guda takwas ne nace
"Nagansu Innarmu bacci nakeji zan kwantane"dagamin Kai tayi alamar to don haka natashi nayi daki,
Kwanciya nayi tare da rungume envelope din nan kukan zanfara saina tuna yace karnayi kuka dayawa karya cutar Dani don haka nayi shiru saikuma natashi nabude cikin envelope din nadakko kudin dayace aciki kudin Mai yawa yan dubu dubu bandir biyu saikuma ATM nakallesu namaida tare da dorawa asaman jakata,

Baccine yayi gaba dani don haka bansan abinda yake faruwaba,
Sai bayan natashine mahbub yake fadamin Wai Yaya yazo Ina bacci yace atasoni shine mahbub din yace banida lafiya shine ya rubuta wasika yace ya ajiyemin tare da kudi karba nayi nagyara zamana nabude nafara karantawa,
*Uhm lallaine yarinya kinsami hutu wato harwani bacci kikeyi ana cewa baza,a tadakiba okay hakane gwara kigama hutunki cikin yan kwanakin da suka ragemiki kafin kibar gidan kishiga kurkuku, Daman bawani abune yakawoniba mamace ta takirani akan saina Baki kudin fati wallahi badaban itace tace nabakiba da Babu abinda zanbaki saidai ki mutu idon bakiyiba Kuma insane naki kawo Miki da wuri don karkiyi komai dasu maganar katin bikima insane Kuma nabugashi harna bawa mama nata kekuma naki saikinje can Zaki sameshi acan, hmm Ina Kara

murna da irin rayuwa da zakiyi acikin gidan yarinya gashi kinsaba dabin Maza ko yanzu Kuma za,a kawoki gidana Zaki daina haduwa dasu bansan Yaya zakiyiba Kuma saidai ranar, mara kunya jaka Yar iska karuwa wacce tarbiyya Bata ishetaba saikin shigo gidana zamu hadu don bana fatan haduwa dake Sai acan din*

Maimaita takardar nayi saikuma nasaki murmushi kudin naduba naga dubu goma tsaki nayi nace

"Banza talaka kawai kalli wandama bashi zan auraba yabani kudi wanda bansanma yawansuba tunda gawani acikin account dina don haka namikawa mahbub dake zaune Yana wasanshi nace

"Kaiwa Innarmu kudin" karba yayi yafita,

Tashi nayi nashiga wanka Saida nafito nagama shiryawa sannan saiga Innarmu tashigo tazauna kusa Dani tace

"Kudinme yace Miki wannan" murmushi nayi nace

"Waikudin fatine mama tace saiya kawo da Babu abinda zai kawomin" itama murmushi tayi tace

"Ai dama yabarshi tunda mungama komai, Amma yanzu kirikesu ahannunki Koda zakiyi wani abun" girgiza Kai nayi nace

"A,a Innarmu Kinga Muslim ya aikomin da kudima gashi nabata bandir Daya nace kirike wannan Koda zakiyi wani abun dashi"

Zare Ido tayi tace

"Duk wannan kudin yabaki nafisa?"

"Bama sukadai bane Kinga sauran" dakkowa nayi na nuna mata Nan tashiga yimasa addu,a da godiya tace

"To Kinga kihada kirike inyaso kyafunga amfani dasu acan din"

"A,a Innarmu kibarshi kawai wannanma yayi"

"To Amma Ina ganin inkikaga yanayin unguwar kifara Sana,a don zama haka bazai yiwuba"

"To Innarmu zanyi ammadai kibar wannan kudi awurinki kuboyesu kyayi amfani dasu" to tace tatashi tasakasu cikin kayanta tayi waje,

Abinci tazubo takawomin tace kwanon take bukatar hakan yasakani dole nazauna nacinye,

Dayake Ina fashin sallah shiyasa nakoma nakara kwanciya don banajin dadin jikina,

*******************

Rana Bata karya saidai uwar Diya taji kunya inji hausawa,

Ayaune dubban jama,a suka shaida daurin auren *ADAM ISYA JIGO DA NAFISAT ADAM JIGO saikuma MUDASIR ADAM JIGO DA NAFISAT ISYA JIGO* wanda dubban mutane suka

shaida anata addu,are Allah yabada zaman lafiya,

Kasancewar agidan babanmu aka dauramin auren shiyasa bamu saniba Amma nidai lokacin da aka dauramin auren Saida gabana yayi mummunan faduwa dafewa nayi Ina ambaton sunan Allah,

Ahaka nayi wunin ranar cikin sanyi kawayena sunzo anmana wa,azi wata mata da Innarmu tadakko tayi nasiha akan zaman aure biyayya dakuma hakuri,. Duk jikina yakara sanyi Banda kuka Babu abinda nakeyi saikuma tunanin masoyina Wanda nake ganin da ace dashine aka dauramana aure yau dabansan irin farin cikin dazanyiba Shima Kuma haka don nasan yadda yadda yake kaunata kamar me,

Wuraren karfe takwas da tabi motocin daukar amarya sukazo Nan yan,uwa da abokan arziki suka farayimin fada nidai Banda kuka Babu abinda nakeyi har aka kaini wurin Innarmu dake daki zaune kasa yimin magana tayi kawai tasaki kuka aikuwa nafada kanta Nima inata kukan mundauki lokaci ahaka kowa tausayin yakeji harda masu tayamu dakyar aka rabani da gida aka tafi Dani inata kuka,

Lokacin da mukaje gidansu Yaya lokacin har andakko amarya nafisa itama anyo Nan da ita dakin Mama aka kaini tayimin nasiha sannan dakin baba Shima nasihar yayimin sanann muka fito akayi gidan don Babu wani nisa sosai atsakaninmu dasu,

Munje mutane nata yaba kyawun gidan haka aka Gama gani sukayimin sallama Daya bayan Daya suka tafi aka barni nikadai Sai kewar Innarmu da mahbub nakeyi,

Har karfe shabiyu babushi Babu alamarshi tashi nayi nashiga bandakin dake dakin nayi wanka nafito nashirya cikin kayan bacci nasaka Riga da Wanda nakoma nakwanta Saida nakarayin kukana kafin nan bacci yayi awun gaba dani,

Cikin bacci naji an dakamin want irin duka daysakani tashi zaune Ina murje idanu wazan gani ba yayaba yata wani cin magani kallonshi nayi dagashi Sai gajeran wando don haka nayi saurin dauke kaina Ina kallon kasan dakin,

"Kega Yar iska shine tundazu akawoki bazakije dakinaba kiji ko akwai abinda zakiyimin to Maza kitashi kike kidafamin shinkafane da wake kafin ranki ya baci yanzun Nan"
Kallonshi nayi zanyi magaan saikuma nafasa natshi nayi waje biyoni yayi abaya har kitchen din nidai bankara hi takansaba naje nakunna gas sannan nadora ruwa dubawa nafarayi naga banga wakeba saidai shinkafane da taliyar da sauran kayan da aka kawomin na gara don haka najuya da nufin naje wajensa na tambayeshi saina ganshi tsaye nace
"Ina waken yake?"
"Nizaki tambaya dama ba,a hadomiki dashiba cikin kayan garar nakina lallaima kunrainamin hankali wallahi" kallonshi nakarayin na dauke idona Ina jiran naji abinda zaice Sai kusa yace
"Shiga Nan kiduna akwai komai aciki gidana ba,a yunwa Kuma Koda bakizo dashiba natanadi

kayana don nasan kuma ba isarku yayiba balle kukawo wani gidan" maganarshi ta batamin Rai Amma saina daure nayi gaba abuna debo waken nayi nagyarashi na wanke nazuba duk Yana tsaye Sai cankuma yafita,

Zaune nayi inata tunanin wannan rayuwa Wai ace ranar da katare matsayin amarya Amma asakaka girki uhm Allah ya sakamin,

Ina zaune inata girkin harna gama nazuba Mai acikin kula nadauki faranti nafita dashi kaimasa nayi sannan nadawo nadauki Mai nakawo Masa Yana zaune afalo,
Ina Gama ajiye Masa nayi hanyar daki don bacci nakeji sosai ba kadanba ga gajiyar taro damukasha jinai yace
"Ke" nayi niyyar yimasa banza saikuma najuyo nazo na tsugunna nace
"Gani"

"Haka aka koya Miki agidanku idon aka kawowa miji abinci ba,a zuba Masa kokuwa duk cikin rashin kunyar taking haka" matsawa nayi nafara zuba Masa batare danace komaiba nagama sannan nayi shiru Ina tsugunne yace
"Meye Kuma Kika zauna kin sakani gaba kina kallona saikace mayya wama yasani ko iatance" mikewa nayi nakoma daki inata tunanin wannan rayuwar,

Kwantawa nayi bacci yayi awon gaba dani inacikin tunani,

Nayi nisa cikin baccina tare da mafarkin masoyina waiya dawo harmunyi aure kawai saijinayi an daukeni da wani gigitaccen Mari Wanda bansan adadinsaba tashi nayi zaune cikin tashin hankali tare da kallonshi.

*🙆🙆 RAYUWATA CE*🙆🙆

*Na*

*Khadeejah Sani (Journalist)*

*🌈KAINUWA WRITERS✍🏼 ASSOCIATION*🤝🏼
```{United we stand and succeed;Our ambition is to entertain & motivate the mind of readers}```
```

https://www.Facebook.com/kainuwawritersassociation

*🅿27 _ 28*

Kuka nasaki da fadin
"Don Allah kabarni nahuta mana inace abincine kuma nadafa maka amma bai,ishekaba saikata dukana kamar wata jaka nidai agas......." Ai bankai karshen maganarba naji saukar wani Marin cikin bakina tare da karamin wani a kuncina dafe bakin nayi nasaki sabon kuka,

"Dallah tashi kije kiwanke kayan da Kika Bata kina nufin kazanta Zaki dunga yimin ne acikin gida to wallahi bazan daukaba niba kazami bane kintashi ko Baki tashiba saina makeki mara kunyar yarinya Yar iska"

Kokarin sakkowa daga gadon nafara tare da tunanin wannan itace irin rayuwar daya shiryamin kenan acikin gidan aikuwa indai hakane nashiga uku,
Waje yayi yanata faman fada ganin hakan danayi yasakani saurin kulle kofar nace "wallahi Babu inda zanje mugu kawai" Jin nakulle kofar yasakashi dawowa Yana faman masifar nabude kukama ya ballani idon yadakko makulli Jin hakan yasa nadauki makullan da akabani harda nadakin naje nasaka ajiki nakulle nabarshi ajiki nadawo hankalina kwance nakwanta abina nacigaba da baccina,

Haka yakaraci hayaniyarsa yagaji yaje ya kwanta yaci alwashin da safe saiyayimin dukan tsiya nidai baccina nake bansan wainar da ake toyawaba,
Washegari da asuba natashi kasancewar akwai bandaki wanka nayi sannan nayi sallah nafara karatun alkur'ani saikuma naji bacci kawai na rufeshi nakoma nakwanta baccine yakara daukeni kamar amafarki naji muryar Yaya Yana hayaniya yanata fada bude Ido nayi najiyoshi Yana fadin
"Bazaki bude dakinba ke bafa nason rashin mutunci ke wacce iriyar jakar yarinyace wallahi idon Baki budeba jikinki zai gayamiki bazaki budeba"
Ina jinsa nayi shiru inata raba idanu saikuma namike nasaka hijjab Dina danayi sallah naje nabude tare da fadin
"Inakwana Yaya?" Rufe bakina keda wuya naji saukar duka dakinayi da gudu yabiyoni Yana dukana Wai akan jiya nakwanta banyi wanke wankenba haka yakamani da duka Saida yaga nadaina kuka saboda wahala nayi shiru sannan yabarni yayi hanyar fita waje tare da cewa
"Kuma kifito kiyi wanke wanken kafin nadawo nasameki"
Kukan danakeyima yadaina fitowa sosai saboda wahalar danasha danaga abin nashi da gaskene don harya dawo dakin Wai zaikara dukana hakan yasa namike nayi waje Babu shiri,

Kayan Dana kawo Masa najiya nagani azube inda suke daukewa nayi natafi kitchen dasu,

Wanke wanken nakeyi Ina kuka don jikina Banda radadi Babu abinda yakeyi wannan bawan Allah akwai mugun mutum,
Ahaka nagama namaidasu inda suke sannan nafito,
Bansameshi afalonba don haka nashiga daki Ina zaunawa naji ya kwadamin Kira tashi nayi nafito nace gani kallona yayi yace
"Okay kazantarce Zaki farayinta acikin wannan tsararen gidan nawa to Maza kije kiyi wanka kafin ranki yabaci" komawa nayi dakin nashiga toilet don nayi wanka,

Bayan nayi wanka nasaka Kaya Mai kawai nashafa ajikina da duk yakemin zafi har wani wurin yayi shatin duka,
Daukar magani nayi nasha sannan nakwanta Ina tunanin da ace inagida yanzu banma tashiba tunda Sai wurin takwas muke tashi ranarda Babu makaranta Amma yanzu no babuni Babu bacci kenan,

Ina haka bacci barawo yayi gaba dani Saida nayi Mai isata sannan natashi don kaina Ina tashi naduba Naga karfe goma tashi nayi da sauri nashiga toilet nawanke bakina nafito,
Fall nayi saina samu ankawo Mana breakfast daga gidansu yaron na zaune Mai suna mashkur sa,an mahbub ne Nan yagaidani yace
"Anty tundazu nazo inata sallama naji shiru Dana shigo sainaga kina bacci Kuma Naga Babu motar Yaya yafita shine nazauna jiran tashinki" murmushi nayi nace
"In Banda abinka mashku ai dakasani katasheni, ya gida ya mama da baba?"
"Lafiya kalau suke suna gaidaki Kuma mama tace Wai karkiyi girki na Rana da dare har zuwa sati zata dunga Aiko Miki dashi"
"Allah sarki mama aikuwa nagode kafada mata nagode sosai" Nan mukayi fira dashi dakko faranti nayi nadibi abincin tare da tea din da aka hado dashi naci Shima nazuba Masa yaci kunsan abin yaro koyaci aguda baiki ka Kara masaba,

Bayan nagama tashi nayi nadakko want abun najuyewa Yaya nawanke kwanonin nabashi yatafi dasu,

Hakama da Rana aka kawomin abinci alokacinne Kuma kawayena sukazo Nan mukasha Hira sunata tsokanata Wai kodai kodai sunga nacanja azuciyata nace nasha duka dai,
Haka muka wuni dasu Sai bayan magriba sannan sukace zasu tafi cikin kudin da Muslim yabani da do akko dubu daya nabasu kudin mota kowanne mamaki yakeyi Wai Ina nasami kudi haka nidai shiru nayi dasu Sai Daya daga ciki maisuna aysha tace
"Kuma dawata tambaya ta rainin wayo mace da mijinta kuce Ina tasami kudi lallaima to nibari nabaku amsa mijintane ya ajiye mata saboda Baki masu zuwa" dariya nayi nace
"Yawwa tawan kinbasu amsa daidai kuwa" dukkansu mamaki sukeyi haka muka rabu kamar nabisu suka tafi sukuwa kowacce da tunanin dama itace ta auri miji kamar haka data huta,

Har aka kawo abincin dare baidawoba hakan Kuma yayimin Dadi naci abuna nabarmasa nasa

anan falon nakoma daki nayi Shirin bacci kulle kofar nayi na kwanta tare da dakko wayata Ina kokarin Kiran Innarmu tashiga Nan tadaga muka gaisa tare da dantaba fira kadan,

*******************

Bangaran su Yaya kuwa bayan ankawo amarya mutane suntafi Innarmu tanata sallamar bakinta itama amarya da kawayenta suna cikin dakinta kawayen amanarya sunata shewarsu irin ta yanmatan amarya,

Wurin Taran dare suka yimata sallama suka tafi nan tazama saura ita kadai,

Yaya kuwa Sai wurin Tara da rabi sannan yashigo don dama yafada mata shifa Babu wasu abokai dasu rakoshi shiyasa itama tace basaisun tsayaba,

Yana shigowa dakin Innarmu yafara zuwa ya ajiye mata kullinta sannan tayimasa nasiha Mai ratsa jiki bayan tagamane tace yatashi yaje Allah yabasu zaman lafiya,

mikewa yayi yashiga dakin nata zaune take bakin gado fuskarta rufe da mayafi zama yayi kusada ita tare da bude mata fuska Yana murmushi,

Itama murmushi tayi don ita to kuka batayiba sosai,

Kallonta yayi tare dayiwa Allah godiya Daya mallakawa mishi mata kamar wannan,

Mikewa sukayi sukayo alwallah sukayi sallah sannan yayi musu addu,a sosai yakama kanta yayi sannan suka faracin kazar Daya shigo da ita kunya ta hanata ci sosai don haka kadan taci tatashi tace takoshi,

Shima tashin yayi tare da tattare kayan yakai cikin firinji yadawo toilet tashiga ta wanke baki tafito Shima shiga yayi Amma Saida yayi wanka sannan yafito kasa kallonshi tayi har yasaka sleeping dress yazo kusa da ita yace

"Ganaki kayan tashi kisaka saikizo kikwanta nasan agajiye kike"

Tashi tayi tadauki kayan tayi toilet don tasaka.

*Comment*

*&*

*share*

*By*

*Khadeejah (Ummu Fu,ad & Afnan)*

*Comment*
*&*
*Share*

*By*

*Khadeejah (Ummu Fu ad & Afnan)*

[9/14, 8:08 AM] Hayat: *🙆🙆 RAYUWATA CE*🙆🙆

*Na*

*Khadeejah Sani (Journalist)*

*🌈KAINUWA WRITERS✍🏽 ASSOCIATION*🤝🏻
```{United we stand and succeed;Our ambition is to entertain & motivate the mind of readers}```

https://www.Facebook.com/kainuwawritersassociation

*🅿31 _ 32*

Saida nayi musu wani kalolin abincin sannan nafito musu dashi, suna Nan sunata aikin da sukaga afimusu nashige abina,
Daki nakoma nakwanta asaman gado tare da dafe kaina dakemin wani irin ciwo rufe idona nayi ina tunanin wannan rayuwar,
Sundauki lokacin sunata firarsu inajinsu sai zuwacan naji sunkoma daki saikuma naga anturo kofar dakina,
```

Mikewa nayi da sauri tare da kallonshi yawani hade rai yace
"Kitashi kije kikarasa gyaran falon sannan kiwankemin motata tafita sosai ki gogeta saikuma wankin da na ajiye Miki Yana Nan afalo Shima kiyishi kafin mutashi daga bacci don yau bafita zanyiba sai anjima zankai dear unguw" yana gama fadar haka yayi waje mikewa nayi jikina duk yayi sanyi dajin irin wannan muguntar shikenan nazama yar aikinshi kenan kuma harda wankin mota toni inama nataba wani wankin mota ko ganin yadda akeyi bantababa balle nace nakoya anan,

Fitowata daga daki naga wani abun mamaki kayanshine kala uku saikuma gajeran wando guda hudu harda Wanda yasaka jiya da yazo da yarinyar Nan dama nayau Dana gani ajikinsa saikuma kayan danaganta dashi jiya na bacci dakuma nadazu sai pants dinta Suma kallon kayan nayi kawai sainaji wani kuka yazomin yanzu ace mijin da nake aurene yazo da wata karuwa gidana sannan sugama iskancinsu abani kayanta ace nawanke ai wannan bakaramin rashin mutuncineba gaskiya,
Gyaran falon nayi nadauki kayan nayi waje wankin nafarayi sannan nakoma wajen motar nama rasa mezan fara kallon motar nakeyi sai kawai naje nadakko ruwa acikin bokiti na ajiya nadakko wani bokitin karami na ajiyeshi omo na kada nasami wani abun nafara wankewa inatayi harna gama nazo nadauraye sannan nadauki duster nagoge,
Saida naga Babu ruwa ajiki sannan nabarshi nakoma daki,
Lokacin Dana koma har biyu tawuce toilet nashiga nayi wanka nayi alwallah nadawo nayi sallah sannan macanja Kaya nashirya kwantawa nayi duk agajiye nake banajin Dadin jikin gabaki Daya don haka nakwanta shiru Ina haka bacci yayi gaba dani,

Bansan lokacin da suka tashiba kawai jinayi an wankeni da wani Mari daysakani tashi zaune Ina hawaye yace
"Dan ubanki haka ake wanke mota duk kinbi kinjikemin ita kalli jikina dana zauna yanzu" yafada Yana juyomin bayansa duk yajike yadora da fadin
"Hakama dear itama duk jikinta yabaci to zakici ubanki wallahi yau....." Karuwar tashice ta katseshi tace
"Dear rabuda ita kawai tazo muje taciremin kayanan ta canjamin wani kaima tacirema tacanjama wani aikin da zatayi kenan sannan tawankesu tahada da wadancan kayan ta goge Mana"
"Yawwa dear kinkawo shawara haka za,ayi wuce muje" wucewa nayi gaba suna biye Dani abaya har dakin nashi natsaya karasowa tayi tace
"Uhm fara aikinki"
Kallonta nayi nama rasa abinda zanfara yimata don haka nakalleta nace
"Mezanyi to"
"Ciremin kayan zakiyi Mana kicanjan wasu har pant dinama yajike don haka harshi"
Murmushi nayi kawai nasaka hannu nafara zuge zip dinta don doguwar rigace ajikinta nadawo na cireta nazame pant din nata duk kunya tabi takamani Amma ita Naga ko ajikinta sai firarsu sukeyi dashi,
Bude jakar kayanta nayi zan dakko mata wasu kayan sainaji tace
"A,a zuki fara ciremasa kayan sannan kidakko Mana wasu"

Juyowa nayi zanfara cirewa Sai naji yace
"Dear kiciremin da kanki wallahi Ina gyamin wannan yarinyar ne shiyasa banaso ta ciremin"
"Okay bara nacirema kekuma dakku kayan"

Juyawa nayi tare dayin hamdala bansan abinda suke yiba najuyo don na ajiye kayan akan gado kawai Naga nagansu manne da juna sunata aikinsu Sai uban nishi sukeyi saurin dauke kaina nayi na ajiye kayan nayi waje,

Wanka nayi nayi sallah sannan nafito nadibi abincina nakoma daki nakulle don banaso yazo yadameni,

***************

Haka rayuwa taketa tafiya kullum akwai kalar rashin mutuncin dazai billomin dashi yau inyayi wannan gobe wancan ahaka har munci wata Daya da kwanaki yanzu nice kemana girki idon karuwar tashi taso inagamawa tace baimataba inkuma taso tayi shiru taci idon yatafi office Bata kulani saidai tashige dakinshi tayi zamanta nikuma nayita aikina,
Bangaran su Yaya kuwa anacan anatashan soyayya kamar baza,a mutuba nafisa tasaki jikinta tana fitowa wurin Innarmu suyi aikin gida don abincin Rana Dana dare tace keyinshi tahana Innarmu itakuma innarmu tahanat yin breakfast itace take musu,
Dafarko innarmu tasoma anraba girkin tadungayi da kanta amma tace a,a abarshi ahade yafi don haka sukabar girkinsu ahade,

Acikin kwanakin Nan Naga suncanja want kalar tsarin idon yafita aiki itama saita fita Bata dawowa sai dare kokuma sudawo tare hakan bakaramin Dadi yayiminba don nasake Koda baki nayi banata jin tsoran karta fito sugantaba,

Yau zaune nake nagama abincin rana inata kallo kawai saijinayi anshigo da mota kasancewar akwai get man kallon kofar falon nayi nace araina ko wanene kokuwa shine yadawo yau yanaji da wani bala,inne bankai da rufe bakinaba kawai naga mahbub yashigo ai tashi nayi cikin murna natareahi don baitaba zuwaba,
"Oyoyoyo my brother kaida waye haka naji mota?" Tunda nasan Yaya bashida mota,
"Nida yayane da anty mukazo gasunan shigowa" ai inajin haka nayi waje da guduna na tarosu Ina murna Nan suka shigo Ina kusa da nafisa muka gaisa nanfa akafara fira tashi nayi naje nadakko abincin danayi nakawo nakina nadakko lemukan da akayimin iyaka dasu kullum siya kirga idon zaifita Wai karnasha Masa tunda ko agida Basha nakeyiba lokacin naji zafin maganar don haka bantaba tabamasaba sai yau Shima Kuma saboda bakine,
Nacika musu gabansu da kayan motsa baki sannan nazauna munata fira,
Yayane yace
"Waikekuwa yanaga kinrame kinyi wani bakki haka kodai bakida lafiyane" murmushi nayi nace
"Wallahi Yaya lafiyata kalau Nima haka Naga nakoma wata kala Amma Naga nafisa tayi kiba

takara wani haske kodai kodai" gallamin harara yayi yace.
"Sa,ankine Niko?"
Dariya nayi tare da sunkuyar dakai kasa.

*Comment*
*&*
*Share*

*By*

*Khadeejah (Ummu Fu,ad & Afnan)*
[9/15, 7:16 AM] Hayat: *🙆🙆 RAYUWATA CE*🙆🙆

*Na*

*Khadeejah Sani (Journalist)*

*🌈KAINUWA WRITERS✍🏼 ASSOCIATION*🤝🏼
```{United we stand and succeed;Our ambition is to entertain & motivate the mind of readers}```

https://www.Facebook.com/kainuwawritersassociation

*🅿33 _ 34*

Fira mukeyi cikin kwanciyar hankali can nace
"Au namanta Yaya yaushe kayi mota bansaniba Babu labari?"
Dariya yayi yace
"Kindai ganta baki ganetaba ta Muslim ce yasaka drive dinsa yakawomin Wai narunga anfani da ita kafin yadawo, saboda ajiyan karfe ba,a hawa yanada matsala" lokacin Daya Kira sunansa Saida gabana yayi mummunar faduwa don kusan kulluma sainayi kukan rashin mutum Mai ilimi, mutumnci, sanin yakamat, nutsuwa, uawa uba kuma tarbiyya saurin dauke tunanin dayayimin karan tsaye nayi tare da zabga uban murmushi Wanda ake cewa kafi kuka ciwo nace
"Ayyah Allah sarki yaya Muslim ashe kunayin way dashi" don dama agaban Innarmu da Yaya
```

haka nake fadamasa amsa yabani yace
"Aikuwa ko jiya munyi waya yacemin ya wajenki nace kina can bantaba zuwaba shine yace gaskiya ban kyautaba nasamu jiyan nazo nace yayi hakuri saidai zuwa gobe"
"Allah sarki bawan Allah ashema shine yasakaku zuwan Nan da kukayi"
"Aikuwa dai don wallahi idon ta nine bayanzu zanzoba saidai baby tazo itada mahbub"
"Ai gashinan yayana yasakaka zuwan dole dai"
"Kuma Allah dandai Ina masifar ganin girmansa yasa nazo da Babu inda zani cewa kawai zanyi Masa nazo kina gaidashi dondai bazan iya yimasa hakaba don daima yanzu nasan Yana makaranta ko compan ninsa Dana kirashi kungaisa Amma darensu yakusa bari kafin mutafi nakira mikishi"
Cikin farincikin nace "yawwa Yaya dakuwa ka kyautamin wallahi"
Nafisace wadda tundazu taketa kallonmu muna Bata Sha,awa jitake dama yayantane yake zama haka suyi fira datafi kowa Jin dadi Amma shi sai shegen girman kantsiya da jijjida Kai Sai masifar tsiya tace
"Uhm uhm naga alamar kunmanta danima gabaki daya awurin Nan alama ko?"
Murmushi nayi nace
"Habadai na isa namanta da matar yaya babba ai ban,isaba wallahi"
Dariya shikuma yayi yace
"Kekuwa yaushe rabon da muhadu kusan wata da sati Daya kenanfa ai dole azanta"
"Ummm gaskiyane to Nima bari nakira nawa yayan yadawo guda muyi hira tunda naga Bata da alamar kiransa"
Kallonta nayi nace
"Kirashi da kanki ai kunfi kusa"
Dariya tayi tare da daukar wayarta tafara kiransa tashi tayi tabar wajen don tasan indai takirashi da zagi yake farawa don haka ta tashi karma yabata kunya,
Firarmu muka Dora da Yaya nace
"Ni Yaya naga haryanzu bakaci komaiba Dana ajiye muku gwara nafisa Tasha lemo taci abincin kadan"
Murmushi yayi yace
"Ke akoshe nake Amma bari nasha lemon kawai"
Dauka yayi yanasha kallonshi nayi azuciyata nace
"Hmmm bakasan akalar cin mutuncin da akayimin ba akan wannan abin banzan daba damuna yayiba kwata kwata" maganar da yayine yadawo Dani yace
"Yada kallo haka konima nayi kibarne bansaniba" dariya nayi nace
"Wallahi kayi kiba sosai bakaga yadda kakomaba harda wani tunbi kayi" dariya yakeyi yace
"Lallaine yarinya kinrainani da yawafa nine nayi tunbin?"
Nima dariyar nayi nace
"Eh Mana kaga yadda kadawo ne?"
"A,a banganiba saike sa idunawa" dariyar nakarayi nace
"Yaya wallahi jinake kamar karku tafi dama harda Innarmu kukazo dayau naji dadin dayafi haka" kallona yayi yace
"Kefa dadina dake bakida wayo wani lokacin shikenan Sai mutaho harda Inna saidai wata ranar nakawo miki ita ta yini idon nadawo daga aiki nabiyo muwuce gida"

"To Allah yakaimu" nafisa ce tadawo tazauna kusa da Yaya tace
"My love kaji Yaya yace Wai aiki yayi Masa yawa shida gida Sai dare bazai samu dawowaba dawuri"
"Ayyah Allah baiyi zaku haduba sai wani lokacin"
Fira mukeyi har akayi sallahr la,asar don haka Yaya yafita masallaci dake layinmu mukuma muka shiga dakina donyin sallah,

Bayan mun,idar muka zauna acan munata fira da ita har lokacinda yadawo yace tafito suwuce,
Munyi sallama da ita awurin mota ta shiga sannan muka tsaya da Yaya nace
"Yaya waya nakeso Mai kyau zandunga chat da ita don Allah inada kudi zanbaka kasiyamin ko gobene idon kadawo daga aiki saika bani don Allah" kallona yayi yace
"Dama naga alamar bakwayin zaman lafiya da mijinki Amma zamuyi maganar Sai nadawo jeki dakko dubu goma saina cika miki nasiya Miki Yar dubu talatin ko talatin da biyar"
Harna juya saiyace
"Kezo nakirashi kugaisa Kinga namanta ko?"
Murna nayi dajin hakan don dama Yana Raina maganar kawaidai nayi shirune Kuma shiyasa na kawomai maganar siyan wayar donya tuna,

Gaisawa sukayi sannan yace gani Nan yamikomin na juya nayi gidan Ina cewa
"Yaya bari nakawo kudin yanzu"
Gaidashi nafarayi ya amsa sannan yace
"Ya guda da maigidan gidan naki?"
Cikin sanyin murya da rawarta nace
"Lafiya kalau ya karatun"
"Alhamdllh yanajiki haka bakida lafiyane?"
"A,a lafiyata kalau mekaji"
"Kifadamin gaskiya wallahi acikin kwanakin Nan inaji ajikina akwai abinda yake faruwa dake Kuma bamai Dadi bane shiyasa na takurashi yazo yaga lafiyarki"
"Uhm Babu komi yaushe zaka dawo?"
"Babu rana saina kammala karatu Nanda shekara da rabi insha Allah"
"Allah ya kaimu yabada abinda ake nema yasa anyi asa,a"
"Ameen kema Allah yabaku zaman lafiya kidunga yiwa mijinki biyayya kinji Nafeesat nasan kinada tarbiyya da ilimi to don Allah kikara akan wanda nasanki dashi kinji?"
Kuka nafara tare da fadin
"Insha Allah zanyi yadda kace nagode Allah yabaka mata tagari kamar yadda kake nagari" inakaiwa Nan nakwashe wayar tare da goge fuskata nafito daga falon don dama nashiga harna dakko kudin nafito,

Tsaye na taddashi kamar yadda nabarshi na mikamai wayar tare da kudin nace
"Yaya nasan abubuwa sunma yawa ga dubu talatin nan kasiyamin wayar kacikamin sauran nagode Allah yabar zumunci" kallona yayi kamar zaiyi magana saikuma yafasa yace ameen,

Komawa nayi na yiwa nafisa godiya tare da Bata wani sirrinmu aleda nace zamuyi waya nan tafara godiya shikuwa mahbub bashi kudi nayi nace yakaima Innarmu sannan Shima nabashi dubu daya,

Ina Nan tsaye harsuka bar gidan kukane yaci karfina nakoma ciki,
Ina shiga naci Karo da jarkokin lemon da sukasha guda uku murmushi nayi nace
Ohhh ni nafisa ko Yaya zamuyi da wannnan bawa naka idon yadawo kuwa akan lemon Nan oho saiyazo naji,

Gyara falon nayi sannan nashiga kitchen don girka abincin dare,

Sai kusan magriba nagama komai sannan nadibi nawa nakoma daki,
Bayan nayi sallahr magrib da Isha,I sannan nazauna naci abinci yau kasa cin abincin nayi sosai saboda tunanin Muslim dayake raina Shima yadda naji muryarshi nagane dauriya yakeyi kawai kiris yarage yayi kuka don nasan bashida wuyar kuka shiyasama nayi saurin kashe wayar,
Zaune nake inata tunanin Muslim abinda nayi kokarin yakicewa kaina kenan amma hakan yaki ciruwa saidai dana fara tunaninshi nayi saurin fara karatun alkur'ani hakan yakesa nayi saurin kawar da abun Amma yaudai abun yaci tura kodan nayi wayane dashi kila yasa hakan,
Bansan tsahon awannin Dana daukaba anan kawai saijinayi ana kwadamin Kira dawowa nayi daga tunanin Dana Lola tare da kallon agogo tashi nayi da sauri ganin goma harta wuce nayi saurin fitowa zuwa falon tare da amsawa nace
"Sannu da zuwa ya......." Ban karasaba yafara fadin,
"Wanne Dan iskanne ya shamin lemona Dana ajiye, banace karki sake kidaukar minba dama Ina kirge da abuna guda hudu nabari gashi naga yadawo guda daya, kokuwa rashin taibiyyar Zaki nunamin, bamagana nake makiba Kika tsaya kina kallona?"
Gyara tsayuwa nayi nace
"Inace nafisa takiraka sunzo itada Yaya shine nabasu sukasha"
"Dan ubanki banace karki daukarmin abunaba, tab asheyau zakici uwarki tunda bakida mutunce shegiya yar'iska mara tarbiyya wallah......." Katseshi nayi da fadin
"Kaga malam gaskiya kadaina zagarmin iyaye don bafin iyaye sukayiba haka kawai akan wani abun naira dari da hamsin karunga zagina wallahi bazan dauki wannan wulakancinba nagaji gaskiya haka kawai kamaidani kamar wata jaka saidai na dafa maka abinci kaida wannan yar'iskar matar nabaku Babu godi bare nagode to wallahi nagaji gaskiya da sake" nakarasa tare da rike kuguna Ina jiran amsarshi, baisan dama cike nake dashiba akan rabani da masoyina da yayiba yau zuciyata asama take jiran kowana nake yayimin narama don bazai yuwuba ahadamin zafi goma da ashirin.

*Toh su nafisa anyi bakifa fans kunajin yadda take*🙊 *bazan karasaba naga anty Fareed Auwal da sayyada da Ayshat zazzau na kallona karnasha*🤪

*Comment*
        *&*
*Share*

*By*

*Khadeejah (Ummu Fu,ad & Afnan)*

*👽🔥ALJANA AISHA👽🔥*

https://www.facebook.com/groups/1569379426621615/

*~✍🏽✍🏽GOLDEN PEN WRITERS ASSOCIATION✍🏽✍🏽~*

*~We are bearer's of so golden pen🖊️~*

*~we write assidiously perceive no pain~.*

*~So magical,Our creative golden pen✍,behold our words.~*

*~A product of our pen🖊️,savour our words, for it will cause you no pain.~*

*🤣🤣🤣🤣 kai jama'a kowanne group maganan kenan bana marubuta kowa labarin Aljanu har damasu cewa last year aka gama SANADIN KAZA ,SANADIN KAZA this year kuma aka dunga aljana kaza sanadin aljana 🤣🤣🤣🤣🤣 so funny to ina da tambaya wai maiyasa wanda suke rubuta labaran soyayyar ,yaki d.s ba ayi magana bah sai wanna nan ...to ba lallai ba dole idan zaki karanta to idan ba zaki karanta bah sai ki\ku bari akwai dubunku masu karantawa ...haka kwanaki aka gama cewa MAMA GEE tana kwafan littafin BILLY ABDUL a Littafinta na RAINA KAMA   Dan kawai Ku hada fada sai suka baku kunya yanzu kuma wai masu rubuta labarun aljanu suna kwaikwayon wacce ta rubuta FATALWAN MIJINA duk da bansan littafinba to mun

kwafa ai abun alfahari ne ga marubuciyar ta samu maso kwafan labarinta dai dai yanda tayi ...wallahi mutane mu gyara HASSADA babu kyau kuma HASSADA ga mai rabo takine .... Yan uwana marubuta karku kula readers Dan wasu readers din ba a iya musu ....kace na Kudi a zage danginka kace kyauta baka tsiraba🤦🏻‍♀️Allah ya kyauta Ameen*

95-100
A hankali ya bude idonsa yayi tunanin ganinsa  a jije sai yagansa akwance a gefen Fatima

Mtsww ashe mafarkine

Kusan haka amma zaka gane halanne idan ka gyara halinka ko kaci gaba

A zabure ya juya yaga mai magana

Wata matace zabgegiya kayan jikinta kadai abun tsorone balle fuskanta

Karkarwa yake yi yana naiman maboya

Daina wahalar da kanka idan kayi abunda nace babu abunda zanyi mah

Banda mazurai babu abunda yake

Nafarko ka wadata gidanka da abinci sanna ka kula da matarka kuma ka daina abuta da sani Dan burinsa ka saki matarka ya aura ...idan baka yardaba zo muje kagani

Zuwa yanzu yadan rage tsoron

Muge ko

Ahankali ya sauko a gadon yabi bayan matar

Suna tafiya yana Satan kallonta

Karka damu babu maiganina sai kai

A haka sukaje amma babu kowa a wajan... Can ya hango sani yasa waya akunne alamun waya yakeyi ko kuma kira  zaiyi

Wayansa yaji yana  ringing yana dagawa yaga sani kuma basu da nisa ko bai gansa bane

Bai ganka ba saboda na tareka kadau wayan karka nuna kasan nufinsa

Dauka yayi bayan sun gaisa sai Yusuf yace yanayin meyene

Gyara tsayuwa sani gayi yace kaga shegiya yanzu kuma ina tsaye abayanta nasata dole tayimun girki kaga bulalan hannu na kuwa sai ka tausaya mata

Daskarewa yayi Dan mamaki

Da fatan baka ragawa Fati

Eh kawai iya cewa ..zuciyarshi banda tafasa babu abunda yake

Bayan sun gama waya sani yace

Wawaye kuje kuyita dukan matanku har Ku sakesu na aura na hada danawa nayi tattalinsu tunda kunzama sukayen mazaje

Yusuf Dan bacin rai jikinsa har karkarwa yake yunkurawa yayi zaiciwa sani uwa

Sai ji yayi anyi sama dashi

A tsakiyar falonsa aka direshi

Nan ALJANA AISHA ta bayyana masa kanta sanna tayi masa nasiha mai shiga jiki sanna tace karya Bata sani ya barsa

Nan tace anjima zata dawo

Bayan tafiyanta ya dafawa Fatima abinci sannan ya daura mata ruwan zafi

Tadata yayi tayi kwanka yaciyarda ita sanna ya naime yafiyarta kuma ta yafemasa nan suka dasa sabon soyayya

*********

Su saratu sun dako kowa daya tashi sai yayi hanyan gida amma daga kaje sai su dawo a guje

Ko meye abakin kofan oho

*YAWAN COMMENTS YAWAN TYPING*

*Aishmar (Queen Indo)*

*🙆🙆 RAYUWATA CE*🙆🙆

*Na*

*Khadeejah Sani (Journalist)*

*🌈KAINUWA WRITERS✍🏼 ASSOCIATION*🤝🏻

```{United we stand and succeed;Our ambition is to entertain & motivate the mind of readers}```

https://www.Facebook.com/kainuwawritersassociation

*🅿37 _ 38*

"To wallahi zanyi Miki kashedi na farko Dana karshe duk ranar da Kika Kara shiga harkata acikin gidan Nan wallahi saina kusan kasheki ke Allah idon kikayi Wasa saina ballaki baras Kuma nazauna lafiya tunda ke kikazo har gidan mijina Kika sameni idon kunne yaji jiki yatsira banza mara tarbiyya, jahila, mara ilimi mara tunani kawai"
Ina kaiwa Nan najuya nayi kitchen don nayi abinda ya fiddoni,

Kallo tabini dashi na mamaki tare da tunanin abinda zatayimin,
Fitowa nayi zanje daki don namance wayata Kuma nasan za,a iya kirana inacan tunda muna cikin magana da Innarmu kudina yakare nasan kuma zata iya kirana,
Fitowata nayi nazo tsakiyar falon kawai sainaga mata agabana tawani rike kugu tafara magana,
"Ke wato kinsami wuri harni Zaki kalla kifadawa magana to wallahi yau Sai kingane shayi ruwane" kafin na Ankara kawai naji ta daukeni da wani Mari aikuwa kafin ta sauke na maida mata martani Nan muka fara fada,
Dukanta kawai nakeyi har nasamu nakaita kasa jibgarta nake Kuma Babu inda nake duka Sai breast dinta don nasan saitafi Jin zafin hakan,
Faskarta nasamu nafara kwadawa Mari ganin takalmin dake kafarta agefe nayi don haka nayi saurin dakkowa tare da fara buga matashi ta kowanne bari gashi Mai shegen tsini aikuwa ihu takeyi tana neman dauki nidai kilarta nake kamar nasami jaka Saida naji muryanta baya fita sosai sannan na kyaleta gashi fuskarta duk ta kunbura harda jini ajikinta don dukta fashe,
Mikewa nayi nakoma kitchen don dama indomi nadora nasan kuma yanzu ta dahu don haka naje ajuyota afaranti nayi daki,
Tana Nan kwance inda nabarta Sai kuka take nashige daki nazauna tare da sauke ajiyar zuciya nace
"Ohh ni nafisa nashiga uku Yaya zanyi da wancan mugun idon ya dawo wayyo Allah nah yau nasan kashenine kawai bazai yiba don wallahi nasan sainasha duka,
Nashiga uku ni Nafisa bansan Yaya zanyiba" tagumi nayi nama kasa cin abincin Sai can nace "umm gwarama nasamu naci kafin yadawo nasan kila nudacin wani abun sai gobe don idan nasha duka ba iya aikatuwa zanyiba" wannan maganar da nayice tasakani faracin indomin Amma badon inasoba haka nayita turata har Saida naga nacinye sannan nasha ruwa natashi nayi wanka don Ina fashin sallah,

Sai wuraren karfe biyar da rabi sannan naji karar motarshi nanfa cikina yafara kullewa mikewa
```

nayi da sauri na kulle kofata nasaka mata makulli nadawo nazauna harna fara sharar kwallar tausayin don nasan Dole natausayawa kaina tunda na Tana waccen abar natabo masifa,

Kwance take afalon yadda nabarta tanata kuka,
Shigowa yayi cikin yin sallama Amma ganinta kwance yasakashi karasawa da gudu Yana fadin
*Ohh my baby jikinne haka haryanzu shiyasa inacan inata tunaninki wallahi shiyasa nayi sauri nadawo kokai amarya bazan tsaya........"maganar ce tatsaya ganin yadda fuskarta tayi yafara jefo mata tambaya yace
"Meya sameki haka baby Dame kikaji wannan ciwon haka?" Yana fada tare da daukarta baki Daya yayi daki Da ita,
Wani sabon kukan tasaki tare da fadin
"Matarka ce tayimin haka kamani tayi taita dukana Babu abinda nayi mata wallahi Kuma bazan yaddaba saika ramamin don bazata dokeni abanzaba" tana fada tana Kara fashewa da kuka,
Kallonta yakeyi cikin bacin rai yace
"Kina nufin Nafisa ce tayi Miki haka don taga bakida lafiya aikuwa wallahi tatabo masifa da Bala,i don yau saita gane kuskurenta saboda rashin mutunci zata kamaki da duka haka kamar ankawo mata jaka tab bari kiga" ajiyeta yayi tare da dakko wata sabowar bulala da daman sabodani yasiyota yafara niyyar fita Daga dakin tayi saurin katseshi tace
"Waime zakayi mata"
"Zanje na rama Miki dukan da tayi mikine yanzun Nan"

"Wai kana nufin idon kadoketa shikenan" tana fada takara fashewa da wani sabon kukan dawowa yayi wurinta yazauna yace
"Fadi abinda kikeso nayi mata wallahi saina yimata duk hukuncin da kikeso?"
Kukan takeyi sannan tafara magana tace
"Ninagama alamar sonta kakeyi inba hakaba yaza,ayi kawani rabu da ita taci gaba da zama agidan Nan bayan abinda tayimin ai Wallahi kyau daga yau tagama zama kawai ka korata wannan kangon gidan nasu sannan ka fara zaneta kafin ta tafi sannan wannan tsohuwar babar tata tayi jinyarta kamar yadda tabarka da tawa"
Shiru yayi Yana tunanin maganarta kumafa gaskiyace don haka yamike tare da dakko takarda da biru yafara rubutu saigmda yagama sannan ya kalleta yace kiga abinda na rubuta mata,
Karba tayi tafara karantawa afili kamar haka,
*"Ni Adam nasaki matata Nafisa saki Daya saki biyu saki uku na haramtawa kaina ita har abada sannan idon tasami miji tayi aurenta Bata da iddata akanta don bana sonta Kuma bana kaunarta Babu abinda zaisa tayi iddata Allah ya had a kowa da rabonshi na Alkairi Ameen"*

Tsalle tayi tare da rungumeshi Tana murna da sakar Masa kiss ta kowanne bari,
Dariya yayi yace
"Amma nasan yau za,a bani kyauta ta musamman tunda na Kori waccen gakar matar ko?"

"Wani abunma saikaje kagama aikinka kadawo sannan kaidai tashi kaje"

Fitowa yayi yazo dakina Ina can inata tunanin buga kofar yafara Amma naki budewa yanata masifa harda cewa zaisa aballeta don wallahi yau saiya zaneni nidai Ina zaune inaji banyi yunkurin tashibama balle na bude kofar,

Haka yasta yanata masifa har akayi magriba dakyar na tashi nakara kyara jikina sannan nadawo nazauna tafiya yayi don zuwa masallaci Kuma nasan idon yatafi Sai bayan sallahr Isha,I take dawowa don haka inajin ya fita nafito don nadauki wayata Dana Bari a kitchen Ina shiga nadauka nadawo nashige daki,

Ashe abinda namanta bankulle kofarba Ina zaune har naji dawowarshi yashiga dakinshi ban ankaraba kawai Sai ganin anturo kafar dakina aikuwa namike tsaye Ina dafe kirji don bakaramin kaduwa nayiba kaina yayi nafara ja dabaya kawai yafara zabga min wannan bulalar Ihu nafara inaja da baya harnakai karshen bango don haka  nazauna awurin na magiyar yayi hakuri dukana kawai yakeyi Babu ko sassautawa.

*Comment*
*&*
*Share*

*By*

*Khadeejah (Ummu Fu,ad & Afnan)*

*🙆🙆 RAYUWATA CE*🙆🙆

*Na*

*Khadeejah Sani (Journalist)*

*🌈KAINUWA WRITERS✍🏼 ASSOCIATION*🤝🏼
```{United we stand and succeed;Our ambition is to entertain & motivate the mind of readers}```
```

https://www.Facebook.com/kainuwawritersassociation

*🅿39 _ 40*

Saidai yayimin dukan tsiya Wanda ko kukanma da nakeyi nadaina saidai nayi kwance Ina ziraran hawaye sannan yafara magana yace

"Kega Yar iska Zaki kamamin mata kiyita dukanta ubanme tayi Miki dazaki doketa kin kallo yau ko fita bamuyi tareba kwance nabarta Babu lafiya shine Zaki doketa, saboda bakida mutunci to inaso kisani zamana dake bazai taba yiwuwaba ahaka don haka ki tattara yanaki yanaki kibarmin gidana Daman kayan daki da kujeru Dole aka sakani nasiya Miki don haka nawane ba nakina ki tattara duk abinda kikasan nakine kibarmin gida kafin naje masallaci nadawo wallahi idon Kika yadda nadawo nasameki Sai jikinki yakara fada miki, kije kikoma wannan kangon naku nasakeki saki uku" hafada tare da wallomin takarda, ai suman zaune nayi tare da sake sabon hawaye dakar nabude bakina nace

"Wayyo Allah nah nashiga uku, yanzu Yaya abinda kayimin ka kyauta kenan baka tsaya kaji abinda ya hadani da itaba zakace kasakeni don Allah kajanye wannan kalmar wallahi nayima alkawarin bazan Kara fada da itaba please kitaimaka min bansan me zanfawa Innarmu ba idon naje gida don Allah kayi hakuri kajanye sakin da kayimin nashiga uku ni Nafisa wannan itace kalar *RAYUWATA* nikuma kalar tawa kaddarar kenan" nakara fashewa da kuka juyawa yayi Yana niyyar fita yakara juyowa yace

"Nafada Miki kafin naje masallaci nadawo kisan inda dare yayi Miki don wallahi nadawo nasameki bazaki tabajin ta dadiba wallahi saina kusan kasheki sannan na wullar dake waje nafada Miki"

Fota yayi yabarni Nan kwance kuka nakeyi narasa mekemin Dadi nidai ba farin ciki nakeyi da faruwar hakanba Kuma bana bakkin ciki da hakan, Abu Daya dai nasani shine tsoran Innarmu yasakani naketa wannan kukan bansan abinda zanje nafada mataba,

Ganin danayi lokaci na tafiya yasakani tashi nadauko jakata nasaka kayana kala uku sannan na dakko ragowar kudina na wurin Yaya Muslim nasaka ajaka tare da wayata nasaka hijjabi nafito,

Afalo na taddata kwance tacanja kalar kayan dake jikinta tana wani danna waya tana yatsina fuska kallona tayi sannan ta tintsire da dariya tare da nunani,

Harnayi kofar falo zanfita saina juya na kalleta nace

"Uhmm dariya kike yimin ko nagode sosai da abinda kikayimin Amma inaso kisani dama basonshi nakeba Kuma yanzu hakan data faru bakaramin Dadi yayiminba Amma inaso kisani ninasan makomata yanzu kekuwa baki saniba saidai yayita jaguleki ya Gama lugwigwiceki ya Gama anfani dake sannan yabarki ya auri wata wadda yakeso don wallahi nasan Dole Sai anyi haka na tabbata bazai taba zama dakeba saiya auri wata wadda yakeso kekuma yarabu dake yagama anfanuwa dake, Ina tausayawa rayuwarki da kike yawon bin mazan wasu sannan duk inda kikayi kece abar dariya baniba kalleki saboda tsabagen bin mazan da kikeyi gashinan Babu cinya balle karfata duk kinbi kinkare, Ina Mai baki shawarar kituba kikoma ga Allah kibar abinda kikeyi don Babu inda zai kaiki Sai hallaka, Allah ya shiyaki"

Ina kaiwa Nan nayi waje donnaji anyi sallama daga sallah karyazo yasameni nayi waje tafiya kadan nayi nasami adaidaita sahu tsaidashi nayi nace yakaini dorayi wajen gidan sarki,

Take muke acikin daidaita inata kuka Mai mashindin kallona yaketayi tacikin madibi har mukaje layinmu kwatance nayimasa yakaini har kofar gida,
Kudinshi nabashi sannan nashiga cikin gidan tare da sallama,
Zaune nasami nafisat da mahbub sukayo kaina suna murna tare da yimin sannu nafisa ke fadin
"Oyoyoyo antynah sannu da zuwa yanaganki haka lafiya?" Ai tana fadar haka nafashe da kuka tare da zama agurin Innarmu ce tafito cikin sauri tare da salati tace
"Kekuma Saida dare ake ganinki Kuma Daya zuwa Sai kuk......." Bata karasaba saboda yadda taga fuskata duk atashe da idona duk yabi yakunbura karasowa tayi tana fadin
"Nafisa meya faru lafiya meya sameki haka?" Duk tambaya take jaro min amma nakasa amsa guda Daya daga ciki Sai aikin hawayen dake zubomin afuska, shiru tayi sannan ta Mike tadauki jakar Dana yarda tayi daki ina nan zaune har Yaya yashigo yasamemu mahbub Shima kukan da yaga inayi yakeyi nafisa Kuma tazubamin idanu itama idon cike da hawaye tana kallona,
Kallonmu yayi Yama rasa abinda zaice Sai zuwacan yace
"Meya faru haka kikeyi me akayi muku ke meyafaru?" Yafada Yana kallona,

Kallonshi nayi sannan na Mika Mai takardai hannuna tare da Kara fashewa da kuka salati ya dauka Yama kasa bude takardar Sai zuwacan ya bude tare da karantawa afili hakan yasa nafisa dake zaune taji aikuwa tanajin abinda yace tamike tayi dakinta da gudu tana rusa kuka kamar ranta zaifita Wanda baisaniba Sai ya rantse ita aka aikowa da sakin,
Innarmu ce takara fitowa tana fadin
"Haba nafisa yazakizo kisamu gaba kiyita kuka batare dakin fada Mana abinda yake faruwaba" kallon yayanmu tayi tace
"Au ashema kashigo gatanan tun magriba tazo taki fadar komai gashi Nan yanzu har takwas da rabi tayi tana Nan zaune inda take" kallon Innarmu yayi cike da tausayi sannan yayi mata bayani kallona tayi tace
"Allah ya kyauta tashi muje daki kiyi wanka ga ruwan zafican" mikewa nazoyi nakasa don dukkan jikina ciwo yakemin hakan data ganine yasakata kamani mukayi daki mukabar Yaya Nan tsaye don yagane dukana yayi kafin nataho ga fuskata Nan duk tabi ta kunbura,

Bangaran nafisa kuwa tana shiga daki tadauki wayarta tafara neman wayar babansu tana shiga yadauka tare dayin sallama,
Kukan da takene yasakashi yin shiru sannan yace
"Mamana meyafarune haka kike irin wannan kukan?"
Cikin kuka tafara fadin "shikenan yajazamin baba yanzu za,a sakeni Nima sallahi ya saketa nasan bazai cigaba da zama daniba Yaya yasaki anty Nafisa nashiga uku"
Cikin firgici yace
"What? Mekikace yasaketa garin Yaya yaushe metayi Masa?"duk yajera mata wadan nan tambayoyin,

Cikin wani kukan tace
"Wallahi baba bakaga yadda yayi mata dukaba duk fuskarta jini yabata takunbura tazo gidan tanata kuka, munyi mata tambayar duniya amma takiyi mana magana saida yaya yadawo sannan tabashi takardar yana dubawa yaga sakinta yayi kuma saki uku" tana kaiwa nan takara fashewa da wani sabon kukan,
Shirune ya ratsa wayar zuwa Dan lokaci sannan yace
"Shikenan ai kiyi hakuri Bari nakirashi naji ba,asi" kashe wayar yayi,
Kiran wayar yayan yaketayi Amma tashiga bai dagaba don haka yafadawa Mama abinda ke faruwa mama harda kukanta don abin yabata mata rai baba tashi yayi yace
"Bari naje gidan nashi nasameshi naji ba,asin abinda yafaru" Allah ya kiyaye hanya tayi masa yatafi.

Bangaran su yayan kuwa abinda yasa baiji Kiran wayarba tunda yadawo daga masallaci ta tsareshi a falo da rigimar itafa saiya aureta don tagaji da wannan rayuwar (kunsan nafisa tayi mata zancen zai auri wata ya koreta shiyasa ta canja shawara tace ya aureta)
Hakan data fada kuwa ba karamin murna yayiba Nan suka Gama yanke hukuncin gobe zata koma gidansu afara Shirin biki,
Rigar dake jikinta ya daga tare da tura hannu cikin rigar Yana taba bobos dinta don bakaramin burgesho sukeba dondaima bawani girma garesuba yadda yakeso yaji sun cikamasa hannu,
Yade bakinsu sukayi guri guda Yana tsotsar harhsenta kamar yasami sweet nandai suka fara lulawa duniyar tasu cikin hakan sukaji ana kwankwasa kofar falon don Allah yasosu akulle take tashi yayi Yana tsaki yakoma yazauna duk yafita daga hayyacinsa itacema take cikin nata hankalin don haka tamike ta tafi tana fadin
"Wayene muna cikin Jin dadinmu yazo yaruguza mana" bude kofar tayi tare dabin dattijon da kallon rainin wayo tajuyo tace
"Baby taso kaga wani tsohone yazo kila Yan neman maulane zuka sallameshi please" tafada tana komawa cikin falon,
Tasowa yayi Yana cewa "waye yake neman shiga hakkina Ina gab da lulawa duniyar datafimin kom..........." Maganarce ta tsaya wuri Daya lokacin dayaci Karo da baba hatta numfa shinsa kasa daidaitashi yayi saboda tsoro da fargaba tare da tunanin mazai biyo baya.

*Comment*
*&*
*Share*

*By*

*Khadeejah (Ummu Fu,a & Afnan(*

[9/21, 7:47 AM] Hayat: *🙆🙆 RAYUWATA CE*🙆🙆

*Na*

*Khadeejah Sani (Journalist)*

*🌈KAINUWA WRITERS✍🏼 ASSOCIATION*🤝🏻
```{United we stand and succeed;Our ambition is to entertain & motivate the mind of readers}```

https://www.Facebook.com/kainuwawritersassociation

*Masoyana kuyimin afuwa na rashin jina kwana biyu da kukayi, kusan jiki akace da jini Sai ahankali, gashi Nan kunsamu nayi amma saidai nace kuyi hakuri nasan yayi muku kadan babu yawa ayimin afuwa my fans*

*🅿41_42*

Bayan nayi wanka nakwanta zazzabi ya rufeni Innarmu ce tahadomin tea tare da zaunawa bakin gado tace
"Tashi kisha tea da magani ko kyaji Dan kwari ajikinki" tashi nayi da wuya tare da jingina jikin filon da Innarmu tasakamin na jingina sannan nafara magana cikin hawaye nace
"Don Allah Innarmu kiyi hakuri karkiyi fishi Dani wallahi balaifina bane shine ya........" Dagamin hannun da tayine yasakani yin shiru Ina raba idanu tafara magana tace
"Banason Jin abinda Zaki fadamin kawai Ina Kara yimin addu,a Allah yasa hakane yafi mafi Alkairi, ni bandauki wani abuba kawaidai nadaukeshi amatsayin ke wannan shine irin naki kaddarar Kuma Ina rokon Allah yabaki ikon cinyeta, don haka banason Jin komai kawai kisha tea din nan da magani kwanta Allah yabaki lafiya"

Bangaran Yaya kuwa Koda yashiga daki yasami nafisa zaune tana kuka yazauna kusa da ita
```

tare da fadin
"Meyafaru Kuma kike kuka"
"Yaya don Allah kayi hakuri da abinda Yaya Adam yayiwa nafisa nasan bai kyautaba amma kayi hakuri karkace zaka rabu dani wallahi ina sonka bazan iya rayuwa babu kaiba yayana please katausaya min Yaya" takarasa tare da fashewa da wani kukan,
Jawota yayi jikinsa yara lallashinta yace
"Wayace Miki zan iya rabuwa dakeba nima inaso kisani laifin wani bazai shafi waniba don haka nidake mutu karaba takalmin kaza kinji dear nah bar kukan nan"
Hakuri taci gaba da bashi akan abinda akayi musu tunda tasan Dole zaiji takaici cikin hakan kawai ya hade bakinsu, nan suka lula wata duniyar,

********************

Murmushi baba yayi tare da fadin
"Inason magana dakaine kasameni yanzu agida Ina jiranka" Yana Gama fadar haka yajuya yayi gida ikon Allah neh kawai yakaishi gida,
Mama na zaune taganshi yashigo zama yayi kusa da ita tare da dafe kanshi sannan yafara salati don da Yama mance da yinshi saikuma yafara "innalillahi wa'inna ilaihirraji'un Allah karabamu da mugunji da mugun gani, wannan musiba da yawa take Allah kabani ikon cinye wannan jarrabawa data tunkaroni, dama haka duniya takoma ace kahaifi yaro amma yazo yayimaka abinda bashike nanba" shiru yayi Yana dafe da kanshi kallonshi mama takeyi bakinta cike da tunanin mezatace daurewa tayi yace
"Wai babansu meya farune haka naganka duk afurgice lafiya meya faru don Allah kayimin magana naji" cikin sanyin murya ga hawaye ya fara Bata labarin abinda yagani dakuma abinda yaji har zuwa karshe,
Itama salatin takeyi tana tafa hannu Tama rasa abinda zata fadi Sai kuka data fashe dashi,

Suna cikin haka saigashi yashigo yanata dukar dakai ya zauna daga gefe can nesa dasu Babu Wanda ya kulashi har tsahon mintuna,

Sannan Bab yace "tashi kabani guri gobe da safe kazo wallahi idon har kayarda na nemeka dakaina saina tsine maka nahuta kaji nafada maka"
Mikewa yayi jiki Babu kwari yakoma gida Yana zuwa sailuba ta mantar dashi damuwarshi don batason taga Yana wani tunani Amma adaren suka Gama yanke shawarar gobe zaikaita gidansu Sai abin yayi sanyi sannan zaizo neman aurenta, aikuw abin yayi mata Dadi sosai,

Washegari da sassafe yadauketa yakaita gida tare da kayanta sannan yayo gidansu don amsa Kiran baba,
Samun mama yayi zaune itada baba sunsaka kayan Kari agaba suna kallo sunkasa tabawa ko kadan tsugunnawa yayi tare da gaidasu Babu Wanda ya kalleshi balle yasa ran zasu amsa Masa,

*******************

Bangarena kuwa zazzabi yayimin ruf Sai barin sanyi nakeyi gashi nasha maganin Amma kamar banshaba ahaka nakwana da zazzabin bacci kuwa saidai barawo ban yishiba yadda naga rana haka naga dare,

Da asuba haka nake kwance nakasa ko tashi gashi inaso nashiga toilet duk da ba sallah zanyiba amma inason shiga don nagyara jikina, taimakamin tayi nashiga hakama dazan fito Saida ta taimakamin hakan yasa tafita takira Yaya tace yazo yadan dubani,

Dubani yayi sannan yafira yace zaije yasiyo ruwa don saidai akaramin tunda jikina yayi sanyi da yawa gashi ko tafiya bana iayawa,

Haka aka karamin ruwan nanne nasami bacci yadaukeni bansan me yakara faruwaba don nayi bacci sosai bantashiba Sai wurin azahar,

******************

Mamace ta kalleshi tafar magana cikin fishi tace

"Kai yanzu abinda kakeyi kayi daidai kenan yanzu kasami yarinyar mutane kayi mata duka sannan kasaketa Kuma saboda hauka saki uku, Koda yake banga laifinkaba tunda har kayi girman da kake ajiye karuwa acikin gidanka Kuma na tabbata yarinyar Nan Mai hakuri tana gani Amma Bata tanka mukuba shine duk da haka Bata yiba ka saka mata da saki, wallahi kabani mamaki bantaba tunanin zaka iya yiwa nafisa hakaba kodan mahaifiyarta yadda ta daukeka, ta maidaka tamakar danta batason abinda zai Bata maka Rai duk abinda tasamu Kaine kaitake kawowa tunkafin ta haihu har bayan ta haihu Bata dainaba Amma shine kasaka mata da wannan mummunan abun, wallahi kabani mamaki Kuma kabani kunya..." Batakai karshen maganarba ya katse mata da cewa

"Mama wallahi wanna yarinyar Bata........." Ai baimakai karsheba taji ta wullo Masa cup din dake kusa da ita daga gani kasan Wanda zatasha tea ne dashi.

*Comment*

*&*

*Share*

*By*

*Khadeejah (Ummu Fu'ad & Afnan)*
[9/21, 7:49 AM] Hayat: *🙆🙆 RAYUWATA CE*🙆🙆

*Na*

*Khadeejah Sani (Journalist)*

*🌈KAINUWA WRITERS✍🏼 ASSOCIATION*🤝🏻
```{United we stand and succeed;Our ambition is to entertain & motivate the mind of readers}```

https://www.Facebook.com/kainuwawritersassociation

*🅿43_44*

"Okay rashin mutuncin naka yakai haka dama bansaniba ina magana kana katseni lallaine wuyanka ya isa yanka, to wallahi kaji nayi rantsuwa indai wannan halayyar ta banza kaga zaka iya babuni babukai saina hakura dakai kwata kwata don bazai yuwuba ka doramin lalurar da Allah bai halittoni da itaba, inbanda Kai sakaraine saika Duba kagani cikin gidan nanfa Kaine babba abinda kannenka sukagaa kanayi shifa zasu dauka bandama dama Allah yayi ba halinku Daya da babanaba datuni ka koya Masa wani mugun halin gashi Nan yaron arziki yanacan yanata Sana,arshi baidamu da wani shashaciba, wallahi tunba yauba nake zarginka Amma nabar abin acikin raina kawai don karna fada kace natakuraka duk da nasan kanama fada, to inaso kasani insha Allah bazan sake saka bakina cikin wannan shashacin nakaba kaje kayi duk abinda kaga dama, Kuma Ina Nan inafadawa Allah akan Allah ya sakawa wannnan yarinya daka cuta ka saketa, kilama ka kulla mata wahala nasan dawuya idon baka cusa mata cikiba to wallahi indai hakan yafaru dolenka ka dauki nauyinta komai har zuwa lokacin dazata yaye abinda ta haifa, waima duk ba wannanba metayi Maka kayi mata wannan cin mutuncin saki harda duka saboda hauka?"

Dafe yake da baki tun lokacin data wulla Masa cup,
Zare Ido yakeyi Yana rarraba idanu Yama rasa abinda zaice Saida ta Kara daka Masa tsawa sannan yafara inda inda Yana fadin
"Ma...ma....umumum....mama dama....dama..tun..." Wata tsawar ta daka Masa tace banason rashin mutunci inayi Maka magana kanawani kame kame to bari nakirata naji Kuma kaima kaji agabanka" daukar ways tayi tare da Kiran Innarmu jin wayar tayi akashe don haka takira ta Nafisa dauka tayi tare dayin sallama sungaisa mama tace
```

"Ke kaiwa mamana wayar zamuyi magana"
"To mama" dakin tanufa don dama tana kitchen din tsakar gida,
Samun Innarmu tayi tana gayaran dakin nan suka gaisa sannan tace
"Inna bacci anty takeyi?"
"Eh kinganta tunda aka saka mata ruwa don jiya Bata rintsaba kwata kwata shine take bacci ai naji dadin yadda baccin ya dauketa"
"Ayyah Allah sarki Allah yakara sauki gashi nan kuwa harta rame" Inna na niyar yin magana aka Kara kiranta dauka tayi tare da fadin
"Mama wallahi kinganta babu lafiya yanzuma bacci takeyi yayane yayimata katin ruwa, don jiya haka ta kwana Babu bacci"
"Ayyah Allah sarki mamana Allah yabata lafiya ina innar taku?"
"Gata kusa Dani"
"Bata zamuyi magana" mikawa Inna wayar tayi tare da fadin ga mama,
Tana karba tajuya tabar dakin gaisawa sukayi sannan mama tadora da fadin
"Saikuma mukaji wannan abun Daya faru babu dadi, yaro ace kahaifeshi amma baka haifi halinsaba Wal........." Saurin katseta Innarmu tayi tace
"Ai acikinsu baza,a iya banbance Mai gaskiyaba Sai anzauna Yaya, don Allah kidaina fadar haka, wannan wata kaddarace da Allah ya dora mana saidai kawai Allah yabamu ikon cinyeta"
"Ameen ya Allah, Daman inason nayi magana da mamanane Kuma naji ance Bata lafiya meke damunta haka?"
"Zazzabine dai takwana dashi amma yanzu bacci take Bari na tadata saikuyi maganar"
"A,a karki tasheta rashin imanin Sai yayi yawa yarinyar takasa bacci yanzu tasamu tanayi Sai atadata barta kawai, amma nace tafada Miki abinda ya hadasu kuwa?"
"A,a wallahi banma tanbayetaba ita Kuma zata fadamin nace tabarshi Allah ya kyauta nasandai itace tayi Masa wani laifin don mai sunan manya bazai mata wani abuba Sai takaishi karshe, shiyasa nake rokon don Allah kuyi hakuri abawa babannasu hakuri yayi hakuri yarinyarce akwaita da zuciya bansan meke damuntaba hartaje tayimasa abinda hakan ta......." Katseta Mama tayi da fadin
"Wallahi tallahi kinji nayi ranstuwa nasan mamana keda gaskiya bakowa don na tabbabata bazatayi Masa komaiba shinedai mugu azzalumi Mara inamani dayayi mata wannan mummunan abun Wanda ko makiyinka baka fatan ayiwa haka, nidai inamai Kara Baku hakuri akan abinda yafaru don wallahi da ace Adam yayi shawara Dani dabai aikata hakaba Amma yaron yanzu halinsu saisu don Allah kiyi hakuri Kuma insha Allah anjima zanzo Naga yanayin jikin nata sainazo"
Tana kaiwa nan takashe wayar tare dakai dubanta ga Yaya Wanda cikinsa ya duri ruwa don duk atunaninsa za,a bani wayar nafadi abinda yayiminne Amma Sai yaji yadda innarmu ke kareshi, Sai anan yayi nadamar yimin abinda yayi duk jikinshi yakara sanyi Yama rasa meke Masa dadi gabaki Daya don haka yayi shiru Yana sunkuye da kansa,
Mama kuwa takasa magana kawai Sai aikin kallonsa take babane ya daure yace
"Inaso kafadamin abinda ya hadaka da ita banason karya karkayimin ita don Dole naje naji daga bakinta karka yadda naji abinda kafadamin karyane idon naji haka ranka zaiyi mummunan baci"
Shirune ya ratsa dakin har mama tagaji tafara want sabon fadan don daman agidan tafi baba

fada sosai bama akan Tara ita Bata Wasa dasu sosai don batason sanyin da baba keyi musu,
Hakan daganine yasakashi fara magana yace
"Don Allah kuyi hakuri nasan nabata muku rai inamai neman gafararku daku yafemin, dafarko bayan bikinmu natakura Nafisa na hanata sakewa acikin gidan none dukanta zagi hatta abinci akwai abinda nake Bata akwai Wanda na hanata daukarmin saboda nayi la'akarine da gidansu don haka nake mata abinda naso, hatta lemo na hanata daukarmin kullum idon zan fita saina kirga abina hakama idon nadawo saina kirga"
Hakadai yayita Basu labarin kalar ukubar dayayita sakani Amma bai fada must maganar karuwarshiba har yazo lokacin dasu Yaya sukaje yadda mukayi dashi akan lemon Dana Basu sannan yadora da fadin
"Saboda nayi mata hakan shine jiya da yamma Ina dawowa nasameta ta fito da akwatinta guda biyu falo tana zaune Ina shigowa tamike tare da fara zagina Wai idon na haifi cikin hafsat da isah na saketa idon ba hakaba saitaga bayana a daren, nikuma danaga haka saina wucewata daki nayi wanka nafito zan tafi masallaci takara tsaremin hanya harda marina shine nikuma abin yabatamin rai nayimata duka nola saketa, Amma Ina Mai kara baku hakurin ku yafemin don Allah"
Babane ya kalleshi tare da share kwallah yace
"To naji wannan tatsuniyar taka Amma baizama lallai na daukaba, Abu na gaba Kuma wannan yarinyar dana gami agidanka wacece ita?"

Nanfa idon Yaya yayo waje yafara kame kame Amma saiya dake yace
"Baba wannan itace yarinyar da nakeson na aura"
"Wadda kakeson aurece Kuma zatazo gidanka da dare meya kawota?" Mamace tayi wannan maganar don haka yakara tsorewa Akan nada yace
"Munyi wayane da ita tajini cikin bacin rai shine tazo donta .........."
"Don tayima uawarka nace don tayima uwarka mutumin banza mutumin wofi" kukane ya kwacewa mama don haka tadaina magana tatashi tashige daki,
Babane ya kalleshi yace
"Kazo anjima zamuje gidan Adamun don Dole muje zamuyi magana Dani dakai da mahaifiyar ku"
To yace tare da barin dakin ammafa cikinsa ya duri ruwa don baisan ya zata kasanceba,

**********************

Nikuwa bangarena Koda matashi naji dama dama bakamar jiyaba saidai ciwon jikin kamar ankaro minshi haka na tashi,
Innarmu itace ta taimaka min nayi wanka sannan nasauya kaya nadawo nazauna afalonmu, mahbub dake zaune don yau babu makarantar boko tahfiz kuma anyi hutu bina yayi da kallo murmushi nayi masa nace
"My kani yau babu makarantar ne?"

"Eh anty babu anmana hutu Sai wani satin za,a koma"
"Jarabawa kukayi?"
"Eh gama report shite Dina can Bari nabaki kigani nayi ta biyu, dama uncle Yana Nan yazo yagani harda na school Dina asiyamin kekena dayace zai siyamin" surutu kawai yakeyi nikuwa tunda yace uncle hankalina yabar gunsa yatafi can.

*Happy jum'at Kareem to all my fans, friends, sisters & Brothers*

*Comment*
*&*
*Share*

*By*

*Khadeejah (Ummu Fu'ad & Afnan)*

*🙆🙆 RAYUWATA CE*🙆🙆

*Na*

*Khadeejah Sani (Journalist)*

*🌈KAINUWA WRITERS✍🏼 ASSOCIATION*🤝🏻
```{United we stand and succeed;Our ambition is to entertain & motivate the mind of readers}```

https://www.Facebook.com/kainuwawritersassociation
```

*💑💑 My mom inatayaki murnar fara sabon littafinki Allah yabaki ikon fadakarwa, Allah ya kara nisantaki da makiya, Allah ya kiyaye gabanki da bayanki mamana takaina, book dinki mai suna ITACE KADDARARMU Yana fadakarwa Yana nishadantarwa Allah yakaro Miki basira Mai yawa my mom SAMEERA HAROUN Ina sonki sosai sosai*

*🅿45_46*

Haka yayita bayani bansan me yake fadaba Saida naji nafisa nayimin magana sannan nadawo daidai,

Zaunawa tayi munata fira da ita muna cikin hakanne mukaji sallamar mama don haka tamike tayi waje da gudu tana murna nidai nabita da kallo don rayuwarta tana masifar birgeni tayi dacen miji Mai kaunarta gashi tana ganin iyayyenta dukkansu uhm Allah sarki ni ga maraici ga wannan kalar rayuwar danake ciki Allah ya hadani dashi *rayuwata ce* haka Allah ka rangwanta min haka Allah yasa na dandani farin ciki nima kodan na farantawa mahaifiyata rai,

Sallama sukayi adakin hakan ya daukemin tunanin danakeyi na amsa shiguwa tayi na saki fuskata Ina mata sannu da zuwa karasowa tayi dakin ta zauna Nan nagaidata tana tambayataba jiki nace dasauki,

Innarmu ce tashigo dakin sunata firarsu ta duniya nidai nayi tagumi Ina zaune ga jikina namin ciwo gakuma tunanin da yayimin yawa,

Muna haka har baba yazo Nan akayimasa iso yashigo yazauna gaidashi nayi nan yayimin ya jiki na amsa sungaisa da Innarmu Sai Kuma mukaji sallamar yaya,

Sallamar tasa danaji Saida gabana yafadi don bazan taba mance wannan mummunar muryarba shigowa yayi daki tare da zaunawa daga gefan kujera daga kasa Yana gaidasu yawani sunkuyar da Kai kamar mutumin kirki, Nafisa ce ta gaidashi nikuwa ko kallonshi banyiba na juyar da kaina Ina kallon gefe guda,

Hada Ido mukayi da Innarmu ta wullamin harara nagane abinda take nufi don haka nakara hade rai sannan nace

"Ina yini"

"Lafiya kalau ya jikin?"

Banza nayi dashi bance komaiba Sai baba yagyara zama yace

"Masha Allah gamu dukkanmu mun hadu Amma banga khalil ba Yana Ina haka?"

Innarmu ce tace "Yana kan hanyar dawowa don lokacin dawowarshi yayi yanzu" kafin baba yayi magana Sai mukaji sallamar Yaya yashigo dakinmu yakaraso don yaga takalman mutane Kuma yaga na maza don haka yagane ko babane yazo,

Shigowa yayi da sallama Nan suka amsa ya gaidasu dukkansu sannan ya zauna Nima sannu da zuwa nayimasa yace

"Ya kikaji jikin naki yanzu kindaina jirin?"

"A,a Yaya haryanzu inayi"

"Okay Allah yakara sauki ai Sai ahankali zakiji daidai"
Bangaran mama kuwa dadine ya isheta don atunaninta ko cikine gareni don haka tafara washe bakin tana fadin
"Ayyah sannu mamana Allah yakara sauki"
Ameen nace sannan dakin yadauki shiru can baba yace
"To naji abinda yafaru sannan inason ganin takardar Daya rubuta mata"yayane yamike yaje dakinshi ya dauko yakawo Mai nan baba yafara karantawa afili aikuwa mama naji abinda yace na bani da iddarshi takara rabga salati tana tafa hannuwa,
Saida baba ya nisa sannan yajuya bangaran Yaya yace
"Inaso ka maimaita abinda kafada Mana dazu agabanta don inason naji abinda ka aikata"
Nan yafara kame kame yama rasa abinda zaice ahakadai yafara bada labarin Daya bawasu mama agida dafarko nayi mamakin yadda yazauna yake fadawa iyayensa abinda ya aikata, saidai Kuma naji yacanja hanya yadda yaki fadin kawo karuwar tasa,
Yanata zubo musu karya akaina nidai inatajinsa kallonshi kawai nakeyi nama rasa abinyi har yakai karshe, Kuma maganar datafi ko wacce batamin rai inda naji Yana fadin
"Banyi niyyar sakintaba Amma abinda take fadamin aranar yasakani na saketa zagina tayitayi tana fadamin magana tana zagina harda idon na haifi cikin uwata da ubana nasaketa nikuma shiyasa na saketa, Amma don Allah kuyi hakuri kuyafemin nasan na aikata abinda ba daidaiba kugafarceni insha Allah hakan bazai Kara faruwaba"kallonshi kawai nakeyi nama rasa abinda zance don abin yabatamin rai juyowa baba yayi kaina yace
"Kinji abinda yace keme zakice"
Banyi niyyar fada musu komaiba Amma tunda haka yakeso Dole zan fadani Kuma bazan boye komaiba don haka namike zaune nafara Basu labarin duk abinda yafaru har zuwa yadda mukayi da karuwar tasa da fadan damukayi nayi nasara akanta dakuma dukan dayayimin da korata dayayi yabani takarda nakare da fadin
"Wallahi wallahi wallahi banyimai karyaba ko nafadi San Rainaba duk abinda nafada shine abinda yafaru Kuma wallahi tunda nake tare da Yaya bantaba zaginsaba kawaidai na fada masane karya Kara zagin iyayena don ba sa,anninsa bane"
Dakinne yayi shiru saini daketa kuka kawai zuwa can baba yace
"Kanajin abinda tace ko kanada ja akan hakan?"
Girgiza kanshi yayi kawai baice komaiba,
Hakan yasa mama fashewa da wani kukan tace
"Dama irin abinda kake aikatawa kenan irin rayuwar daka zaba kenan, haka kadinga cuzgunawa yarinyar nan dama, bawar Allah tana zaune dakai bisa biyayya amma kai kanuna kawuce kayiwa mutane biyayya, yanzu haka kazaba zina! Zina!! zina!!! Innalillahi wa'inna ilaihirraji'un........"kukane yaci karfinta tamike tayi waje batare data karasa maganaba ,
Innarmu ce tabi bayanta itama tana share hawayan tausayina,

Kallona baba yayi yace
"Allah ya saka Miki don nidai bazan taba nema maka gafarar abinda kayiwa marainiyar Allah bah, Allah kuma yabaki lafiya Allah yahadaki da miji nagari ba irin wannan shashashanba sakarai, Allah yayi miki albarka ya inganta rayuwarki"
"Ameen baba nagode Allah yakara girma" amsawa yayi da amin sannan yaciro kudi yamikawa

nafisa daketa kuka yace
"Mika mata tasiya wani abun Allah yakara sauki"
Yana fadar haka yayi waje,
Yayane yatashi yabi bayansa itama nafisa tamike tayi waje tare da mikomin kudin,
Komawa nayi na kwanta nayi kamar banganshi zauneba Saida yadauki lokaci sannan yamike zai fita kallonshi nayi nace
"Allah ya shirya mazinata yasa sugane hanyar gaskiya, Kuma inaso kasani duk abinda kayimin kaima zaka hadu da daidai dakai insha Allah, Kuma bazan taba yafe makaba akan zalincin dakayimin ba har abada, Kai inaso kasani wallahi da ace inada halin dazan kaika court da Babu abinda zai hanani kaika akwatarmin hakkina, Amma kaje kaida Allah, Allah yana tare dani kuma nasan saiya sakamin"
Ina kaiwa Nan nashige cikin daki nabarshi Nan tsaye da jajayen idanu Yana kallona,
Wake yayi yasamu harsu Mama sun tafi don haka yayi waje batare Daya yiwa Innarmu maganaba tana kitchen tana kallonsa Bata tanka Saba yafita,

Alhamdllh jikina yayi sauki don Ina samun kulawa daga bangaran Innarmu, Yaya, Nafisa, harda mahbub Shima ba,a barshi abayaba don ko makaranta yaje harda tsaraba yake kawomin Wai Shima kayana dubiya yake kawon,

Muna hakane nafisa tafara zazzabine nice na rakata asibiti gwajin farko aka fada Mana tana dauke da ciki na wata biyu,
Murna kamar me don lokacin Yaya yayi tafiya bayanan aikuwa nice nafara kiransa nafada Masa sannan muka dawo gida tanata rokona akan Wai karna fadawa Innarmu nace
"Tab wallahi wasama kikeyi ai kinsan kamar taji tagama" hakan yasakata muna shigowa tashige daki Wai ita kunya takeji,

Innarmu tayi farin ciki sosai don harda hawayenta tayi na murna tace
"Da babanku Yana Nan yau da bansan kalar farin cikin dazai yiba don yanason yaga jikokinshi Amma Allah baiyi zai ganiba"
Nima hawayen na share nace
"Allah ya gafarata Masa yasa yahuta"
Ameen ta amsa dashi,

*Agurguje please*

********************

Hakadai rayuwa taketa tafiya hankalinmu yakara kwanciya sosai don yanzu bana cikin damuwar komai saidai yawan tunanin masoyina tare da mafarkinsa da nake,

Ana cikin hakanne yau saiga mama tazo gidanmu yau kimanin wata hudu kenan rabonta da gidan tunda abun Nan yafaru Bata Kara zuwaba Sai yau,

Mungaisa sosai Nana sukafara fira da Innarmu hakan yasa namike zanje dakin nafisa mama tace

"Mamana zo nan wurinki ai nazo don sauri nakeyi"

Komawa nayi kusa da ita nazauna tafr magana tace

"Mamana inaso kiyi hakuri akan abinda yafaru Kuma kidauka kalar Taki kaddarar kenan, insha Allah bazaki kara komawa makaman ciyar taba, abunda ke tafe Dani wata alfarma nazo nema awurinki Ina fatan Zaki karbeta hannu bibiyu, nayi miki alkawarin insha Allah bazaki taba komawa gidan jiyaba" tana kaiwa Nan tayi shiru nikuwa Banda faduwar gaba Babu abinda nakeyi jin abinda tace Amma saina dake nace.  "Mama insh Allah bazan baki kunyaba indai zan iya abinda Zaki fadamin din" kamo hanuna tayi tafara fadin

"Inaso zama dake, inason kizama sirikata saidai wancan yakasa cikamin buri na, wannan daliline yasakani yanke shawarar Kara nemawa yarona Mai hankali da tarbiyya aurenki akaro na biyu, wannan bakowa bane face................"

*Ikon Allah wai akace nazaune yafadi, agaskiya abin Nan yabani mamaki na ganin yadda mutane ke neman kudi ta hanyar haramun, hausawa sukace kura dashan bugu gardi da kwace kudi, muda Shan wahalar zaunawa mubata wanni muna aikin typing Amma Sai asami masu Saida Mana book, agaskiya abin Nan yabani mamaki, sannan idon writers tace zata maida book dinta na kudi saikaji ana aiko mata da zagi da bakaken maganganu, wallahi abun Nan yabani mamaki tare da tunanin Anya kuwa wasunmu zasuga annabin rahama, saboda rashin imani irin na mutane wani yayi abunsa sannan kadauka kadunga Saida Masa, bayan bafinsa son kudin kayiba, mumafa munason kudin nan amma mukaga zamu iya rubuta books kyauta, shine wani can banza zaina Saida mana, to indai hakane ku readers zaku dunga siya ai saimu koma siyarwar kawai, nidai Ina Nan inata tunanin yadda zan maida wannan abun nawa, na yanke hukuncin zan maidashi Nima na kudi gwara Nima na siyar nasmi kudin tunda baifini sansuba😃 Amma Ina jiran shawararku readers me kukace akan hakan, ya kuka gani?, Meya kamata nayi akan hakan?, namai dashi na kudin kokuwa akwai wata hanyar dazanbi wadda zatafi ba ba wannan ba, Ina jiran shawararku*

*Comment*
*&*
*Share*

*Khadeejah (Ummu Fu'ad & Afnan)*

[10/4, 7:46 PM] Hayat: *🙆🙆 RAYUWATA CE*🙆🙆

*Na*

*Khadeejah Sani (Journalist)*

*🌈KAINUWA WRITERS✍🏼 ASSOCIATION*🤝🏻
```{United we stand and succeed;Our ambition is to entertain & motivate the mind of readers}```

https://www.Facebook.com/kainuwawritersassociation

*Masoyana na hakika naga shawar warinku agareni Kuma nagode Allah yabar kauna, dalilin shawar shawarin Dana samu ta Tex message da WhatsApp message da wadanda suka kirani nagode sosai Allah yabar kauna, Kuma wannan dalilin yasa nagane Kuna Sona tsakani da Allah sannan duk Wanda ya daukarmin book yasaida nabarshi da Allah wallahi bazan taba yafewaba Ina Kuma rokon Allah ya sakamin ya bimin hakkina tundaga Nan duniya, sannan wannan book zanci gaba da sambado mukushi kyauta batare dakun biyaniba amma insha Allah book Dina na gaba Mai dauke da tausayi ilimi dakuma tsantsar butulci bazan iya sakinsa kyautaba duk Mai bukata zai iya nemana nabashi account number yaturo kudinsa sannan yasamu yanzu haka nafara typing dinsa Amma ban fara sakinsaba,*

*Bayan haka*
*Wadan da suka karbi account number nah sukaimin kyauta nagode Allah yabar kauna kuma nasan kunasona tsakani da Allah bawai don book dinaba, hakama wasu da yawa daga cikin fans Dina nasani Kuna Sona Nima Kuma Ina sonku sannan kutayani Mika godiyata ga masoyana da sukayimin kyuta yau da safiyar Nan Allah yabar kauna ameen*

*😃😃🤣🤣 Masu zagina Kuma bazan barku abayaba masu cewa dama talaucine yayi Miki yawa shiyasa kikeson billo da hakan, eh naji Kuma nagode Allah Kuma yabarmin ku kuci gaba da zagina nikuma naita cigaba Ina barinku abaya, sannan inaso kisani da ace da wannan rubutun na dogara da wallahi bazan taba kawowa hakaba kisani nayi books ba dayaba ba biyuba bantaba yunkurin maida book Dina na kudiba Sai yanzu Shima Kuma akwai dalili don
```

haka please kusan me zakuce banason rashin tunani cikin Al amarina, baya ga haka zagin da kukayimin bazai taba fitominba don ba akaina aka faraba Kuma ba akaina zaku gamaba, sannan inaso kusan cewa book Dina na gaba na kudine duk maiso ta siya maraso tabarshi, nagama magana*🤷‍♀️🤷‍♀️

*🅿47_58*

"Face muktar nasan kinsan muktar ba halayyarshi Daya da Adam ba yanada halayya Mai kyau ga hakuri ilimi tunani uwa uba Kuma baibar tarbiyyaba don haka nake rokonki dakiyi tunani akan hakan Yaya Kika gani?"
Ai kwata kwata bazan iya fasalta muku halin da nake cikiba nama rasa abinda kemin Dadi don haka nakasa magana nayi shiru hakama Innarmu tayi shiru Sai zuwa can naji nafisa tace
"Mama kiyi hakuri da wannan maganar kibarta tadan huta zuwa wani lokaci tayi tunani sannan tafidda abinda ta zaba"
Shirune ya Kara rsata dakin zuwa wani lokaci sannan mama tace
"Hakane wannnan amma aganina ai baikamata ace tazauna hakaba har na wani lokaci yakamata asan abinyi"
Nafisance takara magana tace "ai yanzu makaranta ma zata fara zuwa jiya naji yace angama mata komai zata fara zuwa cikin satin Nan"
"Uhm ai shikenan tunda anfi karfina Amma inaso duk da haka kiyi tunani akan maganata duk shawarar da Kika yanke kifadamin karkiji kunyata kinji mamana?"
Kallonta nayi nace "insha Allah zan fada Miki mama"
Firarsu suka cigaba dayi nidai natashi nayi waje don cigaba da aikina,

Koda najicmaganar makaranta nayi mamaki don bansan da itaba don haka Saida nabari mama ta tafi na tambayi nafisa Nan take fadamin ai Yaya yadade Yana nemamin makaranta Kuma Alhamdllh lillah nasami fce zanyi nce insha Allah bangaran English Islamic Nan naita murna nace
"To ai Naga banyi jamb dinba duk da nabiya kudin Ina gidan Yaya aka zana banjeba"
"Ai yasaka an zana Miki Nima naso nayi Amma yace a,a Wai bayanzu zan cigaba da karatuba kema dandai kinriga kinbiya kudin jamb dinne yace kema ba karantun zakiyiba kawaidai don kar ayi asarane yasa yayi Miki, lokacin da hakan ta faru Sai ya fara nema maki school ammafa cewa yayi soyake yayimiki bazata don haka karki nunamai kinsani Nima badan abunda Naga Yana Shirin faruwaba dazu Allah da Babu yadda za,ayi kiji daga bakina Sai dai abakinsa" dariya kawai nayi cike da farinciki Nan mukaci gaba da firarmu nida ita,

Sai bayana kwana biyi sannan Yaya yazo yasameni rike da wayata Ina chatting yace
"Kishirya gobe Zaki fara lecture insha Allah ga temitable dinki nan saiki duba, kishirya da wuri na saukeki" murna nakeyi nama rasa bakin godiya nace

"Aikuwa Yaya nagode Allah yabar zumunci Allah ya biyaka da gidan aljanna nagode Yaya sosai bansan da bakin dazanmaka godiyaba Amma Babu abinda zance saidai Allah yabarka da masoyiyyarka yakara dakon kauna tsakaninku" dariya yayi yace
"Keko Allah ya shirya minke" dariya nayi Nima Nan natashi nafara tsalle na nunawa Innarmu godiya tayi Masa itama shidai yayi waje Yana dariyar murnar da yaga inayi,

***************

Alhamdllh haka nafara zuwa makaranta cikin sa,a na hadu da kawata goda Daya Mai mutunci sunanata Ayshat muna zaune cikin mutunta juna da daraja juna,
Ahaka mukayi exam munyi huru munkoma makaranta,
Alhamdllh exam ta fito munsami abinda mukeso don dukkan subject din da nakeyi dukkansu daga A Sai B nasamu hakan yayimin Dadi sosai,

Yau kimanin watana Tara kenan da fitowa daga gidan Yaya Kuma yayi daidai da cikin nafisa wata Tara don haka mukafara shirye shiryen tarbar baby ni maman baby inata sayan kayan baby don yanzu inayin Sana,a sosai Ina Saida atamfa da mayafi hijjab da jakunkuna, don haka bana rasa kudi a hannuna,

Yauma kamar kullom na fito daga lecture naji karar wayata dakkowa nayi Naga Yaya ke kirana don haka nayi saurin dauka Ina fadin
"Asslm baban Yaya ya yaudin?"
"Lafiya Lau ke nafisa ta haihu yanzuma muna asibiti " ai bansan lokacin da nasaki karaba Ina muna nace
" Wanne asibiti kike ganina zuwa yanzun Nan kuwa"
Katse wayan nayi tare da mikewa nace
"Ayshat kinga bazan tsayaba lecture din malamin nanba Sai gone matar yayace ta haihu yanzu" dariya tayi sannan tace
"A,a kice sis anyi baby anzama mom" dariya nayi Ina fadin "kedai Bari ni wallahi nama manta ko tambayar me tabaifama banyi, Kinga natafi Sai munyi waya"
Sallama mukayi na Kama hanyar asibiti
Zuwana keda wuya na samu har anfiddo da ita dakin hutu Nan nadauki baby girl Ina kallo nace
"Innarmu Kinga yarin yarnan kamarmu Daya da ita ko?"
Dariya tayi tace
"Ohh waima ni kike tambaya ke bakisaniba kenan?"
Dariya nakarayi nace
"To Bari naji baban baby me zaice shi, Yaya Dani take kamako?"

Dariya Shima yayi yace "lallaima yarinya Dani take Kama bakeba" bata Rai nayi nace

"Nidai nidai Dani take kama" nakarasa kamar zanyi kuka,
Dariya sukayimin gabaki dayansu nan muka karasa dakin,

Kwance take tana bacci don haka muka Sami guri muka zauna nidai pic nafara yiwa babyna sannan na daukemu tare Innarmu ce tace
"Mawota haka ta huta kinbi kinhanata hutawa"
Badata nayi Ina dariya nan nafara chatting na dora pic din namu a WhatsApp da Facebook mutane nata tayani murna wanine Wanda ban taba chatting dashiba Naga yayimin magana a Facebook messenger yace min
"Ke meyasa Kika saka pic dinki aduniya kowa ya gani bakisan hakan nada matsalabane?"
Kallon sunan nakarayi abin yabani mamaki ganin sunan wai *Uncle* to waye hakan kuka,
Katsemin tunani yayi danaji yace
"Dazaki Kama Dora pic dinki kekadai akaiwa haihuwar ne ko Wanda amayiwa nagadai pic baby kawai yasaka Banda nashi Amma ke ga gwana kinwani saka naki" haushi maganar tashi tabani dakuma mamaki to a Ina yasan Yaya Kuma no yaushema na amsa friend request dinshi gyara zamana nayi sannan nafara typing nace
"Malam waye Kai Kuma dazaka yimin wannan maganar haka?"
Shiru yayi zuwa can yace
"Mutumne ni Kuma kiyi saurin gogewa hanason kikara saka pic dinki aduniya"
"Tab lallai yau Naga karfin Hali barawo da sallama, nida abuna sannan wanine zai nunamin Isa akanshi to naki nacire din ai Allah yasa pic dinane bana waniba ehe"

Typing yafara zai maidamin amsar maganar danayi Masa naji Innarmu nayimin magana tace
"Kinga nafisa zanje gidan kafin ta farka nayi girkin da za,a kawo nandin"
"To Inna adawo lafiya Allah ya tare hanya"
Da ameen ta amsa ta fita.

*Comment*
*&*
*Share*

*By*

*Khadeejah (Ummu Fu'ad & Afnan)*
[10/4, 7:46 PM] Hayat: *🙆🙆 RAYUWATA CE*🙆🙆

*Na*

*Khadeejah Sani (Journalist)*

*🌈KAINUWA WRITERS✍🏼 ASSOCIATION*🤝🏼
```{United we stand and succeed;Our ambition is to entertain & motivate the mind of readers}```

https://www.Facebook.com/kainuwawritersassociation

*🅿49_50*

Innarmu ce tafita Nan nadawo kan wayata da kallo amsa yabani da fadin
"Ke inayi Miki magana kina maidamin to kiyi gaggawar cireshi kafin ranki yabaci, shikenan bakusan inda za,a kaimaku pic ba kidunga sakawa sukuma wadan can masu Kama da bunsuran harsun fara yimiki comment to kiyi sauri kicireshi kafin na nuna Miki asalin kalata"
Ai ganin abinda ya fadamin yasakani saurin zuwa na guge pic din banawa kadaiba harda na babyn Saida na cire sannan na kashe datan na rafka uban tagumi Ina tunanin waye wannan haka Mai kokari dazai hanani abinda nakeso,
Wama yasani ko aljanine baisaniba,
Aikuwa Dana shiga uku da aljanine nake magana dashi,

Tsorone ya kamani natashi da inda nake nakoma kusa da nafisa daketa bacci inata raba idanu don atsorace nake kamar ace Tak nazura aguje,

Bata farkaba har mama tazo don haka nadan saki jikina Amma duk da haka Saida tagane tacemin
"Waini tunda nazo naganki wata kala kodai bakida lafiyane?"
"Mama kaina kemin ciwo kadan kadan shiyasa"
"Ayyah sannu mamana ai Naga alama tunda nazo naganki wata kala sannu"
"Yawwa" Sai lokacin nafisa ta farka Nan mukayi mata sannu mama ta hadamat tea tafarasha,
Muna haka sunata fira nidai bana tofa komai Sai murmushi kawai nakeyi,
Muna haka Yaya yadawo Nan yakira likitan data karbi haihuwar tazo ta dubata sannan tabamu sallama fitowa mukayi baki dayanmu mukayi gida a motar Yaya,

Lokacin da mukaje hidan Innarmu harta Gama girki don haka tasakani nakaimusu daki,
Bayana nagama duk abinda zanyi nayi sallah tare da wanka nadawo daki kan kujera na kwanta sannan na kalli Innarmu nace
"Innarmu yaushe za'a kwasomin kayana daga wancan gidan inason nayi amfani da sauran
```

kayana Kinga Koda Yaya yaje ya dibomin ba dukkansu bane akwai wasu" kallona tayi tace
"Ai dama baban naku yayimin magana jiya yace Wai aurenshi yakusa aje akwashe Miki kayanki nafadawa yayanku da yace yau zakuje ke dashi da nafisa to gashi Kuma ta haihu saidai kibari idon gwagwanku tazo kwaje, tunda anyi haihuwa nasan cikin satin nan zatazo"
"Allah ya kawota lafiya, Amma anfada musu ko?"
"Eh dazo nayi waya da ita dakuma anty larai duk since zasuzo Amma ita cewa tayi kafin suna zatazo"
"Allah ya kawota lafiya"
"Ameen"

Duk firar Nan da mukeyi hankalina yanacan wurin tunanin chatting dina da Uncle Wanda nakasa gane wayeshi Kuma naje don naduba friends dinsa banga Wanda nasaniba haka Kuma Babu pic ko guda Dana sani, daukar wayata nayi nasake bude data nashiga Facebook,
Har yanzu Yana online sainaga ya turomin Tex yace
"Ya gida ya Inna ya mahbub dakuma antynki nafisa da new baby din mu?"
Duk yajero min wannan tambayar Saida na nisa sannan nabashi amasa atakaice nace
"Duk suna lafiya"
"Masha Allah, kekuma ya karatunki Ina fatan bakya Wasa dai ko don banason Wasa da karatu" yakara fada shiru nayi Ina Kara maimaita karanta message din sannan nace
"Alhamdllh"
"Ya kawarki Ayshat yarinyar kirki ai Babu laifi tanada tarbiyya"
Cikin mamaki nake Amma nadaure nace
"Tana lafiya lou"
"Shine yau Kika gudo daga makaranta ko waike kinyi baby to idon Kuma akayi muku test kiyi Yaya kenan"
"Mahadu a exam ai"
"Hahaha lallaine yarinya"
Yakara da fadin
"Kinga nikuwa da ace nine dasaina kadaki kuwa"
Uhmm" kawai nace nayi shiru,

Hakadai mukaita fira dashi nakasa sauka ga tsoro fal cikina ganin danai duk kusan abubuwan dake faruwa a makaranta yaketa fadamin harda yimin maganar wani yaro dan department dinmu dake Sona yayimin Wai karna yarda da soyayyar makaranta Kuma karna yarda yaji ko yaga Ina kulashi don bayason shashanci idon karatun zanyi nayi bayason kule kule,
Kainane ya kulle bayan na kashe data Nan nafara tunanin lallai bazai wuce Aysha ba itace ta fadawa wannan mutumin wani Abu akaina don haka na kirawo number dinta bayan gaisa nace
"Aysha wanene wannan uncle din da kike fadawa abubuwa akaina?"
Shiru tayi zuwa can tace
"Ke kawas banfa gane me kike nufiba meya faru ne haka?"
"Kinga Yar rainin wayo bansaniba, inace kinfini sanin duk abinda yafarun"
"Ke Wai meye haka wallahi bansan abinda yafaruba kiyimin bayani don Allah"

Nan nafada mata yadda mukayi da Kuma Abubuwan dayake fada akaina Wanda Kuma nasan ita kadaice tasani tunda idon naje makarantar tare muke komai ko maganar saurayin iata aka fara Tara aka fadawa Wai yanasona Amma yakasa yimin magana, abin yabata mamaki don haka tace

"Wallahi wallahi Allah kuwa bantaba magana da waniba akanki, kinji na rantse Miki inba da mamarmuba Babu Wanda yasan Ina tare dake Sai Sadiq dina shikuwa har gaisawa kunshayi dashina inace koyau shine yazo yadaukeni amakaranta yace kina Ina nace anmaku haihuwa kintafi har yacema zamuzo barka tare dashi, Amma wallahi kiyarda Dani Babu Wanda mukayi wannan maganar dashi"

Shiru nayi zuwa wani lokaci sannan nace

"Nayarda dake wallahi shikenan nagode saimun hadu Monday kenan ko?"

"A,a gobe da yamma zanzo Naga babynmu ai"

"To saikinzo goben agaida mama da Sadiq"

"Zasuji sosai, Nima agidan Inna da maman baby da baby"

Nandai mukayi sallama cikin mutunci,

Tunani nakeyi akan maganar da mukayi har nahukara na barwa Allah kawai zan dage da addu,a Allah ya bayyana minshi nagan ko waye haka,

****************

Kwanaki sun tafi ansha shagalin suna yarinya taci Sanu Fatima wato sunan Innarmu za,a dunga kiranta da zahra,

Su gwagwa sunzo daga katsina ansha shagalin suna munje munkwaso kayana komai Saida nakwaso hatta tv Dina banbartaba saina nasmu Mai kwancewa ya banbaromin kayata duk nakwashe kayana gidan tsaf dashi anata Kara gyaranshi saboda za,a saka amarya,

Kwanaki nata tafiya nafisa harta Gama wanka tana Shirin dawowa tunda Daman washegari suna takoma gida wanka,

Da baba yaso yahana Sai Innarmu tabashi hakuri tunda taga yarinyar nason komawar, Kuma itama mama tanaso kawaidai tayi karane Kuma tunda tazo ganinta a asibiti aka sallameta mukazo gida Bata Kara zuwaba don haka Innarmu tabashi hakuri ya yarda takoma gida wanka,

Tadawo lafiya Zahra takara girma fa wayo tasan mamarta idon wani ya dauketa tadunga kuka kenan bta yadda da kowa Sai mamarta da mahbub saikuma ni,

Amma kar tasani da zarar Innarmu ta dauketa zata saka kuka hakama babanta bata yarda dashi,

Haka rayuwa keta gudu yanzu gamunan har munshiga nce2 karatu yakara yawa don haka ko chatting bana samunyi sosai dondaima banason naki Hawa online saboda uncle munyi wata kalar shakuwa dashi sosai har jinake kamar so shi nakeyi don yanzu ko tunanin Muslim banayi sosai kamar yadda nake tunanin Uncle,

Yauma kamar kullum bayan nadawo daga makaranta nagama abinda zanyi nakwanta Ina kallon chat Dina dashi don yanzu har WhatsApp mukeyi dashi,
Kawai saina kunna data natafi muna firar bikin Aysha don bikinta ya matso saura sati uku,
Sakonahine Naga yashigo don haka nayi sauri fitowa dakoma wurinsa,
Pic Naga ya turamin kala kala abinda na Dade inaso ya turan Amma yaki saiyau tsaki nadanyi sannan nafara kokarin budewa kawai sainaga fuskar da bazan taba mantawa da iataba har abada Amma takara kyau haske hutu kallon pic din nakarayi nafara magana afili nace
"Anya kuwa wannan pic din na .................."

*😳😳 To ni journalist pic din waye Nafisa tagani kodai pic din Yaya Adam ne😝😝 kokuma na🤭 Babu ruwana kartace nafiya shishigi Kuma Sai zura kaina nake nagani Amma Taki barina don haka nace muzuba idon dani daku dasu ma gani a nex page*

*Comment*
*&*
*Share*

*By*

*Khadeejah (Ummu Fu'ad & Afnan)*

*🙆🙆 RAYUWATA CE*🙆🙆

*Na*

*Khadeejah Sani (Journalist)*

*🌈KAINUWA WRITERS✍🏼 ASSOCIATION*🤝🏼
```{United we stand and succeed;Our ambition is to entertain & motivate the mind of readers}```

https://www.Facebook.com/kainuwawritersassociation

*🅿59_60*

'Yan matane suka fito da abokanan ango don shiga da amarya fitowa sukayi daga motar Nan aka jera nice agaba Sai uncle agefan ango,
Amarya da ango ne kebin bayanmu nan muka shiga tare da sauran mutanen tafe muke ana daukarmu a hotuna da video,
Ina lure da Uncle ransa a bace yake Sai wani hade fuska yakeyi Yana shankamshi kamar Wanda akayiwa wani abu ganin yadda yake jeromin harara yasakani daina kallon ko inda yake,
Ahaka mukaje mukasami wuri mukazauna Ina zama natashi don zuwa wajen kawayenmu nan nafara gaisawa dasu Daya bayan daya,
Taro ya fara kankama don wajen Banda tashin kida Babu abinda kakeji awurin,
Saida nagama yimusu sannu sannan nasami kusa da Nafisa nazauna nan nake tambayarta Yaya tace
"Yana waje ai dama baishigo ba kinsanshi bayason irin wannan abun"
"Okay ashe Yana can aikuwa banganshiba dazamu shigo kokuma Yana nesa da wurin da mukayi parking ne"
"Kila bawuri Daya kukayi parking ba"
Muna nan munata fira kawai Sai jinayi ana Kiran sunana Wai nazo nabada tarihin amarya atakaice kallon Nafisa nayi tare da dafe kirji nace
"Nashiga uku kinji abinda kawas tayimin ko?"
Dariya tayi sannan tace
"Hahaha wallahi kinbani dariya kuwa kawai tashi kije kiyi abinda aka bukata malama"
Niyyar Bata amsa nakeyi naji Ankara kirana don haka namike jiki a sanyaye nayi wurin kowa dake wurin sunzuba min idanu karasawa nayi cikin nutsuwata da takun hankali Ina tafiya anutse Amma alokacin zuciyata Banda bugawa Babu aminda takeyi kirjina Sai dukan uku uku yakeyi harna tsaya tare da karbar abin magana nagyara tsayuwata sannan nafara tunanin da wanne yare zanyi magana hausa ko turanci,
Tunawa nayi ai turanci ba yaranmu bane gwara mudunga yin amfani da yarenmu a kowanne wuri bawai ba'a iyaba a,a Koda ka iya kawai kayi yaren kasarka,

(Wannan babban kuskurene waanda muke fama dashi acikin kasarmu Wai idon mutum baiyi yaren turanci ba Sai adaukeshi Mara ilimi, uhmm Amma abin duba anan shine yadda kowacce kasashe suke amfani da yarensu Kuma suke alfahari dashi, don hakan yakamata muma mugyara gaskiya mudunga koyi da sauran kasashe munayin yarenmu a wurare irin wadan Nan tonda acikin wannan taron kusan dukkan mutanen dazasu halarci wajen hausawane ko akwai
```

turawa Basu da yawa don haka saikayi yarenka da kowa zai fahimta maza da mata yara da manya, Allah yasa mugane Ameen)

Bayani nafara kamar haka

"Assalamu Alaikum warahamatullahi wabara katahu, dafarko Ina Mai fara mika sakon gaisuwata dakuma godiyata gareku, iyayena,yayyane,kannena da Kuma kawayena, muna godiya ga dukkan Wanda yasami halartar wannan shagali Kuma munsan ku masoyanmu ne nagaskiya don haka saidai muyi muku fatan Alkairi tare da addu'ar Allah yakai kowa gida lafiya, Allah yabar zumunci, wannan sakone daga kawata masoyiyata Kuma 'yar uwata Allah yasaka da Alkairi, bayan haka sunana Nafeesat Adam jiggo Kuma Ina Daya daga cikin kawayen Ayshat, itadai Ayshat Muhammad modibbo yarinyace Mai hankali ilimi nutsuwa uwa uba Kuma ladabi biyayya da sanin yakamata, anhaifi Ayshat a mumbila tafara kataunta na primary a mumbila Saida takai aji hudu sannan mahaifanta suka dawo Kano dalilin aiki Daya dawo dasu, anan tadora katunta har zuwa lokacin da tayi candy, sannan tafara kokarin shiga makarantar gaba da sandiri Alhamdllh lillah ansami abinda akeso tasami admission a FCE inda take karantar computer maths yanzu haka tana karatunta anan saidai fatan Allah yabada sa'a sabada abinda ake nema Ameen, (juyawa nayi na kalli wurin da suke zaune sannan nadora da cewa) ango inamai Kara tayaka murnar samun Aysha amatsayin mata don hatta ni kaina nayaba da kalar Alkunyarta, hakurinta, dakuma tarbiyyarta, ko shakka banayi nasan kayi dacen mata ta gari zakaji dadin zama da ita insha Allah, Ina Kara tayaka murnar samun 'yar uwata amatsayin mata saidai nabiku da addu'ar Allah yabaku zaman lafiya da zuri'a dayyiba Ameen, Alhamdllh wannan shine takaitaccen tarihin rayuwar amarya Kuma uwar gida agidan Alhaji Salis, Ina Kara Mika godiyata gareku da kuka bani aron hankalinku nagode Allah ya maida kowa gidansa lafiya Ameen" Ina kaiwa Nan namika abin maganar na koma wurin amarya inda aka tanadamin wurin zama,

Acan bangaran kuwa Yaya Adam ne yayi suman zaune Jin yadda nake magana kallona kawai yakeyi tare da juyawa duniyar tunani,

Tun bayan rabuwarshi Dani take cikin tashin hankali don wannan aurenma dazaiyi bawai don Yana sonta bane a,a kawaidai zai aureta ne saboda tafi karfinsa Kuma shidai bazai iya budar Baki yayi wata maganaba akan maganar bikin Sai yadda tace haka za,ayi gashi kwana biyu baya iya bacci kullum kwana yakeyi da tunanin Nafisa haka Koda baccine ya daukeshi tofa Babu abinda yakeyi Sai mafarkinta bai Gama yadda da cewa sona yakeba Sai yanzu Daya ganni Ina magana Ashe nasan amaryar shi angonne abokinsa don wurin aikisu Daya office dinshi Yana kallon nashi shinema dalilin zuwanshi wurin bikin Amma yayi Daya sanin zuwa wurin bikin nan,

(Nidai nace kwalelanka to don uncle ya ruga ya kwace abarsa aha baka isaba ehe😡😏😒)

Bangarena kuwa Ina karasawa nazauna tare da sauke ajiyar zuciya nace

"Washshsh Allah nah wallahi nasha wuya fah bakini har muryata tafara rawaba Allah kiris nake jira nayi kuka kinsanni bana iya magana cikin mutane" murmushi tayi tace

"Ai wallahi ina Nan Ina maganarki nace nayi mamakin yadda Kika tsaya kinayin bayani Shima

dariya yagama yimiki" murmushi nayi nace
"Allah yasa dai nabaku kunya nayi abinda yadace"
Tashi nayi nace
"Bari naje nayi magana afara rabawa mutane abinci" sakkowa nayi Kuma lokacinne aka Kira abokin ango Shima inajin sunayin magana da Uncle yace asaka wani shi bayajin Dadi bazai iyaba nace oho maka dai nayi gaba,

Nayiwa masu zuba abincin magana sunfara zubawa don haka nafara duba uncle don Naga baya wajen da naganshi a kusa da angon don haka nayi waje don naduba,
Ajikin mota naganshi don haka nakoma nakarba Masa abinci da lemo nakoma don nakai Masa Saida naje nayimasa sallama Amma yaki amsawa don haka Sai kawai na ajiye nakoma dakkowa Yaya don naganoshi cikin mota,
Nafisa nasamu tana shirin fitowa nace
"Ohhhh kaimasa zakiyi ne?"
"Eh gashi nan zankai"
"To wanna ya isheku kenan"
"Eh saidai ki Kara Mana drink din"
Ciki nashiga na nakko musu nafito don kaimusu bayan nabasu na koma kamar zan wucesa Sai jinayi yace
"Zonan" kallonshi nayi yawani hade Rai kamar bashine yayi maganarba nakarasa wani na tsaya nace
"Gani"
Ko kallona baiyiba yace
"Shiga ciki muyi magana"
Daukar kayan Dana ajiye nayi nakarasa nashiga nazauna a bayan motar ganin hakan yasakashi karasowa Shima yashigo bayan yazauna tare da barin kofar abude kamar yadda nayi sannan yafara magana yace
"Nafeesat kina sane kikemin wannan abun ko saboda kinsan kalar soyayyar da nake yimiki shiyasa kike yimin haka ko?"
Kallonshi nayi Naga idanunshi sunyi jajur sunkara kankancewa daga gani kasan kishine kawai yake damunshi don haka nace
"Uncle menayi maka Kuma?"
"Okay Baki saniba kenan?"
"Allah bansani ba"
Nafada cikin shagwabe fuska kamar zanyi kuka kallona yayi sannan yace
"Uhm shikenan"
Kara kwabe fuska nayi nace
"Please kayi hakuri to"
"Kinsan bazan iya fushi dakeba shiyasa kikemin duk abinda kikeso"
"Allah bansan abinda nayiba"
"Shikenan yawuce to, shine kika wani bude Baki dazu kinata zuba bayani mutane sunata kallonki wani kamar yazo ya rungumeki Ina kallonshi Sai wani yake Baki yakeyi wani Kuma yanata wani kwalalo Miki idanu saura kadan ai na tsokane idon......" Nice na dakatar dashi

saboda dariyar da nakeyi.

*Comment*
*&*
*Share*

*By*

*Khadeejah (Ummu Fu'ad & Afnan)*

🍇🍇🍇🍇🍇🍇🍇🍇🍇🍇
*MENENE MATSAYINA ?*
*(fictional story)*

*Written by*
phatymasardauna
*🎈Mrs Sardauna🎈*

*Dedicated to my lovely sister Maryam*

*🌈KAINUWA WRITERS ASSOCIATION*

*https://www.facebook.com/kainuwawritersassociation*

*WATTPAD*
@fatymasardauna

*💃JIKAR HAJIYA 💃* ```bansan mai zance miki ba, amma gaskia kina sani nishaɗi da comment ɗinki,  Inasonki Sosai tawan, kiyi farinciki har ƙarshen rayuwarki, wannan page ɗin kyautane a gareki ke kaɗai...```

*PAGE 56to57*

Gudu kawai Hameed keyi akan titi burinshi baiwuce yaga yayi ido huɗu da Sarah ba,, dayake yasan gidansu, domin kwanakin baya yataɓa kai Farhana, don haka bai wani shan wahala wajen nemanta ba kaitsaye ya nufi gidansu,, daga ɗan can nesa da gidansu Sarah yayi parking motar tasa, jingina yayi da motar bayan yafito yana mai kafe ƙofar gidan nasu da'ido.. Mintuna bakwai da isowarsa ƙofar gidan, yaga wata mota tayi parking a ƙofar gidan, Sarah ce tafito daga cikin motar, carab idanunta suka sauƙa akan Hameed dake tsaye jikin nasa motar, sake waro idanunta tayi domin tabbatar da abun data gani, "shine dagaske wallahi Hameed ne" tafaɗa lokacin da take murje idanuwan ta da hannayenta duka biyu,, "Kaddai har aikin boka naguru yasoma ci ? tatambayi kanta, domin dai yanzu haka daga wajen boka take, tanar ka masa maƙudan kuɗaɗe yakuma bata wani ƙullin magani yace duk yanda za'ayi tasan yanda zatayi tasanya mawa Hameed acikin abinci yaci, yakuma yi mata wani aiki wanda Hameed ɗin da ƙafarsa zaitako yazo gareta,, wani irin tsallen murna tayi haɗe da cewa "Yes Boka wallahi aikinka har ya soma ci domin ko gashi yazo da ƙafafunsa " take Sarah tasauya takunta zuwa rangwaɗa, tanufi inda Hameed ke tsaye, kafeta yayi da mayun idanunsa wanda suka ƙaɗa sukai ja dasu tsabar bala'i da ɓacin rai dake damunsa, tana ƙara sowa tayi masa wani murmushi mai ɗauke da sigan jan hankali, cike da kisisina tace " Yaya Hameed yau kai ne agidan mu, Allah yasadai wajena kazo ?" taƙare maganar tana maiyi masa fari da'ido,, kallonta yayi na tsawon minti ɗaya kafun yasaki wata ƴar guntuwar murmushin datafi kuka ciwo, tsab yakaranceta don haka yace " Shiga mota a kwai abun da nakeso mutattauna dake mai mahimmanci " jikinta har rawa yake jin yace tashiga mota zasuyi magana mai mahimmanci, Azuciyarta tace "Allah kasa zancen soyayyya zaiyi mini" (kuji shegia hatta manta aika aikan da tayi) da sauri tashige cikin motar tasa haɗe da hakimcewa a gidan gaba, shiga cikin motar shima yayi haɗe da sawa duk wata ƙofar fita daga motar luck key yayi mawa motar, da ƙarfin tsiya ya figi motar harsai da Sarah ta suɓalo gaba kanta kuwa yayi wani irin mummunan bugewa,, a matuƙar tsorace ta juyo ta kalleshi haɗe da cewa " Nashiga Uku na Yaya Hameed ina zaka kaini !! ? " baiko kalli inda take ba balle tasa ran amsawarsa, gudu kawai yake shararawa,, tafiya sosai yakeyi akan titi tamkar wanda zaifita gari, yayinda Sarah ke ta yi masa ihu da magiya akan yataimaka ya tsaya ta sauƙa,, amma kollonta bayayi,, gaban wani gini wanda aka fara ba a ƙarasa ba, yatsaya da motar tasa, cire luck ɗin daya sanyawa ƙofofin motar yayi haɗe da ficewa daga cikin motar, ƙofar da Sarah ke ciki ya buɗe haɗe da sanya hanunsa yadam ƙota, haka yashiga janta tana ihu har cikin wannan gidan, kitsaye wani ɗaki da ke cikin gidan ya nufa da'ita, bakomai acikin ɗakin sai zallan ƙasa, amma akwai rufi asaman ɗakin hadda winduna,, cikin turbuɗin ƙasan dakw ƙasan ɗakin ya wurgata, haɗe da zare belt ɗin jikin wandosa, yayi kanta, batare da tunanin komaiba Hameed yashiga dukan Sarah baji babu gani, ihu sosai Sarah takeyi na neman taimako, amma bawani mahaluƙin dake jinta, duka sosai Hameed yayi mawa Sarah harsai da jikinta yafaffashe, fuskarta kuwa raga raga tayi da jini, saida Hameed yaga Sarah ta daina numfashi kafun yadaina jibganta, bayan yagama illata mata jiki da duka, ruwa mai sanyi ya ɗebo ya kwara mata, afirgice tafarfaɗo daga suman da tayi, motarsa yakoma ya ɗauko wata gorar Fanta, danne sarah yayi da ƙarfin tsiya yaɗura mata wannan fantan dake cikin gora, saida tashanye tas kafun yayi wulli da goran gefe, wani

irin kallon tsana yayi mata haɗe da cewa " Banza sakarya wacce batasan mutumcin abota ba, ke atunaninki zaki kashe jinin Hameed kuma kizauna lafiya ? wallahi yau saikin gwammace da uwarki bata haifeki ba, ƴar iska mahaukaciya " yawun dake cikin bakinsa yatofa mata akan fuskarta, haɗe da ɗaukan kaca yaɗaure mata hannayenta da ƙafofinta gamdashi, "Nan da 5 minute ki saurari baƙon yanayin dazai zo miki, wallahi saikinji fiye da azaban da kikasanya Farhana aciki, saikinji fiye da zafi da raɗaɗin da kikashayar da Farhana" yana kaiwa nan a zancensa yasakai yafice daga cikin ɗakin haɗe da danna mawa ƙofar ɗakin kwaɗo yajefa key ɗin acikin aljihunsa,, cikin motarsa yakoma haɗe dayi mata key, kaitsaye yaɗauki hanyar asibiti.....

Yanazuwa asibitin yasamu doctors suna shirin sallaman Farhana, domin har su Ummie da Abba sunzo, nan aka sallamesu suka tarkato suka dawo gida, koda Farhana tagama zayyane mawa su Ummie abun da yafaru tsakaninta da Sarah, Salati Ummie da Abba suka somayi cike da alhinin abun " lallai duniya, wanda kayarda dashi shike cin amanarka, lallai zuciyar ɗan adam cike take da baƙinciki da kuma hassada, zamani ya lalace wanda kabawa yarda da amana shike yaudaranka, ya Allah karabamu da sharrin maƙiyanmu nafili da na ɓoye, Ameen ".......

Minti biyar da tafiyan Hameed Sarah dake ɗaure, tasoma jin mararta na wani irin ƙullewa, yayinda cikinta ke wani irin ƙugi tamkar hanjinta zasu tsistsinke haka takeji, ihu tafara kurmawa daduka ƙarfinta, tana mai neman agaji amma ina bamaijinta balle yakawomata agaji, wani irin masifaffen ciwon ciki da na mara ne suka addabeta tamkar zata mutu haka takeji, haka tashiga murƙususu acikin ƙasa tana kwarara ihu, iya azaba da raɗaɗin duniyarnan Sarah tajisa, gashi babu wani maijinta balle yataimaketa, saboda tsananin azaba da Sarah keji, yasanya numfashinta ɗaukewa baki ɗaya......

Kwance suke akan gado rungume da juna, idanun kowannensu nakan ɗan uwansa, wani irin kallo Hameed kejifan Farhana dashi, mai cike da tsananin soyayya da kulawa, itama irin kallon da takeyi masa kenan, a hankali yakawo bakinsa kusa danata ya haɗesu waje guda, wani irin kyakkyawan kiss suka shiga mawa laɓɓa da harshen juna, kiss suke mawa juna, wanda bakow keyin irinsaba sai ga babban masoyinsa, a hanakali yagangaro da hannayensa kan breast ɗinta wanda aƴan kwanakinnan suka sake cika da girma, yanda yakeshafa breast ɗinta yasanya taƙara lafewa a cikin jikinsa domin kuwa sosai hakan keyi mata daɗi, a wannan dare wani irin gangariyar soyayya Farhana da Hameed ɗinta suka gudanar, Hameed ya shayar da Farhana'nsa daɗi son ransa, yayinda itama tashayar dashi daddaɗan zumanta wanda babu algus acikinta.......

****

Cikin muryan kuka Beedah ke cewa " Dan Allah kasanar dani *MENENE MATSAYINA* acikin

gidannan ?  ka ƙauracewa shimfiɗata, baka saurarata, baka shiga duk wani al'amurana, nasan cewa nayi maka babban laifi, amma maiyasa bazaka yafemin ba ?? " wani irin mugun kallo Hameed dake tsaye a gabanta ya watsa mata, haɗe da cewa " Koki bani hanya na wuce kona tattakaki anan wajen "  yaƙare maganar cikin kakkausar murya,     cikin matsanancin tashin hankali Beedah ta zame a wajen tashiga rera kuka, Hameed kuwa tsalleketa yayi, yayi tafiyarsa abunsa,,, koda yaje gidansu bai ɓoye mawa Ummie da Abba komaiba yagaya musu cewa yakama Beedah tanashan ƙwayoyin planning,, sosai ran Ummie yasosu da abun da Beedah ta aikata, taji zafin abun sosai, amma tunda ta fuskanci cewa ɗannata yanason matarsa, yasanya ta shanye ɓacin ranta cikin zuciyarta,,  Abba ma yaji zafin abun, amma sai ya taushi Hameed haɗe da basa haƙuri akan kada yasake yaɗauki wani tsattsauran mataki a kanta, duk da cewa tayi laifi, kada ya yi mata tsastsauran hukunci, Abba yayi masa nuni da yayi mata nasiha mai ratsa jiki, ko hakan zaisa ta kiyaye gaba,, yanda Abba yayi ta bawa Hameed shawarwari a game da rayuwa, yasan yashi jin zuciyarsa tayi sanyi....

Tunda Hameed ya kulle Sarah a cikin wannan kangon baisake waiwayarta ba, saida tayi kwana Uku,    koda ya je a wani irin mummunan yanayi ya isketa, tamkar gawa,  murmushin mugunta yayi haɗe da cewa " Nasan kinɗanɗana azabar da Farhana ta ɗanɗana alokacin dakika zubar mata da ciki,  ke ƙaramin mugunta kikayi mata nikuma namiki babba, idan kin rayu ruwanki idan kin mutu duk ɗaya"  kiiii haka yajata a ƙasa, yacusata cikin mota, bai zarce da'ita ko inaba, sai ƙofar gidansu, ƙafansa yasanya ya tangaɗata waje daga cikin motarsa, haɗe da bamawa motar tasa wuta, yafice daga area'n nasu,,   ƙanin Sarah dayazo shiga gida shiya fara yin tozali da ita yashe a gefen titi kamar wata gawa, ai dagudu yayi cikin gida haɗe da ƙiran mamansu,   kuka maman Sarah ta sanya, ganin ɗiyarta yashe a ƙasa jikinta duk jini bata ko numfashi,,  da taimakon mai gadinsu aka sanya Sarah acikin mota, aka wuce a sibiti da'ita.........

Duk iya ƙoƙarin da doctors sukayi wajen ceto numfashin Sarah abun yaci tura, domin dai abincikensu sun gano cewa "Maganin zubar da ciki tasha mai ƙarfin gaske, batare kuma da tanada ɗauke da ciki ba, ƙarfin maganin kaɗai ya isa ya sanya numfashinta ɗaukewa na har abada, maganine mai haɗarin gaske, Allah ne dai kawai yasa kwananta na gaba, amma ita da farfaɗowa bayanzu ba,  kuma side effect na maganin yasanya mata wani ciwo a mahaifa,, koda doctors sukai mawa iyayen Sarah bayanin halin da ƴarsu keciki, baƙaramin tashin hankali suka shiga ba, bama kamar mamanta......

*Bayan Sati Biyu*

Gaba ɗaya hankalin Hameed yau a tashe yake, domin kuwa tun safe Farhana keta kwarara amai, gashi taƙi sanya komai acikinta, uwa uba gawani zazzafan zazzaɓin dayayi mawa jikinta rubdugu,,  ganin abun nata na ƙara da ɗuwa yasan ya shi ɗaukanta, suka nufi asibiti.....

Zama yayi akan wani benci dake bakin ƙofar ɗakin da  aka shigar da Farhana, kallo ɗaya zakai

masa kafuskanci cewa yana cikin damuwa,

Doctor Rasheed ne yafito fuskarsa ƙunshe da murmushi, Hameed na ganinsa yayiyo kansa yana cewa " Doctor yajikin nata ?"     " jiki Alhmdlh, tama samu bacci, saidai a gaskia..... "Saidai me doctor dan Allah karkacemin wata matsala ne yasameta, Hameed yakatsesa da hanzari,, murmushi doc Rasheed yayi haɗe da cewa " Bawata matsala, ina mai tayaka murna Mr Hameed matarka tana ɗauke da juna biyu  !!!"

Waro idanunsa Hameed yayi cike da tsananin mamaki yace "Dan Allah doctor dagaske kake ?" " Ƙwarai kuwa Mr Hameed matarka na da ciki !!" Rasheed yasake maimaita masa,

"ALLAHU AKHBAR ! ALLAHU AKHBAR !! Allah bawani sarki bayankai, kaike isar mawa bawa ako wani hali, Ya Allah inamai miƙa godiyata a gareka " Hameed yafaɗa idanunsa cike da ƙwallan farinciki, Sujja yayi awajen haɗe da sake gode mawa Allah, daya sake a zurtashi da kyautar ɗa ko ƴa,,  yana ɗagowa daga sujjada ya rungume doctor Rasheed cike da farinciki yace " Kayimin albishir wanda bazan taɓa mantawa ba, haƙiƙa zansaka maka da kyauta wanda kaima bazaka taɓa mantawa ba,,  yana kaiwa nan azancensa yacusa kansa cikin ɗakin da Farhana ke kwance,,, murmushi kawai doc Rasheed yayi, domin ya fuskanci cewa Hameed ɗin yanacikin farinciki......

*13/October/2019*

*MRS SARDAUNA*

*🙆🙆 RAYUWATA CE*🙆🙆

*Na*

*Khadeejah Sani (Journalist)*

*🌈KAINUWA WRITERS✍🏼 ASSOCIATION*🤝🏼
```{United we stand and succeed;Our ambition is to entertain & motivate the mind of readers}```
```

https://www.Facebook.com/kainuwawritersassociation

*🅿65_66*

Agurguje

Biki yazo anata shirye shirye naje gidan amarya Aysha nasameta lafiya kalau saboda muna haduwa a makaranta shiyasa bamuyi kewar junaba Nan muka kara shirya yadda bikin zai kasance don saura kwana biyar daurin auren,
Zaune nake falon Aysha ita Kuma tana daki take dakkomin dinkin da akayi mata zangani na bikin,
Dawowa tayi ta zauna kusa Dani tace
"Ke waima Ina Zaki zaunane haryanzu banji unguwarba Allah yasa kusa damune madunga tahowa tare da makaranta"
Murmushi nayi nace
"Uhm kinsan abinda har yanzu banma saniba kenan Kuma jiya naji ana maganar jere Yaya Yana cewa gobe za,aje ayi Amma wallahi bansan ko wacce unguwa bane" dariya tayi sannan tace
"Kajini da 'yar duniyar amarya Wai da gaske kike Baki saniba?"
"Wallahi Allah bansaniba nifa bamu tabayin maganar anguwar da yake giniba kawaidai nasan yanayin gini Amma bansan unguwar ba"
Hade Rai tayi sannan tace
"Malama banson rashin kirki kirashi muji inane" kallonta nayi sannan nafara dariya nace
"Kinjiki kawai kibari idon kukaje kyagani ai dake za,aje gobe ko bazakiba?"
"Au waidama hardani za,aje jere?"
"Eh Mana abinda nazo fada mikifa kenan Innarmu tace afada Miki kishirya da wuri Yaya zasu biyo shida Nafisa da anty safnah"
"Okay Allah yakaimu aikuwa nidai before hakan kikiramin shi kitambayeshi" dariya nayi nace
"Kefa dadina dake naci"
"Eh naji nidai akirashi kawai"
Wayata nadauko kallona takeyi cike da mamaki sannan tace
"Yaushe Kika canja waya bansaniba"
"Ohhh namanta Ashe Baki ganiba ranar Friday ya kawomin wallahi"
Dariya tayi take
"Lallaima wannan angon bayajin garin Nan wato harda canja waya"
Murmushi kawai nayi tare da kiranshi,
Har takatse bai dagaba Sai yabiyoni dagawa nayi tare dayin sallama ya amsa nan nace
"Ya weekend?"
"Alhamdllh y Innarmu ya gida?"
"Inna tana gida tana lafiya kalau"
"Ina kikaje?"

"Gidan Ayshat"
"Da izinin wah kikaje?"
Tambayar tabani mamaki Amma sainace
"Banganeba"
"Zaki gane ai kibani amsa wa Kika tambaya?"
"Innarmu"nabashi amsa atakaice Sai yace
"Uhm bakijin magana ko shine Zaki fita bazaki tambayi mijinki ba Sai bayan kinje sannan kiwani fadamin"
Dariya nayi nace
"Wai nufinka idon zan fita Saina fada maka? Kabari lokaci yayi Wanda Dole Saida izininka zan fada maka"
Dariya yayi sannan yace
"Zan kamakine ai Zaki gane kurenki"
Murmushi kawai nayi sannan nace
"Ayshat keson magana dakai"
"Okay Bata wayan ai yanzu muka rabu da mijinta yazo office dina ya Dade"
"Ayyah Allah sarki gata"
Namika mata hararata takeyi sannan takara kunnen nata gaisawa sukayi sannan ta tambayeshi maganar unguwar da gidan yake sukayi maganarsu bansan me yake cemataba har suka Gama sannan tamikamin wayan,
Karba nayi nakara akunne yace
"Wai dama bakinsan inda gidanki yakeba?"
"Ai baka fadaminba"
"Ohhh kekuma kinwuce kitambayeni wato Sai nine zan fada Miki"
Uhm kawai nace sannan yadora da fadin
"Wallahi ni nama manta ban fada mikiba ai anan GRA yake"
"Okay Ashe anan yake?"
"Eh nanne Babu nisa da gidan hajiyata ai"
"Ayyah Allah sarki ya hajiyar take?"
"Tana lafiya kalau"
"Masha Allah"
"Yaushe Zaki tafi gida"
"Sai da yamma"
"Okay kijirani zanzo na daukeki"
"Allah dama kabarshi kawai karna baka wuya"
"Ohho komadai menene nidai sainazo"
Yana fadar haka ya kashe wayar,

Kallon Aysha nayi nace "ashema Sai anwuce ta Nan"
"Eh Nima haka nace Kinga idon za,aje GRA Sai anwuce ta hauran wanki"
Kasancewar nanne unguwar da aka kawo Ayshat,

*****************

Yaune zamuje kunshi Amma Saida mukaje makaranta don wata lecture zatayi Mana test don haka muka fara zuwa bayan angama nida Ayshat muka wuce wurin kunshi,

Sai dare sannan muka taho daga gidan kunshin don daima Mahmud din Aysha ne yaje ya daukomu Saida suka kawoni gida sannan suka tafi munrabu Akan Sai gobe zatazo don gobe jum'at Kuma ranar za,ayi daurin aure,

Gida nashiga nasami Baki sunzo Amma bawasu masu yawa bane gwagwo da anty jummala Nan muka zauna nafara gaidasu sunata tsokana ta Wai amarya nasha kamshi dariya kawai nayi nashige daki nace
"Wallahi nagaji wanka zanyi"
Bayan nayi wanka Nan aka hadu da Nafisa Yaya da Innarmu akayita fira kamar kar arabu,

*********************

Rana Bata karya saidai uwar Diya Taki kunaya,
Yau andaura auren *Nafeesat Adam jigo da Muslim Muhammad* bature akan sadaki naira dubu dari da hamsin Wanda dubban jama,a suka shaida bayan ansakko daga sallahr juma,ah,

Lokacin da mahbub yazo Yana murna Yana tsalle yace
"Innarmu andaura auren" gabanane yayi wata kalar faduwa saikuma na saki kuka ahankali,
Aysha dake kusa Dani tace
"Eh lallaine soyayyah ruwan Zuma wato harda kukan soyayyah akeyi kenan" banza nayi da ita inata kukana nashige can cikin daki.

*Kuyi hakuri da wannan my fans*

*Comment*
*&*
*Share*

*By*

*Khadeejah (Ummu Fu'ad & Afnan)*

*🙆🙆 RAYUWATA CE*🙆🙆

*Na*

*Khadeejah Sani (Journalist)*

*🌈KAINUWA WRITERS✍🏼 ASSOCIATION*🤝🏼
```{United we stand and succeed;Our ambition is to entertain & motivate the mind of readers}```

https://www.Facebook.com/kainuwawritersassociation

*🅿67_68*

Kan gado nafada tare da sakin wani kukan rayuwata kawai nake tunawa ta gidan Yaya Adam gashi yanzu Ankara dauramin aure akaro na biyu ko Yaya zanyi rayuwa acan din,
Wani kukanne yakara kwacemin nayi Mai isana sannan namike zaune tare dayin tagumi narasa ko menene acikin raina farin ciki kokuwa akasin haka,
Saikuma naji kaina yadauki wani irin ciwo nasan Kuma sanadin kukan da nayine,
Gyara kwanciyata nayi Ina Kara hawaye zuwa can Ina kwance saiga Ayshat tashigo tazo kusa dani tazauna tare da kallona tana murmushi tace
"Amarya ta ango ai saiki tashi muje gasucan a baranda suna jiranki za,ayi photo" kallonta nayi hawaye na zubarmin nace
"Bazan iya fitaba"
Kallona tayi cike da mamaki tace
"Saboda me?"
"Kaina ke ciwo"
"Ayyah sannu kinji wannan kukanne da kikayi shiyasa Miki ciwon kan, kiyi hakuri kawas rayuwa haka take Kuma insha Allah bazaki kara maimaita irin rayuwar da kikayiba ta baya Ina Mai tabbatar Miki Muslim ba halinsa Daya da Yaya Adam ba Kuma idon kin duba aishi Yaya ba auren soyayya kukayiba aurene na hadi da iyayye suka hada don haka kidaina wannan tunanin, please ki cire wata damuwa aranki Ina lure dake acikin satin Nan gabaki Daya kinsakawa kanki damuwa har ramewa kikayi to wallahi Ina Kara Baki shawarar kibar duk wata damuwa kiringumi mijinki ki kyautata Masa, hakuri tsafta da kulawa da gidanki shine abinda zanbaki shawara ki dage da yinshi, kawas insha Allah kinsami miji na kece raini don haka kirike mijinki hannu bibbiyu Allah yabaku zaman lafiya Mai dorewa Ameen"
```

Sunkuyar da kaina nayi tare da goge hawayen fuskata sannan nafara magana nace
"Nagode Yar uwata Allah yasaka da Alkairi yabar zumunci nagode da wannan nasiha da kikayimin insha Allah Kuma zanyi amfani da ita nagode sosai" magana take Shirin yin saiga wayanta nayin kuka don haka tafasa magana taduba tare da kallona tace
"Kingansu sunata jiranmu ko?"
Murmushi nayi daukar wayar tayi tana fadin
"Sorry my love gamunan zuwa"
Tana fadar haka takashe kallona tayi sannan tabude jakarta tadauki Hoda takara shafamin sannan ta gyaramin mayafi da janbaki,
Mikewa nayi nagyara zaman mayafina sannan nakalleta nace
"Ya Kika gani"
Dariya tayi tace
"Wow Sai Amarya Kinga yadda kika hadu duk da Babu wani kwalliya da kikayi?"
Murmushi nayi nace
"Muje kedai karna batawa mijina rai"
Dariya tayi tare da biyo bayana tana fadin
"Lallai kawas wuyanki ya Isa yanka wato ni kike fadawa haka ko?"
Murmushi kawai nayi,
Fitowa mukayi muka fita waje samunsu mukayi su hudune dagashi Sai Mahmud din Ayshat Sai abokan su guda biyu,
Gaisawa mukayi dasu sunata tsokanata Wai amarya Bata laifi nidai na sunkuyar da kaina kasa Ina murmushi,
Shikuwa gogan naku yayi suman tsaye Yana kallona don ko motsi ya kasayi Sai aikin kallona yakeyi nikuwa duk kunya ta kamani abokan sane suka dawo dashi daga duniyar tunani don sunlura da kalar kallon da yakemin don haka suka Kama yimasa dariya Daya daga cikinsune yace
"Haba mutumin irin wannan kallo haka kamar Babu gobe"
Dayan yace
"Idonma yayi hakuri kaimasa ita zamuyi gobe kowamaa ya huta irin wannan kallo haka agabanmu Ina da bama wajen Kuma Sai Yaya kenan"
Mahmud ne yace
"Uhmm ai kila mantawa yayi damu agimun shiyasa ya tafi da yawa"
Shidai Banda murmushi Babu abinda yakeyi Yama kasa yimusu magana,
Nandai muka gyara akayi pic kala kala sannan mukayi sallama nidai nakasa Bari muhada Ido dashi, shikuwa Sai kallona yake nagane me yake nufi don haka nayi kasa dakaina naki Bari muhada idanu,

Ciki muka koma akaci gaba da shagalin don daima Sai gobe za,ayi yinin biki don haka Babu mutane agidan dayawa,
Wuraren karfe shida na yammane Ina zaune adaki nida Ayshat muna fira saiga Nafisa tashigo dauke da babynta ta zauna kusa dani tace
"Please Ayshat ki Kira mijinki ga get pass din dinner din yayana don Allah kujemin keda Nafisa" takarasa fada da Mika mata get pass din nidai inajinsu naci gaba da danna wayata

itakuwa kiranshi tayi awaya ta fada Masa yace to yaje candin ya dauketa da Daren sutafi gida murna tafarayi tace
"Yaushe zamu tafi to?"
"Karfe bakwai zamu tafi"
"Aikuwa Bari mufara shiri"
Tamike tare da kallona tac
"Kekuma yanaganki zaune Kuma munata magana Amma bakiyiba?"
Banza nayi da ita Sai Nafisa tac
"Nafisa tashi don Allah kishirya muje please karkice bazakijeba badan shi zakijeba Donni zakije da mama please kaitaimaka sis"
Jin yadda takemin magiya yasakani yin shiru don da harga Allah banyi niyyar zuwaba Amma tunda tace haka Babu yadda zanyi Dole na hakura namike nayi daki tare da cewa to,

Shiryawa mukayi nabawa Ayshat wani sabon kayana material ne blue colour tasaka nikuma nasaka doguwar rigata light pink Sai mayafina Shima haka Ayshat ce tayimin simple makeup lokacin Dana fito daga daki zuwa tsakar gidanmu wadanda suke anan tafi suka farayi tare da cemin Wai saikace ranar dinner Dina irin wannan kwalliya haka nidai murmushi kawai nayi don koni Naga kyawun da nayi Nan mukayi sallama dasu Innarmu muka fita waje inda Yaya ke zaune Yana jiranmu,

Bayan mota muka zauna Sai nafisa tashiga gaba muna tafe Yaya yace
"Kekuma kinsha gayu kamar ranar dinner dinki"
Nanma murmushi nayi nafisace tace Masa
"Wallahi nimadai haka nace mata nasan dawuyama idon batafi amaryar kyauba"
Dariya nayi nace
"Tab rufamin asiri hajiya ni asuwa?"
Dariyar itama tayi tace
"Allah kuwa ai Naga amaryar yayan bawata Mai kyau bace ni wallahi ganima nake tayi sa,a dashiba kila bakigantaba wata tsohuwa da ita"
Yayane yac
"Banason gulma kekuma meyayi ruwanku Kunga shiyasafa mata suke shiga wuta wallahi meyayi Miki zafi da matarshi aidai ahakan yaganta Kuma yace yanaso ko?"
Shiru mukayi dukkanmu don munsan Yaya inyafara fada Sai Allah,

Munje wurin munsameshi cike da mutane amarya da ango suna zaune anata shagalin muna shiga Yana dago idanu hada Ido mukayi dashi na kauda kaina gefe nakara hade gira sannan muka Sami wuri muka zauna,
Tunanine yakamani na ganin wadda Yaya zai aura wannan matar ce kokuma nace karuwarsa da muka zauna da ita gida Daya innalillahi wa'inna ilaihirraji'un shine kawai abinda nake maimaitawa acikin Raina ganin inda ya bige abinma abin tausayi don wallahi tausayi yabanima ni,
Munje har wajensu mungisa sannan muka dawo,
Muna zaune Amma duk dago kaina da zanyi saina hada idanu da Yaya dakecan kusa da

amaryarshi Sai Kara manne Masa takeyi tanata wani kwantawa ajikinsa,
Wayanace tafara kuka don haka nadauko ganin Mai Kiran yasakani sakin ajiyar zuciya nace
"Wai nama manta wallahi ban fada makaba ashefa aikuwa kila sainasha jaraba"
Dagawa nayi tare da karawa akunne nayi sallama amsawa yayi tare da jefomin tambaya yace
"Kina inane haka naji kida Yana tashi?"
Gabana yana faduwa don nasan saiyace maiyasa ban fada masaba kafin a daura aurema yace haka balle Kuma andaura daurewa nayi nace
"Naje dinner neh"
"Dinner Kuma? Nawa Kuma?"

"Na Yaya Adam dama......dama....dama...Yan.....zu nake Shirin fada make"
Tun daga muryar da yayimin magana nagane ranshi abace yake yace
" A Ina akeyin dinner din"
"MBS center"
"Kibani address malama"
Nan nabashi address din wurin sannan mukayi sallama,

Baifi ten minutes bah saigashi yakara kirani yace
"Fito waje gani nakaraso"
To nace sannan na kalli Ayshat nace
"Bari naje wurinshi Yana waje"
"Okay Nima yanzu zan wucedai don Yana kan hanya"
"Ai yanzu zan dawo"
Fita nayi nasameshi amota Yana zaune shiga nayi ciki nazauna tare da gaidashi kin amsawa yayi Yana kallona zuwa wani lokaci sannan ya nisa yace.
"Me yasa Kika fita batare dakin tambayeni ba?"
"Mantawa nayi wallahi kayi hakuri bazan karaba"
"Idon kinsami hanya kima Kara din" saikuma y tsaya da maganar Yana kallona sannan yace
"Bana hanaki saka wannan abunba?" Yafada Yana shafo lebena hakan yasa nagane janbaki yake nufi don haka nayi shiru Ina raba idanu Sai Kuma nafara Shirin gogewa,
Rikemin hannun yayi sannan ya matso kusa dani ya hade bakina da nashi Yana tsotse janbakin jiki tureshi nakeyi Amma Ina Saida ya Gama abinda zaiyi sannan ya koma mazauninsa ya gyara zama tare da kallona,
Kasa nayi da kaina Ina matsar hawaye shikuwa Saida ya daidaita kanshi sannan yace
"Ai daman nafada Miki Zaki shigo hannuna zan kamaki ne Kuma gashi kinfara shigowa indai Kika saka wannan abun abaki ko gaban waye Sai nayi Miki haka Kuma wannan kadanne zanmiki Wanda yafi haka inkika Kara"
Hawaye nakeyi har yagama magana,
Shirune ya ratsa wajen na wasu lokuta sannan yace
"Ina Ayshat take?"
Ciki na nuna Masa da hannuna batare Dana dagoba,
Kallona yakeyi Sai can yace
"Baki da bakine?"

Girgiza kaina nayi yakara cewa
"Okay so kike nakara kenan?"
Jin hakan yasakani saurin dagowa nace
"Tana cikin wurin'
"Ita ta tambayi mijinta kuwa?"
"Eh yace zaizo sutafi tare"
"Kece wato Kika rainani Baki tambaya ba ko, aidai komai yazo karshe daga yaune gobe kamar yanzu ankusa kaiki gidanki"
Shiru nayi kawai sannan nace
"Zanje wajen Ayshat tacemin yanzu zaizo sutafi"
"Kema daga Nan kiyi musu sallama don gida Zaki koma"
"Tare muke da Yaya fah"
"Eh zanfada Masa namaidaki gida"
Fitowa nayi daga motar batare danace komaiba,
Nasami Ayshat atsaye har zata tafi Nan muka fito tare da Nafisa muka rakata har mota mukayi sallama sannan nacewa Nafisa
"Nima tafiya zanyi"
"Saboda me kibari mutafi tare muma yanzu zamu wuce ai"
"Yana mota yace nafito ya maidani gida"
"Toh Ashe yazo muje nabashi hakuri nidai yabarki karku tafi kibarni nidaya"
Muna zuwa muka samesu tare da Yaya Nan suka gaisa da Nafisa ganin mijinta agurin yasakata kin yiwa Muslim magana yayane yacemin
"Kije ya saukeki agida muma yanzu zamu taho"
To nace tare da shigabama motar

Tafiya mukeyi Babu magana Sai sautin karatun alkur'ani Mai girma dakuma muryarshi dayake bin karatun,

Sai da mukazo kofar gida sannan yace
"Baby Wai fishi kikeyi Dani ne?"
"A a"
"To me akayi"
"Babu komi"
"To meye Kika wani hade rai kinyi shiru yaufa gabaki Daya Ina lure dake ko kallona bakiyiba fah"
"Uhmmmmmm" kawai nace tare da Wasa da hannuna,
"Shikenan nagadai kunyata kikeji jeki ki kwanta ki huta Sai gobe, please gobe karki gajiyarmin da kanki ki kwanta kihuta kinji?"
Daga kaina nayi tare da cewa
"Insha Allah nagode kaima kahuta da kyau"
Murmushi yayi sannan yace"kinaso na huta?"
Murmushi nayi batare Dana kalleshiba nace
"Sosaima kataba ganin matar da bataso mijinta ya huta" Ina kaiwa Nan nayi saurin bude motar

zan gudu kawai nayi ya riko min hannu yace
"Karki tafi bamu Gama magamaba, da gaske kike kinaso nahuta baby? Amma bantaba ji kinfada minba"
Muryata kamar zanyi kuka nace
"Please sakamin hannu to kar wani yaganmu ahaka"
"Menene don miji ya rike hannun matarshi?"
Shiru nayi sannan yadora da fadin
"Ni dama yayanmu yaganmu ahakan yace natafi dake danafi kowa farin ciki yau wallahi, kinsan yanzu yadda nakeji kamar na juya kan motar Nan mutafi gida mukwanta muhuta"
Kunya tagama kamani Amma na dake nafara magana batare Dana kalleshiba nace
"Tab aikuwa da anyi abin kunya wallahi gobe za,ayi yinifa sannan kace hakan mutane suzo ace Ina can ai Allah da bazan iya hada Ido da kowaba goben"
Dariya yayi sannan yace
"Ai dasauki tunda bani za,a kasa hada Ido daniba, toma Ina zakigansu har kiji kunyar?"
"Uhm kaidai dare yayi kaje gida kahuta Sai munyi waya"
Fitowa nayi banjira abinda zaiceba, Shima fitowa yayi tare da biyoni Yana fadin
"Bari na karasa ladana nakaiki har cikin bedroom sannan natafi"
Dariya nayi nace
"Dadai yafi"
"Ohhhh kice na birgeki hakan da nayi"
"Sosaima " nafada Ina dariya sannan na tsaya abakin kofar soran nace
"Nanma yayi nagode Allah yakaimin Kai gida lafiya kakulamin da kanka my one" Ina kaiwa Nan nashige gida da da gudu shikuwa yayi suman tsaye don abin ba karamin birgeshi yatiba,
Tunda yake Dani baitabajin wannan kalarmar abakinaba Sai yau don haka abin ya kayatar dashi sosai Kuma yafara tunanin kalar farin cikin dazai fuskanta acikin gidanshi Kai rayuwar aure akwai Dadi tundaga yau yafara shiga wannan abin Dadi akwai yawa,
Fuska cike da murmushi yafito yashiga mota yayi hanyar gida yanata doka murmushi kamar Wanda akayiwa bishara da gidan aljanna,

Bangaran amarya da ango wato Yaya Adam ansha dinner Wanda shi dukkan hankalinshi Yana kaina ahaka akayi dinner din aka Gama,
Ana gamawa amarya da ango aka kaisu gidansu don daman tayi sallama da gida dukda da bahaka aka tsaraba Sai asabar zata tare Amma dalilin want magani da kawarta tabata ayi amfani dashi a yaudin yasakata canja ra,ayi Nan takirashi tace tanaso daga gurin dinner suwuce gidansu lokacin Daya tanbayeta saboda me tace
Yabari Sai sunje gidan zaiji,
Suna zuwa gidan suka shige dakinsu Nan yace
"Kije kiyi alwallah muyi sallaha" kallonshi tayi sannan yace
"A,a nidai kawai muje much kazar can sannan ayi koma meye"
To yabita dashi don tsakaninsa da ita Babu musu,
Suna zuwa suka faraci bayan sungama suka shiga bandaki atare sukayo wanka bayan sunfito Sai suka faraci Shirin kwanci kallonshi tayi tace

"Baka tambayeni meyasa nace mutare yauba "
"Ohhh hakanefa inason nayi Miki wannan tambayar namanta meyasa kikace haka?"
"Uhm jinai Ina bukatarka kasan nayi kokarin rashinka sosai na tsahon shekara da wani abun shiyasa na Matsu najini kusa dakai, Allah Ina tsananin bukatarka fah my dear"
Murmushi yayi tare da zama abakin gado,
Kusa dashi tazauna Nan firar tasu ta canja
(🤔 Ohh ni deejah Allah ka shiryemu Shirin adinin muslinci kunjifa wannan watsewa don Allah, Kai duniya ana Sha,Ani Allah yasa mudace ameen).

********************

Washegari haka aka gudanar da yini cikin farinciki da annushuwa har yamma tayi lokacinne aka farayin Shirin kaini gidan Muslim,
Sai lokacinne na Kara tabbata da cewa dagaske gidan zanbari akaro na biyu hakan yasa nafara hawaye Nan aka shiga lallashina wanka nayi da wani ruwan turare sannan nayi turaren jiki bayan nagama wannan aka kawomin wani Abu Wai nashamyeshi duk Ayshat neh da Nafisa suka sakani agaba Sai faman turo Baki nakeyi gaba Ina hawaye,
Atamfa suka bani nasaka sannan nadaura dankwalin don Babu komai afuskana mayafi na yafa nasami guri nazauna bakin gadon Nafisa don adakinta muka wuni anan,
Yarane keta murnar ankawo motoci don haka mutane duk sukayi waje kowa yanaso yaje yashiga mota kar,abarshi abaya,
Wurin Innarmu suka kaini suna zaune dasu gwagwo da Inna salame 'yar uwarsu abbanmu da sauran Yan uwa Nan suka sakani gaba sukaitaimin fada daga karshe gwagwo ta kamamin hannuna ta karasar Dani kusa da Innarmu tace
"Gata Nan kiyimata fada Bari muje daga waje"
Duk kansu fita sukayi suka bamu guti jikin Innarmu nafada nasaki wani sabon kukan,
Kamani tayi ta rikemin hannun sannan tafara magana tace
"Kiyi hakuri mamana nasan dole kiyi kuka da kaddarar da Allah ya Dora Miki ta aure biyu kina cikin kuruciya, Amma wannan ba komai bane idon Kika dubi rayuwar wasu sannan inaso kirike gaskiya aduk inda kike, tsafta tsafta tsafta bazan gaji dajan hankalinki akwan wannanba don tsafta tana Daya daga cikin abinda yake sakawa mazajenmu suke gudarmu don wasu matan basayin tsafta yadda ta kamata Ina Mai Kara tunatar dake daki Sani tsafta itace abinda Zaki rike hannun bibiyu tare da hakuri, hauri shine maganin zaman rayuwa duk matar da Kika gani acikin gidanta tofah hakuri shike zaune da ita idon kikace bazakiyi hakuriba to wallahi bazakiji dadin zamankiba, don Allah mamana kizauna da mijinki lafiya, kidunga kallon mamanshi kamar yadda kike kallona, mamana kidage da yiwa mijinki girki kala kala acikin gidanki sannan karki yarda mijinki yaji wani wari acikin gidanki Koda yaushe ya kasance ko Ina na gidanki akwai kamshi, kinadai ganin yadda mukayi rayuwarmu cikin talauci Amma duk da haka Baki taba ganina nazauna cikin dattiba don Allah mamana kizauna da mijinki lafiya Allah ya Baku zaman lafiya Allah ya tsare ya rabaku da dukkan makiyanku ameen, tashi kije nasan anata jiranki"
Kuka nake tare da rike hannun Innarmu hakan da tagenine yasakata kamani ta fito Dani tsakar gida Nan suka kamani muka fita wajen mota,

Motane duk sungama shiga cikin motoci don haka muna shiga aka bar layinmu inata kuka,
Gwagwo ce takemin fadan Wai nadaina kukan haka ai taga yanzu Yan birni sundaina kukan aure nidai inajinta nayi banza da ita don nasan tsofane ke damunta,
Bansan inda aka kainiba Saida naji suna cewa mufito zamu shiga gidan uwar mijina agaidata Nan nagane gidan hajiya mukazo,
Munsameta afalo Nan muka zauna aka gaggaisa nidai Ina kudundune banbude kainaba hajiya har kusa dani tazo tadafa kaina tace
"Diyata kiyi hakuri kinji kibar kukan Nan haka karya saka Miki ciwon Kai"
Sassautawa nayi da kukan Jin abinda tace Nan suka gama maganarsu Mika fito don tafiya gidan,
Babu wani nisa don haka Babu wuya mukaje can,
Shiga akayi mutane nata shiga suna ganin yadda gidan yake,
Nan mutane sukaita santin gidan Ayshat mAh dake kus Dani itama Sai fadamin take wai gidan ya hadu sosai mantawa tayi bamuyi maganarba lokacin da sukaje jere nidai Ina jinta nayi shiru,
Bayan sallar magriba saiga abokinshi yazo yace da Nafisa za,a kaini gurin kwalliya dagacan za,a wuce dinner Suma sushirya kafin karfe bakwai da rabi za,a turo mota,
Nan tazo ta fada Mana nida Ayshat neh zamuje it zata zauna da kawayenmu dondaima dukkansu sun sakko kayan ankon nasu,
Munje wurin kwalliyar maisuna tafida itace zatayi Mana kwalliya,
Saida nayi sallah sannan na canja kayana nazauna don afarayimin dama ita Aysha tuni anfara yimata,
Kwalliya aka yimini sosai don tun wurin karfe bakwai akemin har karfe tara don lokacin Aysha tayi waya da Nafisa tace mata suna gurin dinner din mutane duk suncika sosai,
Suma bangaran angwaye suna waje suna jiranmu Muslim neh da Mahmud sukazo tare Ayshat tanacan wurin mijinta Wai yunwa yakeji shine ta tafi rakashi jikin wajen kwalliyar zaici abinci hakan yasa Muslim zama acikin motar Yana jira,
Saida aka Gama yimin sannan nakirata tace gata nan zuwa,
Samuna tayi zaune Ina danna wayata tana shigowa tafara fadin
"Wow wow Amarya Kinga yadda kikayi kyau kuwa wallahi kinhadu sosai wow gaskiya kinyi kyau nifa nama rasa abinda zance dake wallahi" turo Baki nayi sannan nace
"No ke barni kawai wallahi duk agajiye nake kamar zanfadi nakeji"
"Ayyah sannu Bari nabaki magani kifarasha akafin mufita" Jakarta ta bude ta dakko tabani nasha sannan mukayiwa Mai kwalliyar sallama mukayi gaba,
Amota muka samesu ni baya nashiga itakuma ta shiga gaba.

*Comment*
*&*
*Share*

*By*

*Khadeejah (Ummu Fu'ad & Afnan)*

*🙆🙆 RAYUWATA CE*🙆🙆

*Na*

*Khadeejah Sani (Journalist)*

*🌈KAINUWA WRITERS✍🏼 ASSOCIATION*🤝🏻
```{United we stand and succeed;Our ambition is to entertain & motivate the mind of readers}```

https://www.Facebook.com/kainuwawritersassociation

*🅿69_70*

Zaunawa nayi tare da gaida Mahmud amsawa yayi Yana tsokanata Wai amarya Bata laifi murmushi nayi kawai sannan nayi shiru,
Tafiya aka fara motar tayi shiru kowa da abinda yake tunani saikuma can Ayshat suka fara fira ita da mijinta,
Abinda bansaniba Ashe shi gogan naku Yana nan yayi suman zaune da ganin yadda nayi kyau nagama burgeshi yakasa ko dauke Ido daga kaina Sai zuwa can naji ya riko hannuna kallonshi nayi Sai Naga ya dagamin gira murmushi nayi sannan nace
"Barka da warhaka"
"Ohhh wato da Baki ganniba ko?"
Girgiza kaina nayi batare danayi maganaba jawoni yayi jikinshi sannan yace
"Baby kinyi kyau kyawun da bazan iya fadarshiba don idon zan fadeshi bansan mezan fara fadaba, abinda zan iya fada shine Ina kishin wasu mazan su kallemin wannan gayun wallahi Amma babu yadda zanyi dole nahakura"
Murmushi nayi sannan na kalleshi nace
"Aidai kafini yin kyauma" nakarasa maganar cikin sigar shagwaba,
```

Murmushi yakarayi sannan yace
"Karkiji zancen Wasa wallahi tunda nake bantaba kallon mace Mai kyawun kiba Kuma haka bantaba ganinki kinyi min irin kyawun da Baki taba yiminba, kinyi kyau da kalar wannan shiga ta fararen kayan Amma ni nasani kece Kika haskaka shigar ba shigarce ta haskakakiba baby wallahi Ina yimiki kaunar da bana tunanin.........."
Katseshi Mahmud yayi inda yace
"Kai malama wannan bayani haka kabari idon kuka koma gida kwayu yanzu lokacin mutanene don haka Bismillah tun dazu muka karaso Baku saniba"
Kallon wurin nayi azuciyata nace wow *meenah event center* yayi kalli wurin kamar rana bazaka taba tunanin dare bane idon kana ciki saidai idon ka daga kanka sama zaka gane hakan,
Fitowa mukayi sannan aka Gama gyara yadda za'a shiga cikin wurin taron,

Shiga mukayi ciki taro yayi taro mutane sun cika wajen ni abunma mamaki yabani ganin yadda wajen ya cika da mutane bayan mudai bamuyi rabon invitation hakaba,

(Kasan cewar ni journalist Ina cikin wajen dama tun da wuri nazo don kar arugani cin kaji😋🤣 don haka nazo da wuri can na gano Yan groups kala kala sunsha ankonsu irinsu *kainuwa writers, can na gano su, Ayshat m zazzau, Zarah Abdul, Anty fauzah 'yar amana, Nana Ayshat, Zarah Faruq, official khadyy*, da duk Yan kainuwa don Nafeesat tabani invitation nabasu don haka sun ziyarci wannan shagali, can na gano *RAYUWATA CE fans 1&2* su *anty fareeda anata kwaso shoki dasu sa,adatu Aliyu, hauwa ayuba, hidaya, mmn hanan, mmn mus'b, mmn haidar, mmn habib, anty Salma, anty shukrah,* da sauran masoyan Nafeesat duk suna cikin wannan taro, Sai sauran groups din Dana ganosu Suma irinsu Rayuwar muce haka fans, home of novels, da duk sauran masoyan wannan littafi dama masoya Nafeesat Baki Daya anata kwasar kaji anaci da kuma girke girke iri iri, Sai kwasar gara akeyi, nimadai ba,a barni abayaba wajen kwaso shoki don jikina har gajiya yayi)

Alhamdllh biki yayi Dadi yadda akeso anci ansha haka taro ya tashi cikin farin ciki da annushuwa,
Amotar Mahmud muka dawo Nan suka kawomu gida sukuma suka tafi nasu gidan,
Muna shiga nazauna kan kujera shikuma Saida ya kulle kofar falo sannan ya karaso kusa dani ya zauna tare da fadin
"Wash Allah Alhamdllh anyi biki lafiya angama gani ga masoyiyata akusa Dani yau ga mafarkin dana Dade inayi yauga burina dana Dade inaso yacika ya cika, Kai Alhamdllh" ya fada Yana daga hannnu sama,
Kallonshi kawai nayi sannan nayi murmushi tare da mikewa tsaye nace
"Saida safe zanje nayi Shirin bacci don agajiye nake" kallona yayi sannan yayi murmushi yace
"Lallaima baby me kike nufine da hakan wai?"
Kara kallonshi nayi sannan na kauda kaina nace
"Bacci fah nakeji"
Mikewa yayi tare da rikoni mukayi hanyar daki Yana fadin

"Nima inajin baccin don agajiye nake muje muyi wankan bayan mun fito Sai muci abinci don Ina lure dake awurin dinner bakici komaiba Sai lemo kawai don haka dura zan yimiki yau dinnan"

Shiru nayi nidai nama rasa abinda zance dashi Wai muyi wanka tare da shi, tab babbar magana kenan,

Muna shiga dakin na Sami bakin gado na zauna sannan nace

"Please kaje dakinka kawai Nima kabarni nayi abuna" kallona yayi zuwa can yace

"Okay shikenan jeki kiyi Nima Bari naje nayi"

Fita yayi daga daki don haka na Mike tsaye tare da dakko jakata don daukar abinda zanyi amfani dashi don akwai wani sirrin da nasamu a group din *gyara kanki* na *Anty khadeejah journalist* don haka na dakkosu na shiga toilet,

Bayan na Gama wankan na dawo daki na dakko kayana Dana tanada Wanda zansaka dama tun kafin yau na tanadi kayana saboda *Anty khadeejah journalist* tabamu sirrin kalar kayan da yakamata ace mace zata saka ranar da ta tare agidan mijinta don haka nasaka kayana na Kuma fasha turarurrukan da nahada sannan na yafa mayafina na Sami saman gado na Dane dama Saida nayo alwallah tah kafin na fito daga bandaki,

Ina zaune najishi zai shigo nayi saurin jawo mayafina na Kara rufe fuskata,

Shigowa yayi bakinshi dauke da sallama yasamu kusa dani ya zauna Yana Dan dariya yace

"Ohhh Wai kice sainayi sabon siyan Baki kenan ai nadauka dinner ta karbarmin Ashe abin ba haka bane?"

Shiru nayi hakan yasakashi matsowa kusa dani ya ciremin lullubin fuskata sannan yafara magana yace

"Baby Ina Kara godewa Allah Daya mallakamin ke amatsayin matar aurena Allah nagode maka, irin farin cikin da nake ciki bazai misaltuba tunda nake bantaba tsintar kaina a farin cikiba kamar na jiya da yau saboda nasami abar Sona wadda na dauki shekaru Ina dakon soyayyarta, nayi tsammanin zan Kara rasaki a Karo na biyu Amma Sai Allah ya dagamin ya cikamin burina ya taimakeni ya mallakamin burin zuciyata, don haka inaso kitashi muje muyi sallah don mukara Mika godiyarmu agurin Mai kowa Mai komai" Yana kaiwa nan yatashi tare da dagoni da kanshi ya dakkomin hijjabi babba nan muka tada sallah,

Bayan munyi sallah yayimana addu,o,I sannan ya tashi da kanshi yaje ya dakko ledar da Mahmud ya shigo da ita don Saida suka shigo har cikin gidan yayimana nasiha akan zaman aure tare da addu'o'i sannan sukayi Mana sallama suka tafi,

Zama yayi ya bude ledar tare d budewa yace

"Bismillah muci" kasa saka hannu nayi hakan yasa ya matso kusa dani ya jawoni jikinshi inata nukewa da mannani da jikinshi sosai yafara bani abaki har Saida na koshi sannan ya kyaleni Shima yadanci kadan,

Toilet na shiga nayi brush nafito,

Samu nayi baya dakin don haka na koma bakin gado nazauna,

Saigashi ya dawo Shima toilet din dakin nawa yashiga fitowa yayi da alama brush yayi,

Karasowa yayi kusa dani yazauna yace

"Bacci fah kikace min kinaji Amma naganki azaune"
Hawayene ya wanke min fuska hakan yasakashi saurin fara tambayata menene me akayimin meya faru menene
Nikuwa Babu abinda ya sakani kuka Sai yadda Naga ogan yanata wani rawarkai Yana lallabani shine abinda ya kashemin jiki nafara hawaye,
Ganin yadda ya rudene yasakani cewa
"Kainane yake ciwo" kanshi ya dafe sannan ya dago Yana Fadi
"Amma Kuma shine Zaki Kama kuka basaiki fadamin ba Bari nabaki magani kisha" tashi yayi ya dakko magani yabani nasha sannan ya kwantar Dani ya lullubeni yatashi yafita,
Ajiyar zuciya na sauke sannan na gyara kwanciya,
Harna fara bacci sama sama najishi ya dawo ya kashe wutar dakin yadawo ya kwanta kusa dani sannan yajawoni jikinshi Yana shafamin bayana,
Gabana ke faduwa don jikina harya fara rawa hakan Daya gani shine ya sakashi yimin magana yace
"Kiyi baccinki babu abinda zanmiki kinji?"
Hakan yasakani sakin jiki nafara baccinah,

Amarya da ango asuba ta gari,

******************

Washegari da asuba nice nafara farkawa Amma Jin yadda nake a jikinshi yasakani kwantawa nayi shiru har Saida ya farka da kanshi sannan yatashi Yana addu,ar tashi daga bacci sauna yayi tare da taba kafata yace
"Baby tashi muyi sallah zanje nayo alwallah a dakina indawo" to nace sannan ya fita nikuma na tashi nashiga toilet alwallah nayi sannan nazo nafara nafilah Saida na idar da sallah sannan yashigo kallona yayi yace
"Kardai kinyi sallahrki ke Daya Baki jiraniba?"
Murmushi nayi sannan nace
"A,a nayi nafilah ne"
"Ohhh yayi hakan tashi muyi sallah"
Tashi nayi muka gabatar da sallahr asbah tare da addu'o'i,
Kallona yayi yace
"Bacci bazai barmu yin karatuba muje mu kwanta "
Sunkuyar da kaina nayi sannan nace
"Ina kwana?"
"Lafiya kalau ya gajin bikin Yakima kan yadaina ciwon?"
"Eh ya daina"
"Masha Allah naji dadin hakan"
Tashi mukayi muka koma saman gado,
Yanzuma kamar dazu jawoni yayi jikinsa,
Ammafa sainaji labari yasha banban don jinai kafara wani abunda banganeba hakan yasa

nafara hawaye,

Nidai nace Allah ya inganta hajiya Nafeesat🤪

*****************

Bangaran su Yaya Adam anacan anatashan amarci shi harya gaji da wannan Abu ita Bata gajiya idon taganshi agida ta dunga takurashi kenan tana damunshi da tabe tabe idon yace mata yagaji Sai tace ita Bata gajiba don haka Saida yayi hakuri ya kyaleta,
Yauma kamar kullum suntashi da asuba yanasamu yashiga toilet don yayi wanka yayi sallah kawai yaga mata acikin toilet din tace
"Shine kagudo kabarni to muyi tare wankan" babu yadda ya iya dole suka farayin wankan amma ana cikin hakan sai wasa ya canja nan yafara niyyar kwace amma ina saidai taji ta gamsu sannan ta rabu dashi sukayi wanka suka fito,
Suna idar da sallah ya kalleta yace
"Dear Bari naje nadan duba Abu Ina zuwa"
Kallonshi tayi tace
"Kayi sauri don Allah dear don Ina bukatarka gaskiya"
Kallonta yayi cike da mamaki yace
"To Bari nazo"
Yana fita yashige dakinshi tare da rufe kofar da makulli Yana magana a fili yace
"Shikenan kinmaidani kamar wani dabba saikiyita damuna keba wani dadinki nakejiba bana samun biyan bukata yadda ya kamata Amma kiyita takurani, tsaki yayi sannan yace kawai kinsa na rabu da matata wadda nake masifar sonta yanzu gashi wani shege yaje ya auremin matata ai wallahi sainaji ajalinsa na dawo da matata na huta, kekuma Ina fatan Allah ya rabani dake inhuta ace mata ko irin Yar kunyar nan Bata da ita saidai mannewa namiji tayita takurashi ni wallahi duk maitata da mata wannan tafini, Allah neh kawai ya hadani da wadda tafini masifa" hakadai yayita surutun shi shikadai cikin hakan ya jiyo maganarta tana buga Masa kofa ya bude mata Amma yaki budewa yayi kwanciyarshi Yana jinta,

*******************

*Comment*
*&*
*Share*

*By*

*Khadeejah (Ummu Fu'ad & Afnan)*

*🙆🙆 RAYUWATA CE*🙆🙆

*Na*

*Khadeejah Sani (Journalist)*

*🌈KAINUWA WRITERS✍🏼 ASSOCIATION*🤝🏼
```{United we stand and succeed;Our ambition is to entertain & motivate the mind of readers}```

https://www.Facebook.com/kainuwawritersassociation

*🅿71_72*

Kwance nake asama a saman gado Banda ciwon jiki da kai Babu abinda nakeji gawani kalar zafi da yake tasomin daga kasana don haka tunda na fito daga wanka na kasa ko motsawa nake kwance Ina hawaye,

Shigowa yayi dakin don lokacin dana fito ban same shiba, shine ya hadamin ruwa ya sakani aciki Yana kokarin yimin wanka nasaki kuka nace yafita zanyi da kaina hakan yasakashi tafiya dakinshi Saida yayi wanka sannan yadawo dakin dauke da tea acikin cup Sai magani,

Karasowa yayi kusa dani yazauna abakin gadon tare da dagoni Yana fadin

"Haba baby nace kiyi hakuri kibar kukan nan haka karya saka Miki ciwon Kai please"

Kukan na daina Sai hawayen dake zirarowa ta idona kawai bani yayi nafarasha yasakamin maganin abaki nashanye sannan na koma na kwanta,

Tashi yayi yafita zuwa can Kuma Sai gashinan yadawo ya kwanta kusa dani tare da jawoni jikinsa cikin tsora nafara kokarin kwacewa ganin hakan ya sakashi cewa

"Please kiyi baccinki Babu abinda zanyi miki, idon kikayi bacci Kika tashi zakiji jikin yayi Miki sauki"

Jin abinda yace yasakani yin shiru Ina raba idanu don har lokacin a tsorace nake,

Bacci ne ya daukeni Ina Nan kwance bansan me yafaruba Sai karfe shabiyun Rana sannan nafarka,

Tashi nayi ganin baya dakin yasakani mikewa nayi toilet yanzu Babu laifi naji dadin jikin ba kamar dazuba haka nayi wanka nayo alwallah,
```

Fitowa nayi nasaka atamfa ajikina Riga da zani sannan nayi sallah don lokacin har Daya takusa kasancewar Saida na Dade a toilet nakara gasa jikina,
Baya na idar da sallah nazauna nadan gyara jikina nayi simple makeup sannan nagyara dakin sosai in Banda kamshi Babu abinda dakin yakeyi da jikina,
Fitowa nayi falon na sameshi zaune Yana danna system dinsa dagowa yayi Yana kallona Jin kamshin turarena yasakashi kallona har nazo kusa dashi na zauna tare da gaidashi kallona yake nikuwa nayi kasa da kaina don Banda kunya Babu abinda nakeji shiyasa nakasa hada Ido dashi,
Jawoni yayi jikinsa yace
"Lafiya kalau baby ya jikin naki?"
"Da....da....sau...ki"
"Allah sarki baby dazu nayi babban laifi ko ayimin afuwa bazan kara irin wannan laifinba Allah yayi Miki Albarka, saidai abinda nakasa yarda dashi shine ya akayi haka ta faru bayan nasan kintaba yin aure?"
Shiru nayi Ina Wasa da yatsun hannuna hakan yasa yace
"Kiyimin bayani Ina cikin wasi-wasi akan hakan don abin da abin mamaki"
Cike da Jin kunya nayi Masa bayani yadda zai gane akan zamana da Yaya Babu abinda ya shiga tsakanina dashi Sai suka da zagi,
Rungumeni yayi Yana murna tare da yiwa Allah godiya yafara fadin
"Gaskiya naji dadin hakan Allah na gode maka daka nunamin wannan rana Dana sameki matsayin da ko wanne namiji yake murnar yasamu matar aurenshi Allah na gode make dakasa wannan wawan bai samarmin matataba Allah Kaine ka tsare wannan baiwa taka Allah ka Kara tsaremin ita duniya da lahiya nagode Miki matata takaina Allah ya biya Miki bukatunki yahadaki Alkairi aduk inda kike yarabaki da duk sharrukan duniya ameen" yakarasa fada Yana sakar min kiss sannan yace
"Tashi muje muyi break tun dazu mom ta aiko Mana da abinci inata jiranki Baki farkaba"
Mikewa nayi Ina fadin
"Ayyah dama tashina kayi ai kokuma kaci abinka Naga Rana tayi sosai ai"
"Ai bazan iya ciba batare da keba nifa cin abinci tare da matata shine Abu na farko da nakeson yazama kamar farillah atare dani insha Allah"
Murmushi nayi kawai,
Muka karasa kan daining din nan nafara kokarin saving dinmu yace nabarshi na huta aikinshine wannan,

Bayan mungama haka muka dawo muka zauna afalo munata fira Wanda kusan shine Mai yintama,
Muna hakanne Sai mukaji ana nocking din kofar falon hakan yasakashi dagani daga jikinshi yaje yabude,
Muryan Ayshat naji hakan ya sakani saurin tashi Ina fadin
"Shinema Sai yanzu zakizo ko?"
Shigowa tayi suna gaisawa ta harareni tana fadin
"Ai wallahi badaban ya takura Wai nazoba da bazaki ganniba"
Kallonta nayi tare da zama kusa da ita sannan nace

"Saboda me to?"
"Saboda nabarku kusha amarcinku karna takuraku" dariya nayi sannan nace
"Kindai Rana kawai zakicemin"
"Eh narama" kirana naji yanayi Wai agaban Ayshat mah baby yake cemin abin yabani kunya na kalleta dariya tayi tace
"Gulma tashi kije Zaki wani Kama kallona to meye hakan?"
Tashi nayi Ina fadin
"Zakiyi bayanine Bari nazo"
Dakinshi na shiga kawai jinayi ya jawoni jikinshi Yana fadin
"Baby zandan fita zanje gida da asibiti don jiya nayiwa wani tiyata bankara zuwa na dubashiba Kinga gwara naje Naga jikin nasa ko?"
"Eh gaskiya hakane Allah ya tsare agaidamin da mom kafin nazo"
"Zataji Yar gidan mom" karasa maganar yayi da hade bakina da nashi Saida ya tsotse janbakin dake bakina sannan yace
"Alhamdllh" tare da Kara gyara jikinsa, Nima na daidaita nustsuwata sannan muka fito a tare,
Ayshat na zaune nan yayi mata sallama ya fita nikuma nazauna kusa da ita Ina fadin
"Me Kika tahomin dashi?"
Rike Baki tayi tare da fadin
"Kardai harkin Sami abun daga abunnan" dariya takeyi nikuwa kallonta nayi azuciyata nace dama ana ganewa Ashe ai bansaniba saikuma na tuna haryanzu tafiyata Bata dawo daidaiba don haka na Kara hade Rai nace
"Banason hakafa malama"
Dariya takeyi sannan ta bude Jakarta tare da Ciromin kula tace
"Gashinan danbune Nima mamarsu Mahmud ce ta kawominshi Ina niyyar tahowa saina dibar miki" karba nayi cikin zumudi Ina fadin
"Wayyo Dadi yaushe rabona Dana cishi dama"
Kallona kawai takeyi tana wani rausayar dakai alamar tausayi na bata,
Ajiyewa nayi nace
"Sai anjima zancishi ba yanzuna"
Murmushi tayi sannan tace
"Uhm hajiya kawas anzama mata" kallonta nayi sannan nace
"Banason wulakanci wai yauna farayin aurene dazaki wani dameni da magana"
Kallona tayi tace
"Lallaima yarnan kina nufin aurenki na baya Dana yanzu Zaki hadashine wallahi kinsan kema akwai banbanci idon Kuma Babu kifadamin inaji"
Banza nayi da ita natashi nashiga kitchen Kara dumama mata ragowar kaza nayi sannan nafito mata da ita nace
"Nasan dai wannan kikazo kici gashi Nan Allah yasa na rage Miki" kallona tayi tana dariya sannan tace
"Tab wallahi karya kikeyi yanda Kika cita jiya da dare akasha amarci Nima haka nacita Kuma muka Kara Shan wani amarcin dazaki wanice ita nazo naci"
Dariya nayi sannan nace "Aidai nice amarya duk abinki kekin tsufa gashi nan harda baby anan" nafada Ina nuna cikinta dariyar itama tayi tana shafashi tace

" Allah sarki my buy harkinsa ya juya"
"Waini watanshi nawama nagadai kwata kwata watanki biyu da Yan kwanaki"
"Watanshi biyu hajiyata"
"Ohhh Ashe shiyasa kikemin fatan Nima nasamu ko don ke bakisha amarciba Nima karnasha to ta Allah ba takiba"
Dariya tayi tana fadin
"Insha Allah lokacin da zakiyi wata Tara anan gidan Zaki haihu"
Shiru nayi Ina murmushi don Nima inason hakan harga Allah,

Wuni tayi Sai yamma sannan Mahmud yazo suak tafi suna tafiya Shima yadawo dama Ayshat saida tagama abinci sannan ta tafi ta jereshi a daining ta gyara gidan yayi tsaf yayi kyau,
Lokacin Daya shigo Ina dakinshi nagama gyarawa Ina jiyo shigowar motarshi nayi saurin shigewa toilet nahada Masa ruwan wanka,
Shigowa dakin yayi lokacin na fito daga toilet nace
"Sannu da zuwa"
Karasowa yayi ya jawoni jikinsa Yana fadin
"Haka ake taryar miji ai ba daga nesa nesaba" murmushi nayi sannan nace
"Ya mom take"
"Lafiya kalau tace tana gaida diyarta"
"Ina amsawa"
Zaunawa yayi abakin gado hakan yasakani saurin fara cire Masa takalmi da safar kafar,
Bayan na Gama nace
"Ga ruwan wanka can na had a"
"Ai Baki Gama aikinki bah"
Juyowa nayi daga jikin kwaba Ina Shirin debo Masa Kaya nace
"Na,am"
"Eh haka nace nasan kinji abinda nace ai don haka kidawo kikarasa"
"Ai bansan ko mezanyiba"
"Ki karasa aikinki mana, Baki ciremin kayan bah"
Ruke Baki nayi tare da zaro Ido nakasa magana,
Mikewa yayi Naga yayo kaina hakan yasakani saurin fita da gudu nayi dakina dariya yayi sannan yacire kayan yayi toilet don yayi wanka gashi magriba ya kusa bayaso lokacin sallah ya kure,

Koda ya fito daga wanka kayan Dana zaba Masa yasaka sannan ya tafi masallaci ba biyo dakinaba don sauri yakeyi kar atada sallah,

********************

*Agurguje*

Haka rayuwa taci gaba da tafiya cikin kwanciyar hankali da anushuwa muna nunawa juna kulawa daidai gwargwado har nakoma makaranta munfara exam shine yake kaini yawuce office dinsa idon nagama naje can nakirashi mutafi gida tare wani lokacin Kuma natafi gida idon ya kasance ranar zaikai yamma,

Bangaran su Yaya kuwa ababuwa suna tafiya yadda ya kamata anata zuba love saidai shi gogan naku abin yadameshi gashi hajiyar tasamu ciki tanata faman shagwabewa Sai ita Mai ciki shine ke Mata girki idon bashine yayiba bazata cishiba Wai bazata iya ciba don haka yadawo kuku kulluma shine yake mata girki safe Rana da dare ga wani kalar ci da take dashi yanzu tana Gama cin abinci zakaji tace yunwa takeji,
Hakadai aketa lallabawa tare da ita saidai mutayasu da addu'ar Allah ya Rana lafiya,

*******************

Mungama exam lafiya Alhamdllh munsami hutu Mai yawa tsahon wata uku,
Amma wani ikon Allah ranar da muka gama exam naje gida na yini acan don da safe muka gama tundaga gida nakejina banida lafiya ahaka na daure har yazo da dare muka taho gida,
Kamar jira muna zuwa Sai sanyi nakeji kafin Yan mintuna Sai zazzabi Nan nafara amai kafin wani lokaci harna fita Daga hayyacina,
Shikuwa duk yabi ya rude Yama rasa abinda zaiyimin kawai saiya daukeni yasaka amota nan getman ya budemasa get mukayi waje,
Cikin sauri muka karasa clinic dinsa nan aka fara duba lafiyata tare da yimin gwaje gwaje Wanda bansan anyi sauranba nidai nasan ansakani nayi fitsari nakasa ko rmtashi zaune shine ya kaini har toilet din ya sakani nayi yadiba yakaiwa doctor din.

*Comment*
*&*
*Share*

*By*

*Khadeejah (Ummu Fu'ad & Afnan)*

*🙆🙆 RAYUWATA CE*🙆🙆

*Na*

*Khadeejah Sani (Journalist)*

*🌈KAINUWA WRITERS✍🏼 ASSOCIATION*🤝🏼
```{United we stand and succeed;Our ambition is to entertain & motivate the mind of readers}```

https://www.Facebook.com/kainuwawritersassociation

*🅿73_74*

Kwance nake inata baccin wahala, don Saida akayimin allurar bacci sannan nayishi ganin yadda naketa amai gashi na galabaita sosai,

Shigowa doctor din tayi office dinsa inda yake tsaye akaina Yana aikin kallona,

Bakin gadon ta karaso tare da fadin

"Congratulation doctor" tana fada ta Mika Masa takardar tana murmushi dubawa yafarayi inda yaga cikine gareni na sati biyar ai baisan lokacin da ya kwanto kainaba Yana mika godiyarsa ga Allah murna yakeyi Yama rasa abinyi Sai kudi Mai yawa Daya bawa doctor din data kawo Masa wannan labari sannan yashige toilet din dake office din yayo alwallah yatada sallar farin ciki,

Bayan ya idarne ya dauki wayarshi yashiga Kiran mom dauka tayi tare da fadin "my son "

Ai ko amsawa baitsaya yiba yafara fadin

"Mom albishirin ki"

Murmushi tayi sannan tace "kome kakeso zan baka son fadamin menene?"

Dariya yayi cikin farin ciki yace

"Baby tanada ciki mom kinganmu yanzu haka muna clinic"

Cikin murna da zumudi tace

"Kai haba my son da gaske kakemin kokuma wasan da kasaba yiminne?"

"Kawai mom kizo kigani da kanki muna office dina saikinzo"

Kashe wayan tayi tare da mikewa tasaka hijjab tayo waje ko driver Bata tsaya kiraba ta shiga da kanta tafarayin driving da kanta tayo hanyar clinic din,

Bangarena bansan abinda yake faruwaba,

Kamar kiftawa saiga mom acikin office din tashigo cikin sauri lokacin shikuma ya kwanta a gefena yanata shafamin ciki Jin anbude kofar yasakashi tasowa da sauri mom din da yaganine yasa shi sakin dariya Yana cewa
```

"Ohhh mom irin wannan sauri haka" dariya tayi tace
"My son jika wasane ya jikin nata Allah sarki baby sannu kinji kalli yadda ta rame dama Bata da lafiya ne?"
"A,a wallahi mom ko daya harfa taje tayi exam yau suka gama shine nace tawuce gida zuwa yamma naje na dakkota, lokacin da naje muka taho take cemin batajin dadi" nandai ya Bata labarin duk abinda ya faru har zuwa yanzu,
Kasancewar mom doctor ce saita kalleshi tace
"Yanzu abinda za,ayi kasaka mata ruwa insha Allah tana tashi zataji dadin jikin"
Yadda tace hakan akayi,
Tashi yayi yace "mom Bari nayi sallahr magrib don namanta banyi wallahi gashi Naga Isha,I takusa"
Dariya tayi tana fadin
"Ohhh my son irin wannan zumudi haka ya Kuma da ranar da yazo ko tazo duniya?"
Dariya yayi sannan ya shiga toilet din office din,

Bani na farkaba Sai wurin karfe goma Ina bude Ido naganshi zaune kusa dani Yana ruke da hannuna murmushi nayi Masa tare da fara yunkurin tashi,
Kamoni yayi ya tadani zaune Yana yimin sannu kaina na rike sannan nace
"Banyi sallah bah"
"Zakiyi ai sannu yanzu meke Miki ciwo?"
"Kaina saikuma bakina Babu Dadi"
"Ayyah sannu Suma zasu daina a hankali"
Mikewa yayi Yana fadin "Bari na hada Miki tea kisha nasan kinajin yunwa"
"Banason tea amai zaisakani" dawowa yayi kusa dani Yana fadin
"Mezaki ci me kikeso?"
"Babu komi sallah nakeso nayi bani ruwa nasha"
"A,a baby kidaure kici wani abun dai please banason zama da yunwa"
Yatsina fuska nayi sannan nace
"Zanci waina da Miya da man shanu" dariya yayi sannan yace
"Ohhh baby kwadayi ko?"
Nima murmushi nayi sannan nace"sallah zanyi"
Kamani yayi Yana fadin "muje kiyi alwallah, waima yanzu Ina za,a Sami wainar Nan da kike fada?"
"Ana saidawa a bakin layinmu ai"
"Okay Bari inkira yayanmu naji ko zaishigo office yanzu saina bashi sako"
Tsayawa nayi da tafiya nace
"Please karka fada Masa" dariya yayi sannan yace
"Okay angama ranki ya dade"

Alwallah nayi nafito sannan natada sallah
Waya ya dauka tare da Kiran Yaya
Dauka yayi suka Kara gaisawa don Daman sun gaisa dashi lokacin da yaje daukata agida,
"Yayanmu don Allah kafitone?"

"Eh kaganni a kofar gida yanzu zan fito dai"
"Yawwa please ka tahomana da wainar shinkafa da Miya da manshanu a bakin titin Nan please muna Nan cikin clinic din"
"Okay Babu damuwa Amma lafiya kuwa naji kace Kuna clinic?"
Saida ya kalleni inata sallah a zaune don bazan iya yintaba a tsaye jiri nakeji sannan yace
"Kaganmu wallahi madam ce babu lafiya muna nan"
"Innalillahi meya same ta haka da sauri inace dazu kuka wuce gida meya faru" magana yake cikin tashin hankali da fargaba ganin hakan ya sakashi fita daga dakin don yanason ya fadamai abin farin cikin Daya sameshi sannan Kuma ya kwantar Masa da hankali don yaji har muryarshi ta canja,
Nan yafada Masa ai baima Bari ya Gama fadaba yakoma cikin gida da sauri Yana fadawa Innarmu abinda ya faru murna ta kamata Nan tayimin addu'ar Allah ya saukeni lafiya,
Nafisa dake daki itama fitowa tayi tana murna tare da rokonshi don Allah tazo suje tare,
Kallonta yayi sannan yace
"Taho muje ki tahomin da kullah babbah da karama"
Kallonshi Innarmu tayi sannan tace
"Mezakayi da kula Kuma?"
"Waina za,a siya musu yace"
Nan suka fito nafisa saboda murna ko baby bata daukaba tace tabarma Innarmu ita kafin ta dawo,

Lokacin da suka karaso harna idar da sallah Ina zaune abakin gadon na dasa Masa rigimar zansha icream shikuma yace bazansha Abu Mai sanyiba don haka nasami wuri nazauna inata hade rai shikuma ya shareni Yana danna wayarshi Yana satar kallona,
Shigowar nafisa ruke da kula yasakani yin murmushi nace
"Yawwa maman baby sannu da zuwa"
"Wacece maman baby Kuma bayan ke?"
Kallonta nayi cike da alamar tambaya sannan nace
"Yau kuma nizaki cewa mmn baby Ina babyn take?"
"Tana gida barta nayi acan tunda munyi sabowar baby"
"A Ina kukayi sabuwar babyn?"
Dariya tayi kawai tana fadin
"Kedai sannu Allah ya saukeki lafiya"
Kallon wurin da Muslim yake azaune nayi da niyyar nayi Masa korafin ya fada kawai sainaga yaya zaune kusa dashi don haka nayi saurin sunkuyar da kaina Ina Wasa da hannuna ni wallahi kunya nakeji,
Katsemin tunanin yayi da cewa "sannu ya jikin naki Innarmu Tana Miki sannu"
Shiru nayi tare dayin kasa da kaina Ina Wasa da hannuna,
Nan suka zauna sunata fira Sai zuwa can Nafisa tace
"Kinga na manta Bari na zuba Miki wainar kici ko?"
"Yawwa zuba mata please Nima na Sha,afa inata fira"Muslim ne yayi maganar cikin sauri,
Daukar plate tayi ta zuba min aikuwa cikin sauri da zumudi nafara aikawa bakina Ina lumshe idanu dan tayimin Dadi sosai,

Sunjima ana sosai sannan Yaya yashiga ciki don yayi aikin da yakawoshi Sai wuraren shabiyun dare sannan suka tafi don haka Nima nace mutafi aikuwa yace a,a Sai Ankara karamin wani ruwan naji dadin jikina sosai zuwa safiya saimu tafi rigima nasaka akan nidai kawai mutafi gida hakan yasakashi tashi Dole mukayi waje,
Muna fitowa cikin clinic din duk Wanda ya ganmu saiya tsaya ya gaidashi tare da yimasa congrat ni abunma har mamaki yabani ganin yadda lokaci daya har kowa yaji,

Mundauki hanyar gida ne nasaki kuka kallona yayi cikin tashin hankali yafara jefomin tambaya yace
"Meya faru wani gurin ke Miki ciwo menene fadamin please?"
Kallonshi nayi nace
"Don Allah kasiyamin ice cream wallahi jinake idon banshaba bazan iya komaiba please katai makamin don Allah" nakarasa maganar da sakin wani kukan
Hakan da yaganine ya sakashi cewa
"Shikenan zan siya Miki" godiya nayi Masa,
Munje wani guri ya tsaya yashiga saigashi da leda ice cream neh guda biyu aciki Nan nashiga murna nabude Daya nafara shanshi kafin mukarasa gida harna shanye don haka nafara kokarin bude dayan hanani yayi yace
"A,a Wanda kikasha is okay kibar wanna Nima nasha ko?"
Daga kaina nayi sannan muka shiga cikin gidan,

*********************

Alhamdllh iya kulawa dai Ina samunta awurin mom kizo Innarmu Yaya uwa uba kokuma nace Mai gayya Mai aiki ba,a magana agurinshi don har hutu ya dauka na kuka Dani shine dafamin wannan dafamin wancan kuka dani hatta wanka inda Yana gida banayi da kaina saidai yayimin,
Cikin hakanne Kuma muka cinye hutunmu Wanda lokacin cikina Yana wata hudu da sati biyu aikuwa Nan yasaka rigimar bazan komaba Wai ahakura da makarantar Sai bayan na Yaya yaron ko yarinyar sannan nashiga wata,
Nan Nima nace banyardaba Abu kamar Wasa Sai gamu da zuwa wurin Innarmu itama goya Masa baya tayi hakan yasa nayi fishi nafito daga gidan natafi gidan mom Nan naje nasameta zaune afalo tana ganina tafara murmushi tace
"Diyata sannu da zuwa kinji kina fama da kanki Kika iya tahowa Kuma bashine ya kawokiba sannu kinji?"
Nan nagaidata saikuma nafara tunanin abinda zance mata don abindai akwai kunya ace nakawo mata karar danta,
Fira mukayi sosai zuwa can nayi karfin Hali nafada mata abinda yake take Dani Nan tashiga fada tana cewa
"Ai wannan maganar banzace mata nawa keyin karatu da ciki saike zai Hana" Jin nasami karbuwa yasakani cewa
"Mom kumafa wanna kawar tawa matar Mahmud itama ciki gareta akma shine nizaice Wai

saidai nadaina gashi Ina nce2"
"Rabu dashi kinji karatu kamar kinci gaba dayi haka kawai ahanaki karatunki"
Murmushi nayi nan mukaci gaba da firarmu,

Shikuwa ban garanshi Yana ganina natashi na fito alamar nayi fishi Sai Shima ya tashi yafara sallama dasu Innarmu yafito ganin bai ganniba yasakashi yin murmushi ya hawo motarshi yayo gida don yasan nan zantaho fishin da nayine yasakani tahowata,
Yana zuwa samu bana Nan hakan ya daga Masa hankali yafara tunanin inda zanje Mahmud ya Kira yace Masa bana Nan don haka yayo gidan mom don ya fada mata bai taba tunanin Ina gidanba,
Yana zuwa yasamemu zaune munata fira Nan yazauna Yana gaidata amasawa tayi Babu yabo Babu fallasa Nan Tara yimasa fada sannan tace saina cigaba da zuwa makaranta ta Babu maganar yace bazan cigababa,
Daga baya Kuma ta Dora Mana da nasiha,
Sai dare sannan muka taho gida yanata wani hade rai nace kayi ka Gama ai nidai makarantace Babu fashi,

Saida mukaje nabashi hakuri har nasamu ya huce sannan mukaita firarmu,

*******************

Haka rayuwa taci gaba da tafiya inata zuwa makaranta cikina na dada girma,
Lokacin da mukayi exam din Gama nce2 sannan cikin Ayshat ya shiga watan haihuwa nikuma nawa Yana wata bakwai muka tafi hutu,
Bayan sati Daya da hutune Ayshat ta haifi yaronta namiji kyakyawa kamar mamanshi,
Munsha suna sosai yarinya taci sunan Fatima za,a dunga kiranta zarah.

*Comment*
*&*
*Share*

*By*

*Khadeejah (Ummu Fu'ad & Afnan (*

*🙆🙆 RAYUWATA CE*🙆🙆

*Na*

*Khadeejah Sani (Journalist)*

*🌈KAINUWA WRITERS✍🏼 ASSOCIATION*🤝🏼
```{United we stand and succeed;Our ambition is to entertain & motivate the mind of readers}```

https://www.Facebook.com/kainuwawritersassociation

*Assalamu Alaikum masoyana masoya wannan book Ina Mai Kara Baku hakuri na rashin jina kwanaki da yawa hakan ya farune sakamakon rashin lafiyar yayata, Amma yanzu Alhamdllh tasami sauki sosai*

*🅿75_76*

Kwance nake kan kujera ga wani irin ciwo da marata takeyi kwana biyu,

Kasan cewar tunda akayi suna bankara fitaba haka Shima ogan nawa baya fita Sai lokaci lokaci yake leka hospital dinshi,
Yanzuma bai Dade da fitaba yabarni Nan zaune Yana fita marar tawa tafara cuwo gashi lokacin komawa makaranta ya matso don saura kwana biyar mukoma,
Tashi nayi nakoma daki nakwanta tare da fara tunanin waima cikina yashiga wata nawane Nan namike naje na dauko scanning Dina naduba Naga acikin watan zan haihu saidai karshen watan Amma yanzu tun uku ga wata nafara rashin lafiya ga nauyi da yakara yimin hakan yasa nakara gyara zamana abin gado tare da dafe marata Ina maida numfashi da kyar kwantawa nakoma nakumayi nanma naji na gaji don haka nadawo kasan gadon nazauna Ina cije lebe,
Banji shigowar motaba kawai sainaga mutum akaina Yana jeromin tambaya
"Baby meyafaru me akayi bakida lafiyane meke Miki ciwo?"
Dagowa nayi na kalleshi sannan nabude bakina da karr nace
"Mar.....marata ke ciwo " a galabaice na karasa maganar don banajin zan iya Kara fadan wani abun kafin wani lokaci Sai naji kamar ruwa nazuba daga kasana kawai naji nayi yafara salati Nan yadagoni tare da fadin
"Innalillahi wa'inna ilaihirraji'un jini nake ganifah innalillahi"
Duk yabi ya rikice Yama rasa abinda zaiyi kawai saina dauki wayarshi yafara dannawa mom yakira tana dauka yafara fadin
"Please mom kizo Bata da lafiya jini ke zubar mata narasa abinda zanyi"
Cikin rudu tafara cewa
```

"Haba son saikace ba Dr bah please dauketa kutafi hospital gani Nan zuwa muhadu acan"
Kashe wayan yayi tare da daukana a kafada yayi waje amota ya sakani sannan yashi yafara driving cikin sauri,

Nidai nasan munje hospital Amma tundaga lokacin da Naga ya dakkoni bankara sanin meke faruwaba,
Shikuwa lokacin Daya daukeni yayi ciki Dani Nan doctors suka hadu akaina har lokacin da mom takaraso Nan duk suka Bata waje sanin dama ita din babbar likitace,
Kokarin tsaida jini akeyi amma ina hakan yaki yiwowa hankalin kowa atashe yake Muslim kuwa anma hanashi shiga cikin dakin gabaki Daya duk yabi ya rude yakasa zaune yakasa tsaye,
Tun wurin karfe biyu na rana har yamma likis sannan mom tasami damar tsaida jini Nan aka daura min wani jinin don jinina ya kare da yawa,
Saida mom taga nayi bacci sannan ta sakashi gaba tace yakira Innarmu yafada mata saboda tazo ita tanason zuwa gida tayi wanka don duk jikinta ya baci da jini,
Daukar waya yayi yakira yayanmu yace
"Please Yaya kakawo Mana Innarmu asibiti yanzu nafisa Babu lafiya"
Hankalina Yaya atashe yace gasunan zuwa,

Baifi 10mnt bah dayin wayar sai gashi tare da Innarmu da Nafisa sunzo hankali atashe gashi har lokacin ba,a Bari aganni Amma anbar Innarmu tashiga taganni shikuwa ogana har zuwa wannan Tim din mom tahanashi shiga ganin yadda ya tada hankalinsa yasa tace bazai shigaba yaganni a halin da nake ciki,

Saida nayi kwana Daya da wuni sannan aka barshi ya ganni aikuwa lokacin da yayi tozali dani akwance ansamin abin numfashi kuka yafara yiwa mom don dama tare suka shigo rigima yafara waishi kawai ayimin aiki acire cikin ya hakura da samun babyn kawai ayimin CS,
Hakuri mom tabashi tare da Fadin
"Babu yadda za'a,ayi ayimata CS gashi jinita ya hau kayi hakuri zuwa gobe mugani nima sonake ayi mata CS din kaidai kayita yimata addu'a ita take bukata Allah yarabata dashi lafiya" haka taita kwantar masa da hankali harna wani lokaci sannan tasamu yadan nutsu Amma juyin duniya tayita fama dashi akan yafito yaki haka tarabu dashi zaune bakin gadon da nake Yana rike da hanuna,

Saida nayi kwanaki hudu ahaka bansan Wanda yake kainaba sannan aka samu jinina ya sauka aranar da za,ayimin CS ranar na farka ina bude idona ahankali na dago da kaina kawai sainaga Muslim akusa Dani Yana kallona murmushi nayi Masa Shima maidamin yayi tare da rikoni sosai Yana jeromin sannu kokari tashi zaune nakeyi nakasa,
Kara rikeni yayi Yana fadin
"Tashi zakiyi?"
Daga kaina nayi alamar eh don haka ya dagoni tare da sakani jikin filo ya gyaramin zamana sannan ya zauna kusa dani kallonshi naketayi Sai can nace
"Yaushe mukazo Nan"

Murmushi yayi sannan yace "kedai Allah yabaki lafiya kinji"
"Ameen" shigowar Dr ne yashigo dakin Nan suka gaisa dashi tare da tambayata ya jikin nace dasauki Nan yace
"Lokaci yayi nurse zata shiryata yanzu zamu shiga"
"Akawo komai zan shiryata da kaina"
To yace tare da juyawa waje,
Gyara zamana nayi sannan na kalleshi nace
"Wai meza,a yimin?"

"Saboda ana tunanin bazaki iya haihuwaba shiyasa ake tunanin yimiki CS yau za,ayi Miki kihuta banason ganinki cikin wani hali"
Kallonshi nayi sannan nace
"Nidai banaso kawai abari insha Allah zan haihu da kaina basai anmin CS bah"
Kamo hanuna yayi yace
"Kibar fadar haka kibari kawai ayi Miki hakan zaifi tunda Kinga halin da kike ciki kwananki hudu Amma bakisan Wanda yake kankiba please kidaina fadar haka kinji"
Hawaye nafara yi tare da fadin
"Nidai banaso ayimin please karka Bari ayimin " nafada tare da fashewa da kuka,
Lallashina yashiga yi har nayi shiru yadunga lallabani akan karna tada hankalina nabari ayimin Allah yasa hakan shine mafi Alkairi,
Haka aka kawo kayan da ake canjawa mutum idon za,ayi Masa CS shine da kanshi ya sakamin Nan nafara rokonsa gafara akan ya yafemin bansaniba ko mutuwa zanyi,
Aikuwa yanajin abinda nafada yafita daga dakin yaje yasami Dr din yace gaskiya afasa yimin CS shidai tsoro yakeji don yaga Nima banaso Kuma ga abinda nake cewa,
Dr yafara bashi Baki da cewa
"Karkace haka Insha Allah wannan aikin da za,ayi mata Babu matsalar komai Kuma zata tashi insha Allah don haka kayi hakuri Dr karkace haka"
"A,a kawai abarshi tunda Naga itama baso takeyiba kuma Nima jikina yayi sanyi da wannan aikin da za,ayi mata kawai ahakura abarta Allah ya sauketa lafiya"
Ganin yadda ya dage akan maganar yasa Dr Kiran mom da Innarmu Nan suka shiga bashi Baki akan abinda yacedin,
Da karr suka samu ya amince ayidin Amma duk da haka shidai yafi ganewa abarni din tunda Nima nace banaso,

Lokacin da akazo za,a tafi Dani nashiga kuka Ina neman gafarar Innarmu da mom sumadai dukkansu jikinsu yayi sanyi ganin yadda nake kuka Ina rokon gafararsu,
Haka aka wuce Dani inda Muslim yashige office dinshi Yana kuka kamar wani karamin yaro,

Shigarmu keda wuya har andorani kana gadon naji wani kalar ciwo Yana tasomin Nan nafara dafe marata da bayana wani irin ciwone y tasomin Wanda tunda nake bantaba Jin irinshiba a fadin duniya ganin hakan yasaka doctor din Kiran wara doctor mace tazo kaina Nan take sanar dashi haihuwace kila zan iya haihuwar da kaina Adan jira agani,
Fita sukayi sukabar doctors mata akaina cikin kankanin lokaci saga kan yarinyar yafara fitowa

doctor dince taketa rikeni tana fadin kidage kiyi Nishi sosai,
Nikuwa kasawa nayi don karfina gabaki Daya ya kare,
Ganin hakan yasaka suka taimakamin wajen faddo da yarinyar aikuwa kuka tafarayi iaya karfinta alamar lafiyarta kalau,
Nan suka shiga gayarani tare da baby suka fita wajensu mom da Innarmu suka karbo Kaya Nima Saida nacanja Kaya sannan aka kaini dakin hutu su mom natayimin sannu kallonsu kawai nakeyi Amma nikadai nasan abinda nakeji a cikina da marata ganin yadda nake binsu da Ido yasa mom dauramin ruwa tare da allurar bacci,
Baccine ya daukeni bansan wainar da ake toyawaba,

Shikuwa ogan nawa yanacan baisan abinda akeyiba duk yadamu ya kago yaga anfito Dani yasandai bazasu wuce 1 hour bah,
Tagumi yayi yanata tunani kala kala kawai yaji ana kwankwasa kofar office din kamar bazaiyi maganaba saikuma yabada izini,
Ganin doctor din dazai yimin CS yashigo yasakashi mikewa tsaye cikin tashin hankali Yana fadin
"Dr meya faru harkun Gama tana Ina Taki sauki please kabani amsa?"
Murmushi yayi sannan yace
"Kwantar da hankalinka Dr ta haihu ansami baby girl"
Ai baitsaya yagama Jin abinda yake fadaba yaja hannunsa sukayi waje don murna ta ishesa Yama rasa abinda zaiyi maganarma yakasa kawai Jan Dr yakeyi Yana nuna Masa hanya da hannu alamar yakaishi dakin da take,
Suna shiga dakin lokacin nayi bacci mom na rike da baby ko kallon wajen da baby take baiyiba yayi wajen maman babyn Yana tabata tare da fara magana yace
"Sannu baby nah Allah yayi Miki Albarka Allah ya biyaki da gidan aljanna nagode baby nah sannu please kibude idonki naganku ko zansami kwanciyar hankali" maganganu kawai yakeyi batare da lura da waye ke cikin dakinba Allah yasama mom CE kadai Innarmu ta tafi gida zata dafo ruwan zafi,
Mom ce ta katse Masa maganganun da yakeyi tace
"Ohhh my son kabarta ta huta Mana karka tadata"
Shiru yayi tare da yin murmushi yace
"Mom ammadai lafiyanta kalau ko?"
"Son saita farka sannan zan dubata Amma naji Dr tace anyi mata dinki don haka Sai akiyaye"
Karbar babyn yayi yafara yimata addu'a tare da yimata huduba da sunan mom nan ya kalli mom yace "mom kinyi takwara "
Murmushi tayi tare da karbar babyn tace
"Wow nagode sosai Allah ya rayamin ke takwarata"
Ameen yace tare da komawa kusa dani abakin gado Yana kallona,
Bansan wainar da ake toyawaba don bacci nakeyi na gajiya kunsan dai yadda mace keyin bacci Mai nauyi bayan ta haihu balle ni da akayiwa allurar bacci don nahuta,

Har Nafisa tazo itada Yaya banfarkaba shikuwa ogan nawa Yana kusa Dani har mom Saida tayimasa tsiya tace

"Ohhh ni son kakasa barinta ta huta duk kabi ka takurata katashi kaje gida kayi wanka Mana saika dawo kokuna kabari Sai Allah ya kaimu tunda dare yayima ai"
Kallon mom yayi sannan yayi murmushi yace
"Ai mom kafata kafarta don jira nake tafarka muwuce gidama yanzu kuwa"
Rike Baki mom tayi sannan tace
"Amma kadai Bari likitan daya karbi haihuwar yabata sallama ko?"
"Mom akwai likita bayan nine nifa zan rubuta abuna da kaina, fatana kawai Allah yasa idon ta farka tatashi lafiya kalau"
Murmushi kawai mom tayi tare da juyawa ta kalli nafisa suka cigaba da firarsu,

Sai wuraren karfe 8:30pm bayan Muslim yadawo daga masallaci nafarka,
Kallonshi nayi yanata sakarmin murmushi Nima mayar mishi nayi sannan yace
"Sannu baby ya jikin Ina fatan Babu abinda yake damunki kokuma akwai inda yake yimiki ciwo sannu baby Allah yayi Miki Albarka baby" gabaki Daya Yan dakin binshi sukeyi da kallo shiyama manta dasu awurin don lokacin yayane zaune da Nafisa mom taje gida zata dawo gobe don Innarmu ce zata dawo da dare zaije ya dakkota,

Murmushi nayi sannan na kalli Yaya dake jeromin sannu na amsa Nan Nafisa itama tayimin sannu,
Kamani yayi tare da tadani zaune Yana Kara tambayata inda yake yimin ciwo,
Yastina fuska nayi sannan nace
"Nifa dukkan jikina ciwo yakeyimin ga marata da cikina" nakarasa maganar da turo Baki,
Tashi yayi Yana fadin
"Bari na hada Miki tea kisha sannan kisha magani"
Nafisa ce tamike tace
"Bari na hada mata"
"Yawwa nagode to bara na karbo maganin awajen doctor din" yayane ya Mike Yana fadin
"Bashshi na karbo jeka kula da babyn taka" dariya sukayi su duka harda nafisa sannan yadawo kusa Dani yazauna nikuwa cikina na ruke saboda wani kalar ciwo da yake yimin,
Sannu yaketa jeromin nikuwa nakasa amsa ko Daya aciki duk nabi na kudundune wuri Daya dalilin ciwon ciki da Mara,

Saida nasamu ya lafamin sannan nasha tea din tare da Shan magani nakoma na kwanta Ina rike da ciki,
Momce ta kirashi tare da tambayar nafarka Nan yake fada mata nafarka Amma Kuma ciwon ciki da Mara ya dameni har yanzu danasha magani,
"Babu komai insha Allah zai daina ai dama Dole zatayi ciwon cikin Amma insha Allah zata daina bada dadewaba, Bata wayan muyi magana"
"Mom bazata iya maganaba kinganta a dunkule mah takasa tashi ko zaune"
"Ayyah kakula da ita son kukoma ka Kira Dr rukayyah takara dubata"
"To mom Bari na kirata din"
Yana fada yakashe wayan tare da tashi zai fita yayane yace
"Bari naje gida na dakko Innarmu idon nadawo saimu wuce" fita sukayi tare yatafi gida

shikuma yaje ya Kira likitan,
Lokacin da sukazo likitan tace sujira awake shida Nafisa Nan suka fita tashiga dubani tare da tambayata yadda nakeji nidai kasa yimata magana nayi har tagama dubani ta fita.

*Masoyiyata kinsakani yin typing yau Amma banyi niyyar yiba saboda ke nayishi kinkirani kina niyyar yimin kuka ko uhmm zamu hadune, Amma karki manta Nima Ina sonki Mrs khalil kina Raina Allah yabarki da khalil har abada ammafa yakaro Miki Yar uwa bake kadaiba*🤪🤪🤪🤪🤪🤪🤪🤪🙈

*Kuma masoyana Ina yinku Kuma Kuna Raina ban mata dakuba kullum Ina tunaninku sosai da sosai*❤

*My Indo zazzau Allah yabada sa,ar exam yabada A A bamason B mah Kuma Allah yabarki da masoyinki musha biki Ina sonki Mrs Abbas kina🔥 Ina binki da fetur*❤❤❤❤

*My blood sister kemafa ba,a barki abayaba Ina yinki kanwata ta kaina bani da wadda tafini cikin kanne Ina sonki Feenah Allah ya fiddo da admission lafiya mutafi US rakiya please ko atayar jirgine kisakani👏*

*Comment*
*&*
*Share*

*By*

*Khadeejah (Ummu Fu'ad & Afnan)*

https://m.facebook.com/Anatarewritersassocian/

*👨🏻‍✈️CONEL AKRAM👨🏻‍✈️*
*(AK)*

*BY*

*FAUXIA MB(ME AGOGO ⏰)*

*🤝🏻ANA TARE WRITERS ASSOCIATON🤝🏻*
*(we are the best writers among the all)*

*SADAUKARWA GARE KU*

*Kungiyar*
⬇
*❤❤❤❤❤❤❤❤ ANA TARE WRITERS ASSOCIATON* ~~ONE LOVE ALLAH YABAR KAUNA~

1️⃣3️⃣0️⃣➡1️⃣4️⃣0️⃣

🔜Ahankali yaringa bin da duk wani sako najikinta ya lashewa hade da shafawa, adaidai Kan bombom din ta  hannunsa ya tsaya "plss Amaaaaal inason yi yafada cikin dashewar muryar dakuma Jan sunan ta Wanda Bata taba tunin yasan sunan  nataba, plss I need you" yakuma fada idonsa still arufe yake Amma hannunsa Yana Kan bombom dinta dayake luguiguitasu kamar yasami pillows, plss yakuma fada Yana Kuma kwantowa a jikinta kamar besan irin nauyin dayake dashi ba. "plss  karfa ka karyani  tafada itama idonta a rufe, saboda sosai sakonninsa suke kaimata,

"Wai bakowa a gidan ne, yafendo ke neman Amal tunkusan minti arba'in da suka wuce take zagaye rooms din gidan gabadaya tana tunanin Ina Amal tashi ga, Sai da tazo daidai  corridor din daze hadata da dakin AKRAM, tadan daga murya karta leka Kuma tsufanta yazama na

banza.( hahaha yafendo kenan ai da kin leka, kyatuna abun dayafaru 1960s lols)
Afirgice takwace jikinta daga nashi tana neman hijab din ta saboda Jin muryar yafendo kamar takusa shigowa bedroom din, hannunsa yasa ya rikemata hannun indonsa arufe, plss karki tafi bashugowa zatayi ba plss yakuma fada indonsa still a rufe yake,

"toh nidai kacika ni Insaka hijab karta shugo Amal tafada kamar zatayi kuka,hijab dinta tadauka tana nufar kofar fita hartakai bakin kofa bataji yayi magana ba. Juyuwa tayi Daman hannuka ya warke ta tambayeshi ta fita dakin aguje,

Ahanakli yabude Idonsa ganin Ko keyarta be hanga ba yasaka shi yin wani murmushi hade da shafa sajensa, se kuma ya safe cikinsa da Saudi Jin irin yanda ya murdai mai, "why yafendo" ya fada in a low voice Yana me Jin ciwon ciki sosai saboda yasan dole haka zata faru daman ya lafiyar kura ballanta taga samu taga rashi Amma babu kimai next time ko hajiyarsa ce baze Bari ba ya fada a zuciyarsa, lols toh fa.....

"Amma ummi inazaki da wa yanan kayan haka, ita kanta goribar nan tayi yawa ga magarya,taura, tsamigaye, adu'a, charbin malam, duk ita kadai Wai cemiki tayi kisiyo mata ne?" Yaya Malik ke tambayar Yana kallon umminsu da taketa  harhada ledodin kayan tsarabar data siyo. "muje ni don Allah" ta fada tana daidai ta hijab din ta ruwan ganye Sabo dal yaci goga,

" uhm" ya Malik yafada Yana cewa "kawo in tayaki toh" yana gyara Zaman hularsa.

mikamai tayi tana "da yafiye maka da wanan tambayoyin da kakemun kamar kaika aikeni, muje Don Allah Kar Rana tayi"

Yau acikin farin ciki take GA zuwan su Yaya Malik ga nasu isy duk ta hargitsa gidan da kamshi girki take yi tun goma har sai daya aka gama, dukkan abun da take Yana kallon ta mamaki kadai take bashi yanda ita kadai tai uban aiyukan nan, Ahankali yake tura kekensa Yana nufar hanyar kitchen din saboda yasan yanzu yafendo na bacci,

Kanshi dataji ne yasa ta Juyuwa duk da tasan waye me kashin turaren Amma tana kokwanto,

"sannu da aiki" kamar bashi yayi maganar ba, "plss make a cup of tea with lime for me" yafada Yana juya Kan wheelchair dinsa Yana nufar parlour.

Lemon tsami tadauko ta wanke ta matseshi acikin cup tacire kwallon bayan tasaka sugar da lipton a mug din ruwan zafi ta zuba tukunan tadan juya shi kadan lipton din tacire bayan taga yayi baki sosai lemon tsamin tazuba a mug din data hada masa shayin, dauka tayi ta dora a katamin tray, a hankali take tafiya har takarasa inda ta gansa ya sauka daka Kan wheelchair dinsa Yana Kan 3sitter kallon sa take kawai tunjiya take mamakin yanda yaringa yimata da hannunsa yanzu Kuma gashi azaune da kansa bawani bane yasauke shi, girar sa daya yadaga Mata Yana karbar tray din  shayin daga hannuta, "karki fa Kona ni" yafada Yana kallon idonta da still itama shi take kallo,

Dauke idonunnata tayi tana Jin kunyar kallon dayake ta bin kirjinta  dashi tun shigowarta.

"nagode" tare da damke lallausan hannuta, ganyewa tayi a hankali tare da cemasa "Inakwana" tana dan tsugunnawa tana wasa da gashin jikin carpet din parlourn,

"lafiya kalau" ya fada Yana kare Mata kallo Saboda fitted gown ce ajikinta takamata sosai duk shape din ta a bayyane yake tana daya daga cikin a tamfofinta  da  isy takaimata dinkinsu dan kusan rabin laifan isy takai aka  dinkesu, haka Taylor din ya mata dinkin garari masu tsumar da mutum acewar AK ranar da ta fara saka daya saga cikin dinkunan.

Ita dai kanta akasa tana wasa da carpet, karar bude get taji ta tashi tana lekawa ta window kallon ta yake Yana ganin irin murnar da take," suwaye"
taji yafada Yana Kai mug din bakinsa,
"su ummina ce da yayana" tafada harda tsalle,

"Babu Kara wani umminki ke kad'ai babu komai nagode, Amma yanxunan zan kwace su agabanki yafada Yana kanne Mata ido daya, shan tea dinsa yake kamar bashi yake magana ba, hararsa Tayi tana murguda Mai baki wallahi baka isaba tafada kamar zatayi Mai kuka,

" haka kikace" yafada Yana kallon ta yanda ta ke murguda masa Dan bakin ta kamar na tsuntsu.

"eh" tafada tana Kuma murguda masa bakin, bata ankara ba taji ya kama bakin ya tsotseshi tare da dan cizonta. Ta bare Bak zatai ihu taji karar door bell kenan har sun zo bakin kofa. ita ta tashi ta saka security pin  din kofar ta bude  Emanuel tagani "ajiya akwai bako Yana jiranka"

"Let them in" yafada Yana daga inda yake zaune, mamaki ne yakama Ema yanaso yaleka yaji waye yake magana kamar oga, Amma Ina Amal taki bashi dama Don kofar ma kadan tabude ta saboda dankwalin ta taware tayafa, ahaka ya juya   Yana murnar oga yawarke tunda yafara long magana, pls go and put on your hijab ya fada Yana gyara Zaman sa sosai hade da ballar wasu tablets Akan side table din dayake kusa da shi,

Juyawa tayi tanufi bedroom dinta da Sauri Don bataso ya rigata ganin su umminta,

Assalamu alaikum inji Yaya Malik Yana tura kofar parlour din da baagama budeta ba,Ahankali ummi itama tayi tata sallamar tana gyara yar pouse din ta,

"Waalaiku assalam yafada da fara'a sosai afuskar sa, sannun ku da zuwa yafada Yana mikawa Yaya Malik hannu sosai ummi taji dadi ganin be kyamace su ba," ummi sannu da zuwa taji yafada Yana sunkuyar da kansa, ita duk kunya ta'isheta gata ga siriki, "yauwa sannun ka tafada tana neman guri can nesa da su tana zama,da gudu ta nufo cikin parlour din inda ummi take tana zaune,  wani tsalle tayi ta haye Kan cinyar ummi" oyoyo oyoooo ummina tafada tana kuma rungumeta, kallonta kawai yake yana murmushi, sosai take cikin farin cikin zuwan ummin ta da yayanta anazaune anahira Sama-Sama wanda duk hirar tafi karfe tsakanin Yaya Malik da AKRAM,

"baki mukayi agidanne inji yafendo datake fitowa daga dakin datasaka Mai sunan nata, ah ashe ku ne sannu ku da zuwa Fatima ashe kune ke tafi," yauwa yafendo ina wuni yagida mun same ku lafiya"inji ummi tafada tana dan tsugunnawa yafendo. "lafiya kalau wallahi sannu ku da zuwa"
"yafendo ina wuni cewar Yaya Malik da yabari suka gama gaisawa da ummi tukunan Shima yagaidasheta, (take note Yana da kyau Yara sunriga barin manya sugama gaisawa Sai suyi gaisuwa suma) itadai  farin ciki kawai takeyi. yafendo aron wayarki" tafada saboda sun saba indai ba da line land zatayi amfani ba ta yafendo take ara.. "hello Wai kunfasa ne tafada kamar zatayi kuka Okey okeyy tohm shikenan tafada tana kashe wayar, door bells kirr|rr|r| yakarade parlour din gabada daya, anutse tanufi kofar da touching pin din jikin kofar tayi tadanna 8880 duk kofofin gidan pin dinsu kenan, Kuma shi kadai yasani Sai ita,karfa ku gayawa zayyan! Lols.....

Kirrrrrrrrrrkirrrr| hahaahahhha gud job KOLO  aikin ka Yana kyau plssss katabbata yarinyar Nan ta zuba masa poison din nan dukkansa hahhaahhaahh yakuma kwashe wa dariya hahahhahha,

ai ME GANYE kayi babban kuskure Sai da wani bakai ba hahahah. Kana Jina kasame ni a SAMARU ZARIA gida no 304, ka karbi balance din ka, dif yakashe wayar,

Duk inda tagifta bin ta yake da da idanu saboda komai nata shaawa yake bashi, Yana mamakin kansa kodan be taba SOYAYYA bane Amma yayarda kumai LOKACI NE littafi fauxia MB me agogo⏰
 Sosai kowa yaji dadin haduwar nan, anyi hira sosai anyi exchanging din number babu abun da ya birgeni irin yanda Yaya Malik ke satar kallon ihsan da tunda tazo tana kusa da ummi haduwar su ta uku kenan duk da bazuwa gidan tayi sosai ba lokacin auran su Amal Amma sosai takeson ummi saboda macece me tsoran Allah da rashin son magana, Ita daman tafi son irin wanan mutane,

Yana laakari da ita tunda suka zo kusan 2hours amal da yafaendo da su Islam suke hira Sai some times ummi take tsoma bakinta,saboda kunyar AKRAM Amma shi ko ajikinsama, don ko da zaaci abinci nunawa yayi hannu sa haryanzu be warke ba kowa Sai sannu yake mai Amal inbanda hararsa babu abun da take saboda cewama yayi shi ta ajiye spoon da ta dakko da hannu zata bashi yafi Lada ko Kunyar su umma bayaji, umma hadda mata fadan tasan baya iyacin abincin amma tazauna tana hira kowa nacinnashi seda yayi magana. Shiko yana ci Yana hadawa da hannu ta Wanda yake cizonta kadan, harcikin tsakar kanta Sakon kezuwar mata, a haka yaringa dagula Mata lissafi da cizon hannunta har kowa yagama ci shi Yana cewa be koshi ba.

Su Yaya Malik ne suka fata tafiya Don umma cewa tayi agida zatayi sallar laasar, Emanuel Ak yasa yamaidasu Wanda dakyar umma ta yadda, Yaya malik shi da yake d'an yau ne ko ajikinsa murna ma yake saboda daman ana musu gorin sun siyar da Amal, tunda tayi Aure Bata zo ba,tunda suka tafi duk wata majalisa ta munafukai Sai da yasa Emanuel yabi dasu harda sa Emanual yakashe Ac yabude window duk dan yakashe bakin yan gulma, aikwa dai yadauki magana duk wata majalisa ta marasa aikinyi hirar wucewarsu ake yi,su natafiya ba dadewa su isy suka tafi Wanda yafendo take ce musu "kucewa mutan gidan Ina gaidasu, Mundai yi waya da ita babartaku dazu", yafendo tafada tana nufar dakin da tamaidashi nata lols,

Amota Inbanda zuba babun abun da isy take tana fasalta yanda birthday party dinsu ze kasance ita dai ihsan Inbanda murmushi da touching wayarta babu abunda take, ahaka suka karasa gida suna Shiga ihsan ce tafara fita kafin isy da ta tsaya tayiwa yan set dinsu voicenote a group cewar Monday akwai birthday party dinsu ita da ihsan. Ihun da akaringayi avoice din kowace da irin yanda take yin nata Ihun. Wata friends din su ce Hani Abdullahi tayi ihu cewar wayyo Allah ranar akwai chasu gamu ga world soldiers "gaskia Kar wada ta kallarmu YAYA AK"

tafada tana turo imoges na red face, don wallahi zan tsokane idon masu kallan mijin da ba nasu ba,

Hahahhahha wata kawar su hope Godwin tayo voice din ta itama. Wallahi  if his wife catch you she will remove your head from your body, hahahah. Takuma kwashewa da dariya, kowa voice yakeyi acikin kinsu Amma duk na  hope yafi batawa Hany rai,

"my friend go and hug transfomer Yaya AK nawane tafada tana turo Mata imoges din gwalo,wait and see me that day in my army arms, takuma turomata imoges din runguma,

Hahaha hope takuma dariya Okey. My friend I can't wait tafada itama tana turomata imoges na shut your self before that day. Haka suka ringa exchanges voice note duk Akan ranar birthday din su isy Har ihsan dabata yawan magana Sai da tayi munching Akan maganar Hani  Abbullahi Akan cewa tana Jin tausayinta ranar Don matar Yayansu one in town ce.

Gidan shuru kakeji tun bayyan tafiyar bakin da sukayi yaji fitowar yafendo Kuma be Kuma jinta ba Ahankali ya tashi saboda tafiyar sa haryanzu Bata yi kwari ba Dan ma kusan 1week saddam baya na basu fitar dare da suka sabayi ba,

"hello yah AK"

"Ahmad kabara yane 2days, banji feedback ba menene labari muzurun Nan" ya fada Yana me daidaita tsayuwarsa abangon dakin don yafiso yafara tsayaws da kansa babu temakon wani abu,

"wallahi lpy kalau hahhahha kasan muzuru yahada wani bala'in kuwa hummm wallahi ankama wata budurwa ta zubawa ME GANYE insecticide a juice! Yanxu haka Yana emergency Kuma kasan wani abu baze tashi ba,

Innalillahi wainna ILAIHI raju'un me MUZURU YAKESON zamane, ya fada Yana Bude kofar dakin Wanda ajikinta wardrobe take shine kadai yasan akwai kofa Sai saddam. Saboda tanan suke fita duk daran duniya, nikaina meAgogo sakin baki nayi ina mamakin Amma CONEL ya

shammace ni yaushe yafara tafiya!

Fitowar ta daga wanka kenan saboda duk jikinta yayi sanyi sakamakon ganin umminta datayi yau daure take da towel iyakacin sa daidai cinyar ta Rabin ciyarma duk awaje yake. Sure take gogawa a hammatar ta Sai taji kamar Ana knocking tsayawa tayi taji dagaske ne kokuwa kunnenta ne, wani knocking din takumaji gaban tane yafadi Don babu Wanda yatabayi mana knocking toh waye tafada azuciyarta uhm ina tunanin yafendo cema tafada tana daukan hijab. Kiiiiii taji anturo kofar tunkafin tagama saka hijab din.tacikin hijab din take kallonsa Wanda kofar da yarike ita taba shi ikon tsayawa da kyau kamar beta ba samun ciwon kafa ba!

😳

Muje zuwa guys third to d last page...

One love masoyana.

❤❤❤❤❤❤❤❤❤❤❤❤❤Inayinku sosai masoyan littafin CONEL AKRAM. ALLAH YABAR KAUNA.

😍FAUXIA MUHAMMAD BALA(Mrs SSG) 😍

Copied By
YAYA HAYAT
(admin

Hayat hausa novels Group
Hausa novels and fashion Group
Cool novel, makeup and kitchen1 Group
And
WOMEN24 TV Group

WHATSAPP NO:+2349030159301